[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page._ 4

Sosai Aysha tayi jinyar jikin ta batare da Gogal ta gane ba , shi kuwa Khalid tunda ya d'an d'ana Aysha kullum cikin yi mata magiya yake akan takuma bashi jikin ta , Aysha dataga abin nasa yayi yawa ta daina shiga sabgar sa kwata kwata , tun Gogal nayi mata fad'a akan shariyar data keyi wa Khalid har tagaji ta zuba mata idanu .......

Kusan wata d'aya kenan kwata kwata Aysha bata shiga sabgar Khalid , a lokacin kuma takejin wani canji atare da ita tamkar wata mara lafiya , Gogal ta matsa mata sai sunje asibiti amman firr Aysha tace taji sauk'i ba inda zataje , a cikin wata na biyu taga batayi period d'in ta ba aikuwa ta shirya ta nufi asibiti batare da Gogal tasani ba , gwajin farko likita ya sheda mata tana d'auke da ciki na kwana Hamsin , tuni zufa ta karyo wa Aysha tana zaune tuni ta mik'e batare da tasani ba , nan ta dubi dr. Tace " dan Allah likita ka fad'amin gaskiya wanne irin ciki gareni ? duban ta yayi sosai sannan yace " haba ke kuwa 'Yan mata akwai wani ciki daya wuce cikin haihiwa , In kina da miji kije kiyi masa albishir nan da wata takwas yana da Baby agidan sa , tuni Aysha ta goge zufar dake zuba ta jikin ta tace " nagode likita ta juya ta fice daga office d'in , wani asibitin ta nufa shima gwajin farko suka tabbatar mata tana d'auke da ciki , nan ma Aysha bata yadda ba ta nufi wani Asibitin , a haka haka dai sai dataje asibiti guda hudu kuma duk sun tabbatar mata tana da ciki , kuka sosai ta shiga yi a cikin asibitin k'arshe dan abun sosai yabata tsoro , haka ta wanke fuskar ta tayo hanyar gida tana tunanin yadda zata cewa Gogal , koda tazo gida tayi sa'a Gogal bata nan amman tabawa me shagon gidan nasu mukulli

ya ajiye wa Aysha d'in , tana bude gida tashiga tana shiga tafad'a toilet tana kuma wanke fuska sanna tafito ,  d'aki tashiga tasamu waje ta kwanta tana tunanin mafita yadda zata fuskan ci wannan al'amari , wata zuciyar tace " kawai kije kisamu Khalid kiyi masa bayani tunda har shine yayi miki wannan cikin , haka kuwa tabi shawarar zuciyar ta ta mik'e tafice daga cikin gidan.....

Koda Aysha taje gidan su Khalid neman sa tayi sa'ar samun sa , yana ganin ta yashiga murna yana ayyana ko ta sakko yanzu zata fara bashi had'in kai , dan gaskiya tayi masa zak'i sosai yadda yakeso ,  duban sa Aysha tayi sannan tace " inason Magana dakai , Khalid yace tazo su shiga cikin d'akin sa tunda daman babu kowa a gidan su , Aysha bataji komai ba ta bishi suka shiga , samun waje tayi ta tsaya tana duban sa ,  shikuma wata kwanciya yayi kan katifar d'akin sa yana fad'in " ya zaki tsaya daga nan yakama ta ki k'araso nan sai yafi , wani duba Aysha tayi masa wanda banda zallar tsanar sa yanzu babu abinda takeji ,  daurewa tayi sannan tace " ba zama nazo yi ba inaso in sheda maka yanzu haka ina d'auke da cikin ka , wata irin zabura Khalid yayi yana duban Aysha tare da tasowa ya k'araso gaban ta yana fad'in " sake mai mai tamin maganar da kikayi banji kiba , nan Aysha tasake gaya masa tana d'auke da cikin sa , wani murmushi Khalid yayi sannan yace " haba yarinya ki canza magana kawai daga zarar na kusan ceki sau d'aya kawai sai kiyi ciki ,  kuma naga bawani me yawa mukayi abun ba taya za'ace har kin samu ciki , wani takaici ne ya kama Aysha tace " amman ko yaya ne dai kayi ko kuma ko minty  d'aya ne ciki dai yashiga ,  Khalid ya had'e rai sannan yace " yakama ta ki kama kanki kije can ki nemi wanda yayi miki ciki ,  kuma dan na kusan ceki sau d'aya taya zakiyi ciki ? sai dai in wani kike bi yayi miki ciki ba niba , Aysha ta dubi Khalid tace " kaji tsoron Allah Khalid wallahi duk duniya babu wanda yasanni 'ya mace sai kai , kuma tun randa ka kusan ceni ban k'ara kusan tar wani ba , kai kan ka sheda ne akan tarbiya ta kuma kasan bana kula kowanne namiji sai kai ,  Khalid ya yamutsa fuska sannan yace " taya zan gane bakyayin tarayya da wasu mazan bayan ni ?  hawayen dake zubowa a idon ta Aysha ta goge sannan tace " Allah shine sheda ta wallahi ban tab'a tarayya da kowa ba sai kai ,  ta durk'usa a gabansa tana kuka tana fad'in " dan Allah katai maka min kasan yadda zamuyi da cikin nan plss banason Gogal tasani , Khalid yace " kine mi Uban cikin dake jikin ki wallahi bazan tab'a yadda nawa bane ya kewaye ta ya fice daga d'akin , kuka sosai Aysha ta shiga yi tana tsinewa Khalid , ashe dama ba soyayyar gaskiya yake mata ba ?  haka ta tattara tabar gidan tana kuka  tare da tsanar kanta baki d'aya ........

Haka Aysha ta kasance cikin tararrabi kar Gogal tagane , sai dai tabi ta rame ta lalace saboda tunanin yadda zatayi da cikin jikin ,  dabara ce tazo mata  akan taje chemist d'in wata baye rabiya datake a wajen makaran tar su ko tana da maganin zubar da ciki ,  dayake Gogal tana da sakaci akan kula da sabgar Aysha shiyasa kwata kwata bata fahimci cikin datake d'auke dashi ba ,  sai dai tana yi mata fad'a akan ramar datakeyi haka siddarar , sai Aysha tace zazzab'in dare take fama dashi .......

Ranar dataje chamist d'in ta sanar da matar, take tace tabata dubu goma zata zubar mata da cikin ,  Aysha tace " dan Allah kiyi min ragi wallahi bani da dubu goma , haka dai tasamu ta

rage mata dubu Uku zata kawo dubu bakwai kenan ,  haka Aysha tadawo gida tana tunanin ta yadda zata sanar da Gogal taba ta kud'i har dubu bakwai , dabara ce ta fad'o mata tace da Gogal tana so ta bata kud'i zata biya kud'in jarrabawar da zasuyi ta kammala secondry sch , Gogal tace tabari nan da kwana biyu in sunyi k'osai sai ta had'a mata kud'in  .........

*Kuyi Maneji*

*'Yar* *Mutan* *Kanawa* _Ce_ 🌹😍
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR  HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association*💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page._  3

Jabir yayi murmushi yace " inaso kisaki jikin ki dani , bawai na shiga rayuwar ki dan wani abu ba sai dan Soyayyar da nake miki ,  duk san da zan ganki cikin shigar kamala sai na kwad'ai tu da san ganin cikakken jikin ki ,  kullum in zaki zo giftawa ta gaban mu nida abokaina sai na dakata da duk kan abinda nake dan kawai na tsaya kallon ki , hakan tasa na shiga bibiyar ki har nagano ashe kema *'Yar Hannu*  ce , gumin dake zubowa a fuskar ta tasa hannu ta goge tana kallon Jabir wanda yaza mar mata tamkad majigi ,   Aysha ta dake tace " naji kuma na gode da bibiya ta dakake , amman kasani kar ka sake kazo min da maganar soyayya , dan babu ita kwata kwata a cikin lisaafin rayuwa ta ,  sannan in har kana buk'ata ta na yini d'aya to

ka tabbatar da kana da kud'in da zaka d'auke ni , kuma inaso kamar yadda ka bibiye ni kagane wace ce ni inaso kaja bakin ka kayi shuru , dan banaso ace mutane sun san wace ce ni , hakan zai janyo wa Kaka ta babbar matsala na barka lafiya , juyawa tayi da sauri dan bata buk'atar ya kuma tare ta da wani zance .....

Da ido Jabir ya bita tare da yin shu'umin murmushi yace " Tabbas Jabir bashi da kud'in da zaiyi mu'amala dake , sai dai Tabbas sai kin soni kuma soyayya ta gaske , juyawa yayi ya nufi majalisar su yana jinsa cikin farin ciki......

Tunda Aysha ta shiga cikin gida Gogal keyin fad'an kaiwa daren datayi , Aysha cike da ladabi tace " kiyi hak'uri wallahi ashe wani malamine daga cikin malamai yayi hatsari shine aka had'u akaje dubashi ,shiyasa kikaga nakai wannan daren , sosai Gogal ta jimanta tare da yin addu'ar samun lafiya ga malamin , d'aki Aysha ta shige tayi saurin cire kayan jikinta tare da saka wata doguwar rigar atamfa sannan ta fito , wanka tayi sannan ta d'auro arwala tazo tayi sallah , bayan ta idar Gogal ta d'auko mata tuwon shinkafar datayi musu da miyar kub'ewa ta ajiye , sosai Aysha ta shiga murna tare da cewa " wallahi kamar kinsan yau dama sha'awar cin tuwon nake , Gogal tace " ai gashinan sai kici ni dama nagaji da shinkafar nan shiyasa nayi tuwon , sosai suka shiga hira wacce rabi duk akan k'aryar da Ayshar takeyi wa Gogal d'in ne akan zuwan su dubiya......

Wajen k'arfe tara yaro ya shigo cikin gidan yace " wai ana sallama da Aysha , da sauri Gogal ta furta "kace tana zuwa gatana yanzu , Aysha ji tayi ranta yayi mugun b'aci dan duk duniya ta tsani azo ace ana kiran ta , Gogal ta dube ta tace " kinajin ana kiranki a waje naga ko alamar son fita ba kya yi , Aysha tace " haba Gogal ai kafin kice ina zuwa yaka mata kiji ko waye , Hararar ta Gogal tayi sannan tace " sannu uwa ta wato har sai na tsaya jiran jin ko waye kenan ? Sayyada inaso kisani nagaji da wannan halin naki na rashin son fita zan ce , wato kina cikin gida zaki samu muji ko ? maza kitashi kije kiga waye ai a haka zamu dace har kisamu na arzik'i , mik'ewa Aysha tayi tana turo baki sannan ta nufi d'akin ta , Hijab taje ta sako ta feso turare sannan ta fito tasa takalman ta tayi waje .....

Tana fitowa taga Jabir a tsaye sanye cikin k'ananun kaya , mamaki ne ya kama ta cikin zuciyar ta tana fad'in " wato wannan mutumin baiji abinda nace masa ba kenan , tabbas zata koya masa darasi sai yagane ita ba sa'ar sa bace , k'araso wa tayi batare da tayi sallama ba taja ta tsaya , duban ta Jabir yayi sannan yace " wa'alaikissalam tunda bakiyi sallamar ba , had'e rai tayi sannan tace " meye ya kuma dawo dakai waje na ? Jabir yace " Soyayya , Soyayyarki itace wacce ta saka bazan iya k'yale ki ba koda zaki dunga yankan naman jikina , duban sa tayi shek'e k'e tace " amman tunda gar kasan wace ce ni meye na Sona ? murmushi Jabir yayi sannan yace " shi So ba ruwan sa da wane ne wannan ko wancen , inhar yatashi kama mutum to baya duba matsayi ko kuma kyau ko nasaba ko asali , ba ruwana da ko wace ce ke tunda har na tabba tar da ba matar aure bace ke , Dan Allah Aysha kisoni koda nawani lokacin ne , zuciya ta takamu da sonki kuma banajin zata iya daina sonki mutuk'ar ina numfashi , Aysha ta kuma kallon sa a karo na biyu , cikin ranta take fad'in " tabbas baka da makusa ta ko'inah sai dai kwata kwata bazan yi soyayya ba saboda so ba gaskiya bane , a fili tace " babu wani gurbi da zaka samu a cikin zuciya ta , Bana soyayya kuma bazan kuma yin taba , dan

Allah inaso kafita a cikin rayuwa ta , Abu d'aya zaka nema nabaka shine Jikina , dan duk namiji in yazo gareni abinda yake nema kenan , tunda nake ba bu Namijin da yatab'a sona dan Allah sai dan jikina kodan Sha'awa ta , sanadin hakan yasa nafara wanan harkar daka ga inayi , inhar kaima dan jikina kake sona inaso ka tanadi kud'i da wajen da zamh had'u zanzo nabaka sai ka rabu dani , tana gama fad'ar hakan tajuya ta shige gida zuciyar ta nayi mata k'una......

Tuni jikin Jabir yayi sanyi da jin maganganun Aysha , tabbas shima yanaso ko sau d'aya ne ya sha zumar ta , amman tunda yaji kalaman ta yaji yadaina sha'awar ta sai tausayin ta zallah da ya cika masa k'irji , tabbas zai share mata hawayen ta zai tsaya tsayin daka ya nuna mata soyayyar sa ta gaskiya dan ya cire mata shakku akan sauran maza.......

Aysha na shiga cikin gida d'akin ta ta nufa ta fad'a kan katifa tana kuka , rayuwar datayi a baya itace tashiga dawo mata a zuciyad ta .......

*Tuna Baya*

Aysha tunda ta taso a hannun Gogal take , suna sana'ar sai da k'osai a k'ofar gida ita da Gogal , da wannan sana'ar tasu suke rik'e da kansu tare dayin sauran buk'atu , tana zuwa makaran tar Tahfez anayin kuma boko a makarantar , Aysha tana da k'ok'ari sosai shiyasa take da farin jini a gun malaman su tare da sauran d'alibai , lokacin tana da shekara goma sha biyar suka had'u da Khalid , Khalid yana son Aysha sosai dan lokacin ba wanda bai son Soyayyar su ba , Gogal tuni tayi masa Alk'awarin basa Aysha da zarar ta gama makaranta , tunda Aysha tafara zama budurwa komai na jikinta ya k'ara fitowa , kyau na usilin ba fullata na ya bayyana diri da k'ira tamkar itace ta zana kanta , wanna surar ta ta tafara janyo Alhazawan birni suna kawo mata hari , tun lokacin Khalid yashiga jin Sha'awar Aysha tamkar ana hura masa wuta , kwata kwata idanun sa suka rufe akan son sai ya kusan ce ta ko ta halin k'ak'a .....

Wata rana Gogal bata nan taje kasuwa tabar Aysha na shirin tafiya Makaranta , Aysha ta fito daga wanka kenan sai ga Khalid ya shigo cikin gidan nasu , lokacin d'aure take da d'aurin k'irji duk jikinta jik'e da ruwa , Khalid dama yana shigowa cikin gidan saboda shak'uwar dake tsakaninsu , gashi kuma shima d'an unguwa shiyasa gidan yazamo masa tamkar gidan su , ganin Aysha a wannan yanayin yasa gaba d'aya Khalid ya fita daga hayyacin sa , shigowa d'akin yayi yana nufo Ayshar yana fad'in " Mata ta ki taimaka min dan Allah ko sau d'ayane kibani jikin ki , matsawa Aysha tayi ana ja da baya jikin ta na rawa tamkar mazari , shima Khalid matsowa yake har sai da takai bango shikuma yayi mata rumfa , k'ank'ame jikin ta tayi duka tana fad'in " dan Allah Khalid kayi hak'uri karka keta min mutinci na , kajira duk lokacin dana zama matarka sai kayi yadda kakeso dani plss , kwata kwata Khalid ya fita a hayyacin sa dan ji yake mutuk'ar bai kusanci Aysha ba zai iya mutuwa , tuni yayi kanta yana janyo ta jikinsa duk wani k'ok'ari da zatayi dan ta k'waci kanta takasa yi , abunka da Namiji kuma wanda yake a halin Sha'awa komai na jikinsa yayi k'arfi , tuni ya kwance zanin dake jikin ta tuni Aysha ta rufe ido tana ambaton sunan Allah , gashi takasa ihu dan neman agaji ji tayi bakin ta tamkar ansa

mukulli an rufeshi ,  Shikuwa Khalid yana tozali da Na Shanun Aysha yafara murzasu tamkar yasamu fulawa ,  tuni ya kashe mata jiki har yasamu ya biya buk'atar sa , sosai Aysha tayi kuka da azabar da tasha a hannun Khalid ,  sai da yasamu kansa yaji wani irin kunya ta rufe sa , haka ya taimaka mata ya kaita band'aki ya gyara ta tare da bata hak'uri  , Aysha jitake tamkar ta rufesa da duka saboda haushi   , haka ya fice daga cikin gidan tansa fess tunda ya biya buk'atar sa , Aysha tuni zazzab'i ya rufeta makarantar daba taje ba kenan ta zauna jinyar jikin ta .......

Koda Gogal ta dawo gida bata gane me yafaru da Aysha ba , lokacin magriba tayi kuma Aysha tayi mata k'aryar ciwon ciki takeyi da zazzab'i shiyasa bataje Makaranta ba ........

*In naga Comment zanci gaba da Posting*

_Taku A ko Yaushe_

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Dasunan Allah me rahama me jin k'ai , tsira da Aminci su tabbata ga Shugaba jagaba Annabi Muhammad s.a.w 👏🏻👏🏻_

*Wannan littafin banyishi dan wata ko wani ba , nayishine dan nishad'i  duk wanda yayi

daidai da rayuwar sa to yazone a arashi ,*

_Allah kabani ikon rubuta Abinda zai amfani Al'umma_ 🙏🏼🙏🏼

*Mallakar : Fad'imatuz Zakiyya ( Zee MD )*

_Page._ 1

Sanye take da hijab har k'asa duk ilahirin jikinta baka gani , fuskar ta rufe da Nik'af tana tafiya a hankali tamkar wata wahainiya , tana zuwa wata majalisar maza zata wuce dukansu suka bita da kallo , ko gotawa batayi ba wani daga cikinsu yace " nidai wannan matar inason inga fuskar ta , sauran suka ce " to mezakayi da fuskar tata alhalin kana ganinta kaga matar aure me cikar kamala , wallahi Jabir ka rufawa kanka asiri kar kaje watara na mijinta yajika , wanda suka kira da Jabir yace " karfa kuga laifina duk abinda kagansa a killace to tabbas kasan yana da daraja , kuma kowaye zaiso ace ko sau d'aya yaga yadda abin yake , kuma da kuke maganar cewa matar aure ce wallahi nidai ban yadda ba , nan suka kafa musun wannan mata da ta wuce......

Tana k'arasowa titi ta tsayar da Napep koda ya tsaya ta k'arasa ce masa tayi " Green palace Hotel zaka kaini , kallonta yashiga yi sama da k'asa kafin yace " Bisimillah kud'inki d'ari biyu da hamsin , shigewa tayi batare da tace komai yaja suka tafi......

Tafiyar Minty 10 sukayi yakawosu Green palace hotel , suna zuwa ta zuge wata k'aramar jakar ta tabashi d'ari biyar ta juya ta shige ciki batare da ta anshi canji ba ......
Tana shiga ciki ta nufi Reception tana zuwa tace musu " ina da bak'o a room 13. nan suka duba tare da kira number d'akin data fad'a , sai da suka gama magana sanna suka bata umarnin tafiya.....

Hawa sama tayi ta nufi number 13 Room hankalinta kwance , tana zuwa tayi nocking k'ofar aka bata izinin shigowa , tana shiga tasamu Alhaji Nuhu Matawalle yana kishingid'e yana shan lemo , yana ganinta yafara mata kirari " Sayyada kike a cikin gidanku a titi kuma *'Yar Hannu* ce ke , Kankana uwar ruwa sikari baki farin banza ba zuma kike ga zak'i ga harbi , cire Nik'af d'in tayi sannan ta cire Hijab d'in shima , tana cirewa naga ainahin halittar ta , Kyakkyawa ce ajin farko ga kyau ga dirin jiki ko inah acike yake na jikinta , gata doguwa tamkar itace ta zana kanta , k'ugunta kuwa tamkar andasa mata shi haka k'irjinta a cike yake kuma gasu a tsaye k'yam , wani shu'umin murmushi tayi ganin yadda Alhaji Nuhu yasaki baki yana kallonta har wani miyau yake had'iaya muk'ut , riga da siket ne ajikinta na atamfa sosai suka kamata kai bakace zasu fita ajikinta ba , zama tayi kusa dashi numfashin su na bugun juna tuni Alhaji Nuhu ya rud'e yana neman fita hayyacinsa , matsowa tayi sosai ta shafo fuskar sa sannan ta sumbace sa , ai suman zaune yayi tare da wani lumshe ido yana sambatu , cike da kissa tace "

Alhaji gani nazo na cika Alk'awari dan haka nima inaso ka cikamin nawa Alk'awarin , da sauri yace " *Aysha* kifad'i duk abinda kikeso mutuk'ar inadashi to zan mallaka miki , wani wal tayi da ido tare da hura masa wata iska har sai daya lumshe idonsa tace " inaso ka siyamin Motar dan nagaji da yawo a k'asa , amman nafiso kabani kud'in insiya da kaina bawai kasiyamin ba , Alhaji Nuhu yayi wani murmushi yace " Motar kacal kikeso Babyna ? kai ta d'aga masa alamar Ae batare da tayi magana ba , Alhaji yace kituromin Account Number ki yanzu zan miki transfer ta 3 Milloiner sai ki siyi wacce kikeso , da sauri Aysha tace " wow Alhajina nagode da wannan gift d'in naka , Murmushi Alhaji Nuhu yayi sannan yace " akan ki babu abinda bazan iya yi ba dan ked'in ta musamman ce , tuni Aysha tafara rikitashi da salonta , Alhaji Nuhu tuni ya fice daga hayyacinsa sai wani surutai yakeyi , a haka har suka fara aikata ta'asar su .......

Bayan wasu a wanni kowannen su ya gama gamsuwa Aysha ta mik'e tashiga toilet , saida tayi wanka ta kintsa jikinta sannan ta fito , kayanta ta d'auka tasaka sannan ta dubi Alhaji Nuhu , shima ita yake kallo tayi wani murmushi tare da kashe masa ido tace " ni zanzo natafi gida kasan bana so ace nakai yamma banshiga gida b , Alhaji Nuhu take yayiwa Aysha transfer ta kud'in dayayi mata alk'awarin bata , sannan tayi masa sallama akan gobe zata dawo masa .......

Tana fitowa tasamu me Napep tahaye abinta ta nufi gida....

Koda tadawo har lokacin wannan majalissa tasu Jabir tana nan , haka tazo takuma wuce su har ta k'ule suna kallonata , tana k'arasowa k'ofar gidan tashiga da sallamar ta , wata dattijuwa ce a zaune tana lazimi itace ta amsa mata sallamar tare da cewa " sannu da zuwa Sayyada Yaya Makaran tar taku take ? Aysha tace " Alhamdulillah Gogal .....

dan son jin labarin *'Yar hannu* Kuci gaba da bibiyar
*'Yar* *Mutan* *Kanawa*🌹😍😍
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Muna mik'a ta'aziya a  gareki Maman mimi ,na rashin Mahaifi da kikayi  Allah yajik'ansa yayi masa Rahama ,🙏🏼🙏🏼_

_Page._     7

Haka Aysha tashiga jinyar jikinta har tasamu lafiya batare da Gogal ta gane ba , tanajin sauk'i tafara shirya yadda zata fara d'aukar fansa akan Khalid da Farouq da kuma sauran abokansu , tare da duk wani namiji mazinaci me lalata tarbiyar yaran mutane , wajen Madam taje me chamist ta aunata dan tabbatar da ciki bai shiga jikinta ba , sannan tasiyi maganin hana d'aukar ciki , a dai dai lokacin ta kammala secondry sch tare dayin saukar alkur'ani me girma ......

Lokacin suka d'auketa koyarwa ita ma kuma ana koyar da ita sauran littattafai ,  Hameed tunda yaga Aysha zuciyar sa takamu da sonta sosai tare da tausayin ta , sai dai yayi zuwa yafi biyar gidan su amman bata fitowa , tun Gogal na zuba mata ido har tafara fad'a akan rashin fitar da batayi ,  Aysha ta karkace tace da Gogal " amman Gogal kinsan dai Farouq nake so kinga bai kamata na batawa wani lokaci ba , Gogal tace " yaushe rabon da Farouq d'in yazo ? innayi magana kice baya k'asar yayi tafiya ,  Aysha tasamu ta lallab'a Gogal akan tabarta ita dai bazata fita ba ,  kwata kwata Aysha bataso ko kad'an Namiji yace yana sonta , dan ansha ta an warke yakamata tayi hankali zuwa yanzu , tunda ta fuskanci ba ita suke so ba kawai jikinta suke so , dan haka taci Alwashin zata zame musu abar tsoro ko da sunan ta sukaji , tabbas zatayi bariki amman me lasisi wacce sai ta tara dukkan abin duniyar da takeso ,   nan ta yanke shawarar duk sanda wani yakuma biyota zata tsaya kodan tasamu kud'in siyan waya ,   aikuwa ranar tana fita makaranta sukayi karo da wani Alhaji  a wata jibgegiyar mota , aikuwa yana tsayar da ita bata wani ja aji ba ta tsaya abinta ,  motar yace tashigo yarage mata hanya  , aikuwa Aysha bata wani ja ba ta amince masa tashiga suka tafi , suna hanya ya dubeta yace " gaskiya 'Yan mata kin had'u sosai kuma kina da kyau , murmushi Aysha tayi batare da tace dashi uffan ba , hannun sa ya d'auka ya d'ora mata aka cinyar ta yana murzawa tare dawani kashe ido ,  wani takaici ne yakama Aysha cikin ranta take fad'in " daman nasan badan Allah ka d'auko niba dole buk'atar kan kace ta tsayar dakai , katse mata tunanin yayi dacewa " ko zaki rakani Hotel mud'an rage wasu awannin ?  Aysha tayi wani murmushi tare da kashe masa ido sannan tace " zaka iya biyan farashina ?  shima murmushin yayi sannan yace " ko nawa kikeso nikuma zan ninka miki mutuk'ar zaki bani yadda nakeso ,  Aysha ta karkace tace inaso kasiyamin waya Iphone 11pro max sanna  kamin shopping d'in kayayyaki , duban ta yayi yana dariya sannan yace " wannan ai abu masu sauk'ine muje yanzu mufara siyansu kafin ma muje Hotel d'in ,  duk abinda Aysha ta lissafa sai da yasiya mata shi har da wad'an da bata fad'a ba , daganan suka wuce Hotel abinsu  yakama d'aki , sosai ya jigata Aysha dan k'ofar gabanta har yanzu bata gama bud'ewa sosai ba , gata da tarin Ni'ima dan har ihu Alhajin yadunga yi , bayan

sunga ma tayi wanka tare da saka kayan ta , duban ta yayi sannan yace " da zaki kwana d'aya dani dana k'aramiki kud'i fiye da wanda nakashe miki shi , Aysha tayi murmushi sannan tace " next time zamu sake had'uwa amman bazan iya kwana a Hotel ba , haka ta tattaro kayan ta tayi masa sallama tayo gida....

Tunda ta sauka a Napep Taga wata motar me bak'in glass nabinta , sai da ta kusa shiga gida sannan yayi mata hon. da kamar zata wuce sai wata zuciyar tace " kitsaya ki ga kowaye ko zaki samu wani kud'in , Hameed ne ya fito sanye da k'ananun kaya da suka amshi jikinsa , ba k'aramin kyau yayi ba sai k'amshi yake tamkar wani sabon Ango , yana zuwa yayi mata sallama tare da cewa " barka da dawo , Aysha ta tab'e baki sannan tace " barka kadai , ina fatan dai lafiya ka tsayar dani ko ? Hameed jiyayi tayi bala'in burgesa yadda take basarwa da kuma yadda take maganar ta , cike da so da k'auna tare da zallar kulawa yace" nazo yafi a k'irga dan naga lafiyar ki amman bakya fitowa , ina fatan dai yanzu kinji sauk'i sosai dan kin barni da zulumi , murmushi tayi sannan tace " naji sauk'i sosai kuma nagode da kulawa sai anjima ina da abunyi , bata jira amsar saba tayi cikin gida abinta batare da ko waiwaye tasake yi ba ......

Hameed binta yayi da kalli yana yaba kyan halittar ta , tabbas ta had'u sosai komai da yakeso matar auren sa takance to tana dashi , dan haka zai ci gaba da bibiyar ta ko Allah zai sa yadace ......

Aysha na shiga cikin gida tayi sa'a Gogal na cikin band'aki , tuni ta shige cikin d'akin ta da kayan tana b'oyesu dan kar Gogal tagani , wayar ta d'auko dan tanaso tasa ta a caji dan ta saita whaspp da sauran Abubuwan social media , dan acikine zata samu manyan Alhazawa wanda zasu jik'ata da kud'i har tazama wata itama sannan ta rama abinda su Farouq sukayi mata shida Khalid.......

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_😍🌹
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page._ 2

Arwala Aysha tayi tazo ta zauna tafara lazimin itama , bayan anyi sallar magriba ta mik'e tashiga kitchen ta d'ora musu Abinci , tana kammalawa ta zubo musu tashigo cikin d'akin suka zauna tare suna cin Abincin , Gogal ta dubi Aysha tace " Sayyada inaso naga aurenki kafin Allah ya amshi raina , koda yaushe burina ace nabarki a hannun wanda zai zamo garkuwa a gareki , ked'in marainiya ce gaba da baya kinrasa Mahaifiyarki a lokacin da kikazo duniya , shikuma mahaifinki yarasu a lokacin da aka kawo mana hari cikin Rigar mu , a lokacin kina da shekara shida a duniya haka muka samu muka tsira nida ke batare da ankashe mu ba , nice wacce na haifi Mahaifinki kuma dama shikad'ai na haifa a duniya nima , tunda kika taso kike da farin jinin mutane saboda kyawunki , a lokacin rayuwarki tashiga hatsaruruka da dama a gun maza amman Allah yana kareki , dan haka inaso ace na aurar dake kafin nabar duniya , banaso intafi inbarki ke kad'ai batare da kinsamu abokin rayuwa ba .......

Hawayene ke zuba a idon Aysha tasa hannu ta goge sannan ta dubi Gogal tace " Insha Allah bazaki mutu yanzu ba har saikin aurar dani , nima banaso na rasaki Gogal dan bani da gatan daya fiki , Gogal tayi murmushi irin nasu na Manya tace " wai ina wannan Yaron Hameed wanda yake biyoki inkin dawo daga makaranta ? Aysha jitayi wani abu ya tokare mata zuciya , tabbas da Gogal tasan waye Hameed da bazata yi mata maganar saba , amman saita saita kanta tace " yayi tafiya ne shiyasa , Gogal tace " inhar da gaske yana sonki me zaihana inyadawo ya turo iyayensa sai kawai ayi magana , Aysha tace " dan Allah Gogal kidaina damuwa da batun auren nan , komai lokacine inhar Allah yayi inada rabon aure a duniya zanyi , karki manta shima idan ya turo iyayen nasa Abinda yafaru abaya shine zai kuma faruwa a yanzu , inhar za'azo neman aurena dole za'ace ana buk'atar Namiji , mu kuma bamu da kowa sai mu biyun nan muke da kanmu , akan hakan wasu na tsoron had'a iri damu wasu nayimin kallon shegia ce ni bani da iyaye , kinga kuwa samun miji wanda iyayensa zasu ya aureni sai antona , kiyi hak'uri kicire damuwar dake ranki Allah yana tare damu kuma wata rana zai kawo mana mafita , Gogal taji dad'in yadda Aysha ke d'aukar k'addara shiyasa itama ta goya mata baya tare da yimata addu'ar samun mafita.......

Washe gari Tunda Aysha ta tashi take tunanin yadda za'ayi ta fita , dan yau tana da wani bak'o wanda zaizo daga k'asar Ghana , sun had'une a Social media dan dama duk wasu Alhajojin da take mu'amala dasu a can take had'uwa dasu , duk wata kafar sadarwa ta Social Media ba wacce Aysha bata hawa , wayar dake hannunta Iphone 13 pro max ce , amman a cikin gida bata tab'a fitowa da ita ba bare Gogal tagani , kullum rik'e take da keypat d'in ta ,

cikin d'akinta anan take saka cajin ta tunda koda yaushe suna da wuta , sai dare ya tsala sannan take hawa Online tafara chat da Mutanenta , duk irin wannan d'abi'a ta Aysha baisa ta yi sakaci da ibada ba , tana azumin litinin da Alhamis ga Yawan yin Nafila tare da Azkar ......

Tuni Alhaji Ubale Ghana ya shedawa Aysha ya sauka yana Tahir Gate palace , tuni Aysha dabara ta fad'o mata tacewa Gogal Shugaban Makarantar datake koyarwa yace taje suna da taron malamai , aikuwa Gogal batare da ja ba ta amince dan ta yadda da Aysha d'ari bisa d'ari , dan duk kud'in da Aysha ke samu a wajen maza tanayiwa Gogal k'aryar Albashin tane na Makaranta da ake bata shiyasa bata ganewa , kowacce hidima ta gidan nasu itace take d'aukar nauyin ta , Gogal duk tunanin ta Albashin datake samune take musu wannan hidimar dashi , Asalima Makarantar ba zuwa takeyi ba sai taga dama , sannan ba'a biyansu ko ficika kawai suna kyarwa ne saboda Allah .......

Aysha tayi wanka ta shirya cikin wasu riga da siket na material , sosai d'inki ya kamata tamkar zatayi motsi kad'an su yage , ta d'auki Hijab d'inta kalar kayanta tasa tare da d'aukar Nik'af tasa ta d'auki jakar ta wacce tasa wayoyinta tare da kud'in Napep ta fito , sallama tayiwa Gogal ta kama hanya ta fice daga cikin gidan....

Yauma kamar kullum tana zuwa wucewa ta Majalissar su Jabir , a lokacin daga Jabir sai wani Abokinsa a zaune , yana ganinta yafara kallonta harta gifta ta gabansu , koda ta wuce Jabir ya dubi Abokinsa yace " wallahi mutumina ina son ganin wannan matar ko sau d'aya ne , koda yaushe zuciya ta tana kwad'aituwa da son ganin fuskar ta tare da cikakkiyar Halittar ta , Abokin nasa ya dubesa yace " haba Abokina taya kana ganin mace da irin wannan shigar ta kamala zaka ce kanaso kaga fuskarta , inkuma ta kasance matar aure to meye ribar ka na ganin fuskar ta ta ? Murmushi Jabir yayi sannan yace " bazaka gane ba Abokina nifah a jikina inajin wannan ba matar aure ce ba , kuma dole saina bibiyeta nagano ko wacece ita , Abokin nasa yace "aikuwa ka had'a kanka da aiki Allah yataimaka , Jabir yace Ameen tare da mik'ewa yabi hanyar da Aysha tabi........

Aysha na fitowa titi ta tsayar da Napep ta hau tare da gaya masa inda zai kaita , bayan ta sauka ta bashi kud'insa tare da shigewa cikin Hotel d'in....

Dama tuni Alhaji Ubale ya gaya mata Room number d'in d'akin , tana zuwa tashige batare da fargabar komai ba , tana shiga tasamesa daga shi sai boxer da singlet yana kwance yayi d'ai d'ai dashi , yana ganin ta a haka ya tashi yana fad'in " yakuma naga haka Babyn Dad'i ? kinyo shiga tamkar zakije gidan mutuwa , cire hijab d'in tayi tare da Nik'af take surar ta ta bayyana , tuni Alhaji Ubale ya zabga wani ihun murna tare da cewa " wow Babyn dad'i wallahi kin had'u sosai , ashe haka kike da kyau kika sa banzo gareki da wuri ba ? yau zansha wadak'ata da wannan lafiyayyen jikin , Wani fari da ido Aysha tayi tana dubansa sannan tayi k'asa da murya tace " zakaji dad'i mutuk'ar nima zaka jiyar dani , mik'a masa hannunta tayi tana fad'in ciniki yafara fad'awa sai kaji dad'in , Alhaji Ubale yayi murmushi yace " me kikeci na k'asa na zuba Babyn dad'i ? ai kome kikeso zanbaki shi basai mun tsaya wani ciniki ba , kinsan Allah bantab'a ganin mace me irin wannan surar taki ba , nayi aure aure na mata dayawa amman bantab'a karo da me irin wannan zubin halittar taki ba , mezai hana bazan miki b'arin nera ba kuwa ,

kawai kizo muji dad'in mu Babyn Dad'i  Zuma kike ga zak'i ga harbi ,  wani murmushi Aysha tayi tare da hayewa ruwan cikin Alhaji Ubale tafara susuta shi ,  ihu yake tamkar wani k'aramin yaro ga sambatu dayake mata tamkar wanda yau yafara sanin mace ,  saida tabari ta birkitashi sannan suka afka ta'asar su ......

Sosai Alhaji Ubale ya rik'e mata wuta , duk irin Jarumtar Aysha sai da tasha jiki a hannun Alhaji Ubale , dan shi mutum ne me k'arfin sha'awa sosai da sosai , gashi kwata kwata baya gajiya tamkar wanda  yasha zak'ami ,  Bayan ta gasa jikinta ta fito ta saka kayan ta har lokacin Alhaji Ubale a jarabar sa yake , gashi yace shi soyake ta kwana a gurinsa ,  Aysha duk iskancin ta bata tab'a kwana a hotel ba ko kuma gidan Namiji , ta yadda tazo ku yini tare zungur amman bata son kwana sabo da Gogal ,  Aysha tasaka Hijab d'inta tare da Nik'af tadubi Alhaji Ubale tace " zan wuce gida kaga Magriba tayi kuma bantab'a kaiwa haka a waje ba ,  Alhaji Ubale yace " haba Babyn dad'i saikace wata k'aramar yarinya da zaki dunga tsoron gida , kawai ki saki jiki mu kwana tare injik'aki da nera ,  murmushi tayi sannan tace " bazaka gane ba ne shiyasa banason ko kad'an in b'ata ran kaka ta , dan itace wacce tayimin gata  har nazama hakan kuke tarayya dani ,  dan haka idai tafiya zanyi kawai ka sallameni ,  Alhaji Ubale yace turomin Account number saina tura miki kud'in aciki,   take Aysha tatura masa account d'inta , dubu d'ari biyar ya tura mata ta mik'e ta fice batare da ta waiwaye saba .......

Sauri takeyi tunda ta sauka daga Napep dan lokacin har anfara kiran isha'i ,  gani tayi ansha gabanta ana k'ok'arin d'age mata Nik'af , da sauri taja baya tana fad'in " bawan Allah lafiya zaka tare ni ?  Jabir ya matso daf da ita yace " inason ganin fuskar ki ko sau d'ayane a rayuwata ,  Aysha tace " a dalilin me yasa zaka ga fuska ta inkuma ina da aure fa  ?  murmushi Jabir yayi sannan yace " nasan ked'in ba matar aure bace , haka zalika nasan wacece ke dan haka ki nunamin fuskar ki ,  Aysha tace " wacece ni to kuma meyasa zaka sakamin ido  ko natare maka wani Abun ne ? inaso kabani Hanya zan wuce ina da Abubuwan yi , ta zagayesa zata wuce  da sauri yace " Nasan bakisan waye ni ba  to nasan wacece ke , kece aka kira da *Aysha Babyn Dad'i  Zuma kike ga Zak'i ga Harbi ,* wasu kuma da dama suna kiranki da *'Yar Hannu*  , take Aysha ta tsaya tsaf wata zufa na karyo mata ajiki , tabbas ko waye wannan yagama saninta , dan wad'an nan sunan sune wanda ake kiranta dashi a Social Media ,  Abinda yabata tsoro taya wannan mutumin yasanta harya bibiyeta haka ? kuma gashi Uwa Uba acikin Unguwar su yake , wato kome takeyi akwai masu bibiyar ta kenan ? tabbas saita san waye shi kuma taya yake bibiyarta haka.........

*Banga Comment ba*   🤒

*'Yar* *Mutan* *Kanawa* _Ce_😍🌹

[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*

🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page._ 6

Sai Bayan wani lokaci sannan Aysha tafara motsa jikinta a hankali , da k'yar ta iya sakko wa daga kan katifar datake , a hankali ta mik'e tamkar ana yanka mata jikinta haka takeji , d'aukar kayan ta tayi tasaka a jikinta sannan ta tako a hankali ta fito , lokacin data fito bata sami kowa a cikin wajen ba haka ta fice zuciyar ta nayi mata k'una.......

Tana tafe a hankali tana bin hanya tamkar wacce akayi wa shayi , haka ta k'araso bakin titi ko gaban ta bata gani , jitayi wata mota tayi ciki da ita tun daga nan bata sake sanin inda take ba ....

Acan gida kuwa Gogal hankalinta ba k'aramin tashi yayi ba na rashin dawowar Aysha , tasan halin Aysha duk inda taje bata gota Magriba take shigowa amman gashi yanzu har Isha'i ta wuce , tuni zuciyar ta tafara tuhumar ta akan barin Aysha su tafi tare da Farouq d'in batare da ta bisu ba , a hankali Gogal ta furta " tabbas nayi wauta dana barki kikabi wanda ko asalinsa bamu sani ba , Allah yatsareki a duk inda kike Aysha , Allah yasa ba macuci bane ko kuma matsafi.......

Da gudu Hameed ya fito daga cikin motar sa yana salati , mutane suka yi ca ana fad'in " Innalillahi Allah yasa bata mutu ba , tuni Hameed yace " dan Allah kusamin ita a motar inkai ta Asibiti , haka aka saka Aysha a motar suka nufi Asibiti da ita.....

Suna zuwa aka bata taimakon gaggawa saboda buguwar da kanta yayi , jini sai zuba yake da k'yar suka mata allura ya tsaya , ruwa suka sa mata tare dayi mata allurori , Hameed

dayake likita ne shima yana tsaye har suka gama yi mata komai , duban sa Dr. Maheer yayi yace " Dr. Hameed Baffa yaushe kadawo k'asar tamu bamu da labari ? Hameed yayi murmushi yace " wallahi yau kwana na biyu da zuwa wani program , ashe tsautsayin indawo ne in kad'e wannan baiwar Allah , Dr. Maheer yace " Allah yayi sai hakan tafaru shiyasa kadawo , amman ai babu matsala tunda har ciwon bamai girma bane ,  Hameed ya dubi gadon da Aysha take kwance sannan yadubi Dr.Maheer yace " ina ganin kamar akwai wani Abun dayake damun ta bayan wannan buguwar kan ,  inaso kabani waje dan Allah zan duba ta , Dr.Maheer yace " ok badamuwa bari naje office duk abinda kake buk'ata kamin magana ,  Dr. Maheer ya fice daga cikin office d'in...

Yana fita Hameed ya k'arasa kusa da Aysha yashiga duba ta , ganin wani farin zuwa ya bushe gefen k'afar ta yasa yashiga duba jikinta ,  yana bud'e zanin ta yaga irin ta'asar da akayi mata ,  da sauri ya rufe jikin nata yana salati tare da fad'in " su waye suka mata wannan aiki ? nan ya fita daga cikin d'akin da saurin sa , ba'a fi minty 5 sai gashi da kayan aiki ya dawo , yana zuwa yashiga yi mata wasu Allurai tare da goge mata jikinta sannan yayi mata wata allura a gaban ta .......

Sai Bayan awa d'aya sannan Aysha ta farka daga bacci , tana tashi taji duk jikinta yadaina mata ciwon dayakeyi , kanta ne kawai yake mata ciwo shima kuma kad'an kad'an yakeyi , hannu tasa tana tab'a kan nata jitayi ansaka bata bandeji , sai a lokacin ta tuno da Abinda yafaru da ita tunda ga kan abinda su Farouq sukayi mata har izuwa lokacin da aka kad'eta da motar ,  da sauri ta tuno da Gogal dan tasan yanzu tana can hankalin ta atashe mik'ewa tayi da sauri tana dirowa daga kan gadon ,  Hameed tunda ta tashi yake kallon ta batare da yayi magana ba har saida yaga ta diro daga kan gadon , cikin sauri yace " baiwar Allah ina zuwa haka wannan dirowar da kikayi ? da sauri Aysha ta dubi gefensa sukayi ido biyu dashi ta tsaya tana kallon sa , shima ita yake kallo har tsawon wasu minty na kafin tace " dan Allah ka k'yaleni intafi gida nasan Gogal nacan na nema na , Hameed yashiga lallab'ata akan tayi hak'uri zuwa anjima , Aysha kwata kwata tak'i yadda saboda hankalin ta a tashe yake sosai ,  duk wani Namiji yanzu bata son k'ara mu'amala dashi koda ta magana ce  , tuni Hameed yaje ya anso sallama suka fito daga Asibitin ,  koda suka fito yayi yayi da Aysha ta hau motar sa amman firr tak'i hawa , haka ya hak'ura ya k'yaleta ta fito tahau Napep ta fad'i inda zai kaita ......

Hameed a baya yake binsu batare da Aysha tagane ba , ana kawota har k'ofar gida ta shige da gudu batare da ta tsaya ta bashi kud'i ba , me Napep tuni yafito da niyar bin Aysha cikin gida Hameed yayi saurin tarar sa , nan ya yabashi kud'in motar sa ya shige yatafi...

Hameed duba agogo yayi yaga k'arfe goma ta gota sai sannan ya tuno da abinda ya fito yi , da sauri ya nufi mota ya d'auko magun gunan Aysha yadawo k'ofar gidan yatsaya zai k'wan k'wasa , me shagon gidan sune ya fito da buta a hannu , koda Hameed ya gansa sai yayi masa sallama sukayi musabiha sannan yabashi maganin yace " dan Allah kamik'awa wata budurwa a cikin gidan nan , yana bashi ya shige ya nufi motar sa yashiga tare da jan ta yana barin unguwar......

Koda Aysha ta shiga gida samun Gogal tayi sanye da Hijab sai kai kawo take , tana ganin Aysha ta taho da sauri tana rik'e ta tare da fad'in " Alhmd Ina kika shiga haka Sayyada ? duk hankalina ya tashi sosai narasa ina zan nufa , Aysha kasa magana tayi sai kuka data shiga yi a jikin Gogal , nan danan Hankalin Gogal yatashi tashiga tsoro da farga ba tana fad'in " kigayamun meya sameki ina Farouq d'in ? ganin yadda Gogal ta furgice yasa Aysha ta sassauta kukanta tace " hatsari mukai Gogal nida Farouq , Sai sannan Gogal taga bandejin dake kan Aysha , salati tashi ga yi tana fad'in " shi yanzu ina Farouq d'in yake ko shi ya mutu ne ? sallamar me shagon gidan su itace ta katse Gogal suka kalli k'ofar shigowa , gaisawa yayi da Gogal sannan yabasu ledar magani yace " gashi inji wani a waje yace abawa Aysha , Gogal ta ansa yayi musu sai da safe ya juya ya fita.....

'Daki suka shiga baki d'ayan su Gogal nasan jin halin da Farouq d'in yake , ita kuwa Aysha ko maganar Farouq bataso ayi mata dan duk duniya bawan da ta tsana sama dashi , dan ko Khalid bataji tsanar sa irin hakan ba , Gogal tace " Sayyada inaso sanin yadda jikin Farouq d'in yake , Aysha ta lumshe ido saboda takaicin jin sunan Farouq tashiga girbowa Gogal k'arya " yana can Asibiti shima baiju ciwo sosai ba , dan nafishi jin ciwo sosai Gogal kuma tunda akamin allura naji sauk'i , yanzu bari nayi wanka nayi sallah na kwanta dan Dr. Yace in samu hutu saboda ciwon dayake kaina , da sauru Gogal ta mik'e tana fad'in " bari na had'a miki ruwan zafi sai kifi jin dad'in jikin naki , Allah ya kiyaye gaba mungode Allah ma dayasa ba'aji Babban ciwo ba ......

Koda Ayaha ta shiga wanka sai data gasa gaban ta sosai , tanayi tana hawaye tare da jin tsanar duk wani namiji a duniya , tabbas tasha jin yadda k'awayen ta ke bada labarin akan Macen data kai budurcinta gidan miji , Budurcin mace shine k'imar ta darajar ta da kuma mutuncin ta a idon mijin nata , yau gashi ita tuni angama bud'e mata shi a titi , yau wai itace maza hud'u sukayi amfani da ita , Khalid shine na biyar d'insu wanda kuma shine wanda yafara bud'eta , yanzu meye amfanin aure a gurin ta ma ? meye amfanin tayi aure mijinta yaji ta ba cikakkiya ba , tabbas sunriga sun b'ata mata rayuwa sun cuceta cuta me muni , dan haka saita zama *'Yar* *Hannu* yadda zata zamewa duk wani Namiji Mazinaci masifa arayuwar sa , sai ta d'au fansa akan su Khalid da Farouq da sauran Abokansa , wani murmushi tayi me ciwo tare da goge k'wallar idanunta tace " *Yan zu zamu fara wasan*, *Mazinatan maza ku shirya tarar Aysha 'Yar Hannu* sai na zamar muku masifa yadda bazaku k'ara sha'awar aikata zina da Yaran mutane ba.........

*Nadawo daga yajin aikin Rashin yin Comment*, _amman zan maida Book d'ina na kud'i tunda bazakuyi Ciment ba_ 🤒🤒🤒👊🏻👊🏻

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page._ 5

Kwana biyu dayin maganar Gogal tabawa Aysha dubu Biyar , Aysha ta karb'a ta had'a da wata dubu d'aya datake da ita ta shirya ta fice , koda taje tasamu wannan Bayerabiyar ta bata dubu shida farko sai tak'i ansa tace dubu bakwai ai sukayi da ita , Aysha tace " kiyi hak'uri Madam inna samu kud'i zanzo na cika miki , Madam da k'yar ta yadda amman tace nan da kwana biyu zata kawo mata kud'in , haka suka shiga wani d'aki tayi mata wasu allurai tare da bata wata k'waya tasha , Madam tace " ki zauna a cikin wajen dan gudun kar mutane su ganki , haka Aysha ta zauna ta takure tana ta istigifari da kuma hawayen takaici , can kamar an mintsine ta taji marar ta ta d'aure tare da jin wani ciwo na lokaci guda , tuni zufa tafara zubowa ajikin Aysha tafara fad'in "wayyo Allah na shiga uku wayyo zan mutu , tuni madam ta shigo tana rik'e ta tana mata sannu , jinine ya fara zuba guda guda tamkar an hankad'oshi , sosai Aysha tsoro ya kamata tare da sadak'ar wa ta ta ta k'are , tafi minty talatin tana abu d'aya kafin Allah ya taimaka jinin yafa raguwa , sai da tayi awa biyu sannan tasamu jinin ya tsaya sai kad'an kad'an yake zuba , Madam ta had'a mata ruwan zafi tace tashiga gidan ta tayi wanka sai ta kintsa jikin ta sannan tazo zata bata magunguna , aikuwa Aysha tayi wanka ta fito ta nufi wajen Madam ta sheda mata ta kammala wankan , Always ta bata tace tashiga ciki tasaka sannan tazo ta anshi magani , Aysha tana fitowa Madam ta bata magani tare da ce mata " Yarinya in kinason maganin hana d'aukar ciki ina sai dashi , karki k'ara yadda wani namijin ya kusan ceki batare da kinsha magani ba , inba haka ba zaki ta samun ciki kina zubarwa daga k'arshe ki lalata mahaifarki , Aysha ta kasa magana saboda haushin maganar da Madam tayi mata , wato

har fata  take mata na sake yin iskanci har tayi ciki ,   ko magana Aysha batayi ba tafice daga chemist d'in .......

Koda Aysha tadawo gida Gogal ta tambayi me yadawo da ita da wuri haka daga makaranta ? sai tace " batajin dad'ine shiyasa tadawo gida , nan tashiga d'aki ta kwanta abinta......

Bayan kwana biyu tuni Aysha ta ware tamkar ba ita ba , ta koma zuwa makaran ta ka'in da na'in , dama gata da k'ok'ari  kowanne karatu akayi mata sai ta ganeshi ,  Khalid tuni ya d'auke k'afa yadaina zuwa wajen Aysha ,   Gogal ta shirya da kanta taje tasame shi akan ya turo iyayen sa ayi maganar auren su da Aysha , bud'ar bakin sa sai cewa yayi wai " shi gaskiya a yanzu bazai iya aure ba , kuma koda zai yi aure gaskiya bazai auri Aysha ba tunda ba'asan asalin su ba , sosai maganar ta b'atawa Gogal rai  tayi masa sallama batare da ta kuma cewa dashi komai ba , koda Gogal ta dawo gida kwata kwata bata yiwa Aysha maganar yadda sukayi da Khalid ba , haka ta wuni ranta a b'ace kwata kwata ko abinci kasa ci tayi , tambayar duniya ba wacce Aysha batayi mata ba amman tak'i gaya mata har tagaji ta k'yaleta ........

Wata ranar Asabar Aysha ta dawo daga makaranta sukayi karo da Khalid ,  yana ganin ta ya nufota yana murmushi saboda wani kyau na musamman daya ga tayi masa ,  Aysha d'auke kanta tayi tamkar bata gansa ba dan ita a yanzu ba wanda ta tsana sama da Khalid ,   shan gabanta yayi yana fad'in " sannu da zuwa Manya manya maganin k'ananu ,  zagayeshi tayi da niyar wuce shi ya rik'e mata hijab , tana waiwayo wa ta d'aukeshi da mari tana fad'in " cikani mara mutunci kawai , angaya maka kowa ma irinka ne sha sha wanda baisan mutuncin kansa ba , duk wannan abun da Aysha tayiwa Khalid a idanun mutane tayi masa , wani abu yaji yataso masa ransa yayi mugun b'aci , wato shi yarinyar nan zata mara agaban mutane ? tabbas zai koya mata hankali saita gane bata da wayo ,  bai kula ta ba ya k'yaleta ta shige tayi tafiyar ta abinta .......

Sosai Aysha take samun samari amman duk wanda zaizo ba daniyar aure yake zuwar mata ba ,  kowa yazo burinsa ace yayi amfani da ita saboda kyan surar da Allah yayi mata , wata rana taje walimar wata k'awar ta a makaran ta ta had'u da Farouq ,  Farouq sosai ya nunawa Aysha soyayya tamkar da gaske , tunda ya fahimci su Aysha ba wasu masu kud'i bane yafara bud'e mata ido da kud'i ,  tun Aysha nak'in karb'ar kud'i a hannunsa har takai takawo tana ansa , nan yasa Gogal a gaba ya nuna mata shifa so yake ya auri Aysha da gaske , sosai Gogal tayi murna dajin hakan , dama tanaso ace Aysha ta auri wanda zai zame mata mijin marainiya , wanda zai kula da ita sosai koda bata numfashi  , tunda Farouq yanuna da gaske yake son Aysha tuni ta saki jiki dashi ,  komai na rayuwa sai da Farouq ya d'auke musu shi a cikin gidan , dai dai da k'osan da Gogal take sai da Farouq ya hanata ......

Sosai suka saki jiki dashi tamkar wani d'an uwan su , sai da yabari sun shak'u sosai sannan yafara fito mata da kalar halin sa ,  tashin farko ya gayyace ta wai birthday d'in abokinsa , Aysha bata kawo komai ba ta shirya ta bi Farouq tare da yiwa Gogal k'aryar zasu je duba Auntyn sa a asibiti ,  batare da ja ba Gogal ta yadda tare da cewa suyi mata sannu ....

Koda Aysha suka zo wajen Birthday ita da Farouq nan aka shiga ihu , ji tayi ana kiran sa da wani suna wai me Kaca kaca , nan tafara ganin kalar halinsa dan rungumar mata ya shigayi a gabanta tamkar wani bunsuru , bata gama mamakin halinsa ba taji ya janyo ta jikinsa tare da rungumota suka nufo wani step , nan ya tsiya ya musu lemo a kofi tare da bata yace " bisimillah Baby ki jik'a mak'oshin ki , Aysha kasa shan lemon tayi kawai ta zubawa Farouq idanu tana kallon sa , ganin ta zuba masa ido tak'i shan lemon yasa yafara mata fad'a " haba Baby kowa anan fa mu yake kallo kuma ko yaushe a cikin cika musu baki nake akan Babyna wa yayyi yace , haka yashiga lallab'a Aysha har yasamu tasha lemon , ashe sunsa mata k'wayar kashe jiki aciki , ba'afi minty biyar ba jikin Aysha ya mutu tafara ganin wani yanayi , koda Farouq yaga haka tuni suka fara shewa shida abokansa tare da murnar samun Nassara , nan suka d'auke ta cak suka shiga wani b'angaren da ita suka sata cikin wani d'aki , Aysha tana ji tana gani takasa motsi har Farouq ya fara rabata da kayan jikin ta , haka ya hau ruwan cikin ta yafara mu'amala da ita , bayan ya gama sauran Abokansa su uku suma kowanne sai da yai sannan suka k'yale Aysha , duk abinda suke mata tana jinsu kuma tana ganinsu har suka kammala , jikin ta har yanzu kamar ba nata ba haka take ji , hawaye ne ke fitowa ta cikin idanun ta tana dana sanin zuwan ta duniya , cikin ranta take fad'in wato itakuma tata k'addarar haka tazo mata , tanajin Farouq nacewa " ashe ma sauran wasu ce wlh naji ta ba virgin ce ba , nan suka shiga magan ganu akan yadda suka ji Ayshar , d'ayan yace " kaca kaca wallahi Babyn tana da ruwa sosai fa ga wani zak'i datake dashi , Farouq yace " duk tuwan ta bata kai Ummi kankana ba , dan ita in kana tare da ita har tsartuwa take , haka suka fice daga d'akin suka bar Aysha a wannan halin tamkar wata gunki a gado........

*Nagaji da Rashin Comment*
_Zantafi hutu sai wani lokacin_
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🥴🥴

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association*
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page._ 10

Aysha suka koma d'aki ita da Alhajin su Farouq sai kusan hud'u sannan suka fito , shiryawa tayi cikin shigar ta data sa bayi , duban Alhaji tayi sannan tace " zan zo na wuce gida kaga yamma tafara yi , murmushi Alhaji yayi sannan yace " tabbas kinci sunan naki Babyn dad'i , dazaki zauna anan wallahi bazan tab'a gajiya dake ba saboda zak'in ki , wani farr Aysha tayi da ido sannan tace " bana kwana ko ina sai agida saboda Kakata , amman ko yaushe kake buk'ata ta to nikuma zan amsa kiran ka , Alhaji Na Lamma ya taso har zuwa inda Aysha ke tsaye yazo jikin ta gab yana wani shinshinar ta kamar bunsuru yace " ai ni inda ace ko yaushe kina tare dani to bazan tab'a gajiyawa ba , amman nasan bazan tab'a samun haka ba sai dai nayi hak'uri , amman kimin Alk'awari gobe ma zakizo kibani wannan jikin naki me tarin dad'i da ni'imah ? Aysha tayi murmushi tace " indai da kud'in ka me zai hana ko yaushe ka kirani a shirye nake amman banda dare , Alhaji ya sumbaci kumatun ta yace " bani account number d'in ki saina turo miki kud'in kayan kwalliya , nan take Aysha ta tura masa account Number d'in ta , ba'afi minty uku ba taji shigowar kud'i da sauri ta duba dubu d'ari biyar ne ya turo mata , nan tayi masa godiya tasa kai tafice abinta ........

Aysha na fitowa daga cikin gate hause d'in Alhaji , ta hango wata motar me bak'in glass a gefe a ajiye , ko kallon wajen motar batayi ba tasa kai ta wuce abinta , Farouq da sauri ya fito daga cikin motar yabi bayan Aysha yana fad'in " Aysha Aysha plss dan Allah kitsaya zamuyi magana , cak Aysha ta tsaya batare da ta jiyo ba , Farouq yana k'arasowa ya dube ta yace " haba Aysha abinda nayi miki har yakai ga kina kula mahaifina ? kinsan bazan tab'a jin dad'i ba mutuk'ar naganku kedashi plss , wani murmushin takaici Aysha tayi sannan tadubi Farouq tace " au dama Wannan bunsurun shine mahaifinka ? ashe shi ka gada wajen bunsuran ci da iya lalata 'Ya'yan Al'umma , wani abu Farouq yaji ya tsaya masa a k'irjin sa jin irin sunan da Aysha ta kira Mahaifin sa dashi , cikin ransa yake fad'in " da ace ba lallab'aki nazo yi ba wlh da saina yi miki abinda bazaki kuma kiran wani da sunan haka ba bare kuma mmahifina , a fili kuma yace " nasan banyi miki dai dai ba amman dan Allah inaso ki yafemin duk da bani ne nafara sanin ki ba , Aysha tace " tabbas ba kaine ka fara sanina ba amman kuma kaine ka janyo min tsunduma wa cikin wannan rayuwar , Khalid yayi min fyad'e kuma tunda ganan bank'ara kusan tar wani ba sabo da ba'asan kaina akayi min ba , lokaci d'aya ya guje ni yace bai aureni ba saboda yasamu abinda yake so , ina cikin wannan halin kashigo rayuwata da taka yaudara kaima , kai da katashi sai abin naka yafi nashi dan kai har Abokan ka sai da suka sanni , sannan saboda rashin imani kashige kayi tafiyar ka abinka batare da kayi tunanin halin danake ciki ba , shikuma Mahaifinka da ka ganmu tare ni bansan mahaifinka bane shine wanda ya shigo cikin rayuwata , dan haka nikuwa bazan k'i arzik'i ba tunda har ya kirani , tana kaiwa nan tayi gaba abinta batare da ta kuma saurarar Farouq ba , biyo ta ya kumayi abaya yana fad'in " dan Allah Aysha ko nawa kikeso zan baki ki rabu da Mahaifina plss , juyowa tayi sannan tace "

Farouq a yanzu baka da abinda zaka bani , kaje kasamu Mahaifin naka kace yarabu dani mutuk'ar yarabu dani to nikuma zan hak'ura dashi , dama ni ba son sa nake ba Aljihun sa nakeso kuma nasan zansamu yadda nakeso , tana gama magana ta shige abinta tayi tafiyar ta tabarshi tsaye baki bud'e........

Aysha tana shigowa lungun gidan su taga Jabir a tsaye a k'ofar gidan , had'e fuska tayi dan ta fuskan ci nacin Jabir yayi yawa sosai inba mataki ta d'auka akan sa ba zai dameta dayawa , tana k'arasowa yace " sannu da zuwa sarauniyar mata , tun d'azu nake dakon jiranki dan nasan duk inda kike kina hanya , Aysha ta tab'e baki sanna tace " sannun ka da sa ido , to gani nadawo ko akwai abinda zan baka ne kake jirana ? Murmushi Jabir yayi sannan yace " bani da wannan matsayin sai dai ni Almajirine kuma bazan fasa zuwa bara gurunki ba har Allah yasa nasamu , dan kinsan hausawa na cewa " me nema yana tare da samu , Aysha tace " wannan haka yake zan shiga daga ciki dan agajiye nake , bata jira cewar sa ba tashige cikin gida abinta , da kallo Jabir yabi bayan Aysha yana murmushi sannan ya furta " tabbas zanci gaba da naci ko Allah zai sa ki saurareni , zuciya ta tariga da takamu da sanki mutuk'a kuma ina fatan samun nassara duk danasan kinfi k'arfina , haka ya juya yabar k'ofar gidan cike da kewar Ayshar tare da yaba kyawun halittar ta....

*Bayan kwana biyu*

Alhaji Na Lamma zuwan sa biyu gidan su Aysha amman bata fitowa , dalilin kuwa shine " duk kud'in ka duk mulkin ka indai Aysha ta kusan ceka so d'aya bata k'ara komawa koda zaka kirata sau dubu , shikuma Alhaji tuni ya rud'e sosai akan Aysha , koda ya kusanci matan sa jin su yake tamakar dusa ita kad'ai ce me zak'i , haka wata yarinyar sa da suke holewar su itama kwata kwata daya kusan ceta kasa gamsuwa yayi , shiyasa yafara zaryar zuwa gidan su Aysha tare da kiran wayar ta , yau ce rana ta uku dayazo kuma yayi sa'a tana gida , tana fitowa jiyayi tamkar yataho da gudu ya d'auke ta cak saboda dad'i , tana k'arasowa ta dubesa tace " barka da zuwa Alhaji ya hanya ? da sauri yace " ai ni hanya batamin wahala ba kamar yadda kikamin wahalar gani , shikenan kuma daga yin Abu sau d'aya kink'i yadda muk'ara had'uwa kumw , murmushi Aysha tayi sannan tace " haba Alhajina kai kanka kasan haka kawai bazan k'i komowa wajen ka ba sai da dalili , da sauri Alhaji Na Lamma yace " wanne daliline wannan wanda yasa Babyn dad'i take neman gujemin ? murmushi tayi sannan tayi wani wal da ido tace " ranar danazo gidan ka har wannan d'an naka yazo , ina fitowa ya biyoni yacimin mutunci tare da cewa duk randa yaganni da Mahaifinsa to tabbas zai d'au mataki akaina , nikuma kaga bani da kowa sai kaka ta da junan mu muka dogara , kaga kuwa dole na gudu duk abinda zaisa azo ace nashigar da kanmu cikin wani halin , Alhaji najin abinda tace yace " wato Farouq kenan bashi da mutunci ? to wallahi saina sassab'a masa akan hakan ina ruwan sa dani dazai samiki ido ahaka ? wani far Aysha tayi da ido sannan tace " to kai Alhaji me zai hana ka rabu dani kawai tunda kaga yaronka bayason wannan halak'ar tamu , Alhaji ya goge wata zufa sannan yace " shid'in banza dazai saka na rabu da abinda nakeson sa fiye da komai yanzu , dan Allah Babyn dad'i ki tausaya min kiyi hak'uri da Abinda yayi miki kizo mije kibani dad'i wallahi a k'age nake sosai , murmushi Aysha tayi sannan tace " zan hak'ura amman akwai sharad'in da zan fad'a mutuk'ar akayimin su to xanci gaba da biyamaka buk'atar ka , da sauri Alhaji Na Lamma

yace " inajinki fad'i dukkan sharad'in ki nikuma zanyi miki su , Aysha tace " Abu na farko danake so ayi shine inaso kabar min gate hause d'in ka , sannan kuma inaso motar da Farouq yake hawa kasa yazo har nan da ita ka k'arba kabarmin ita kyauta shikuma yakoma yawo a k'afa , mutuk'ar kayi haka to nikuma xanci gaba da baka dad'in dakakeso har lokacin da ya isheka , Alhaji Na Lamma jiki na rawa yace " duk yadda kikace haka za'ayi indai gidane ko yau zaki tare a ciki to nabaki shi , Aysha tayi murmushin mugunta sannan tace " haba Alhaji ai sai kabani takaddu sannan xan yadda da hakan , sannan kuma ka kira Farouq yanzu kasa shi yabani mukullin motar da hannunsa , Alhaji yace " angama Babyna yasa hannu A aljihu ya d'auko wayar sa....

Bugu d'aya yayi Farouq ya d'aga wayar lokacin yana tare da Abokansa , Alhaji yace " inaso kayi sauri kaje gate hause d'ina kashiga bedroom d'ina akwai wata akwati ka d'auko ta ka kawomin yanzu , da sauri Farouq yace " to Daddy amman kana inah to saina kawo maka , nan Alhaji yabawa Aysha waya tashiga yi masa kwatance , Farouq najin muryar ta yaji wani takaici ya kamashi cikin ransa yace " wallahi yarinyar nan saina koya mata hankali sosai wallahi , ya katse wayar batare da tagama masa bayani ba.......

Bayan minty goma sai ga Farouq yazo a motar sa , yana k'arasowa yak'i fitowa daga cikin motar ya kira Alhajin yace yazo , Alhaji Na Lamma yace " bazaka iya fitowa ba kenan ka kawomin sai dai ni inzo ko ? da sauri Farouq yace " aa Daddy ganinan take ya fito daga cikin motar yana nufo wajen dasuke , daman dayake unguwar bata da yawan hayaniya shiyasa ba kowa sai su , Farouq yana xuwa ya rissina yabawa Alhajin nasu wannan k'aramar akwatin , Alhaji ya ansa Farouq ya juya zai tafi Alhaji yace " tsaya mana zamuyi magana , Farouq jiyayi kamar ya wanka wa Aysha mari wacce take wani fari da idanu tana yarfar da hannu , Alhaji Na Lamma ya bud'e akwati ya ciro wasu takardu sannan yace " ga takardun Baby daga yau ni Alhaji Na Lamma na mallaka miki gate hause d'ina kyauta , wata zabura Farouq yayi yana d'agowa yana duban Daddyn nasa tare da Ayshar , bai gama dawowa dai dai ba yaji Daddyn nasa yace " Farouq bani mukullin motar ka daga yau na mallakawa Babyna motar ka dan tace ita takeso , tuni zufa tashiga zubowa ajikin Farouq yana gogewa da hannun sa , kallon Aysha yayi yaga tana masa wani irin kallo na mugunta tare da aika masa dawani shu'umin murmushi........

_Ina mik'a godiya ta ga d'aukacin Masoyana da yadda kuka tayani murnar zagayowar shekarar Haihuwa ta , nagode sosai Allah yabar k'auna_ *Ina Alfahari daku Masoyana*🥰🥰💖🌹💞
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🥴🥴

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page_. 9

Share hawayen ta tayi sannan ta mik'e zaune tana fad'in " bazan tab'a iya soyayya a rayuwa ta ba , dan nasan a yanzu duk maza sun b'aci babu meyin soyayya dan Allah sai dan kyawun  mace ko kuma dirin ta , dazara sun gama da ita su gudu subar ta su komawa wajen wata ....
Aysha Aysha taji Gogal  na kiran sunan ta , da sauri ta amsa tare da goge hawayen idanun ta ta nufi cikin d'akin Gogal d'in , tana zuwa tasame ta a kwance tana rik'e da carbi a hannu , Aysha tace " gani Gogal akwai wani abun da kike buk'ata ne ? Gogal tace " kaina keyin ciwo nakeso ki anso min magani ko zai daina ,  Aysha ta sunkuya tana dafa goshin Gogal d'in sannan tace " gashinan kuwa ya d'auki zafi sannu bari naje k'arshen layi wajen madam me chamest sai insiyo miki , fita Aysha tayi ta shiga d'akin ta sannan ta d'auko kud'i ta nufi siyowa Gogal magani ,   tana tafe cikin nutsuwa har ta iso chamest d'in ta siyo mata sannan ta jiyo dan komawa cikin gida , tan tafe taga wata motar had'add'iya ta tsaya gaban ta kad'an , har ta gif ta taji ance " barka da wannan lokacin 'Yan mata ,  da kamar ta wuce sai wata zuciyar tace " ki tsaya ko zaki samu na kati , tsayawa tayi cak batare da tace komai ba kuma bata wai waya ba , wani Alhaji tagani wanda kana ganinsa kasan nera ta zauna sosai a wajen sa , yana zuwa yace " barkanki da wannan lokacin  dafatan ban katse ki daga uzirinki ba , murmushi Aysha tayi sannan tace " baka katseni ba ina saura ran ka ,  ya gyara babbar rigar sa yace " naga kina sauri amman ga waya ta kisamin number ki sai muyi magana , Aysha tace "ok babu damuwa nan tasa masa number ta ta mik'a masa wayar , yana ansa yasa hannu ya zaro bandir d'in dubu Hamsin ya bata yace " ga wannan babu yawa sai kinjini , Aysha ta anshe kud'in ta tana masa godiya ta shige abinta ta barshi tsaye yana kallon ta.......

Tana shiga gida ta kulle musu k'ofa sannan ta nufi d'akin Gogal , bata maganin tayi tasha sannan ta kunna mata fanka dayake anayin zafi agarin ,  fitowa tayi ta nufi d'akin ta ta rufo k'ofa

tare da hayewa katifa tana d'aukar watar ta , gani tayi anyi mata 10 misscall fitar ta , dubawa tayi taga numbobi iri iri wanda bata san suba , A k'a'idar Aysha mutuk'ar ka kirata bata kusa da waya to kotazo tagani bata bin kiran , dan haka kawai ta kunna data tafara chat abinta , wani kiran ne ya shigo wayar ta da wata b'akuwar Number , har ta kusa katsewa sannan ta d'aga tana karawa a kunne , daga can b'angaren akace Aminci agareki sarauniyar dake mulki a zuciya ta , Aysha najin muryar tagane Alhjin da suka had'u ne dashi , cike da kissa irin tata tace "Barka da wannan lokacin Alhajina dafatan ka koma gida lafiya , Alhaji na Lamma jiyayi wani shauk'i ya kamasa yadda ta kirasa da suna Alhajin ta , murmushi yayi sannan yace " lafiya lau na koma sai kewar ki dana keyi tamkar inganki a tare dani , Aysha tace " mekakeci ba k'asa na zuba ai ganina har sai kagaji , Alhaji yace " inaso gobe kizo gate hause d'ina muji dad'inmu , wani takaicine ya kama Aysha cikin ranta tace " daman nasan hakan ce zata faru , wai wannan mutumin tsofai tsofai dashi yake fad'in muji dad'in mu , wanda yayi jika dani amman saboda lalata wai dani zaiji dad'i , su kwata kwata ko tunanin mutuwa babu aransu sai dai tunanin duniya , tabbas zakaji dad'i amman zakayi danasanin had'uwa da *'Yar Hannu* , jitayi yana cewa Baby ko dai bazaki bani kayan ruwan bane naji kinyi shuru ? wani murmushi Aysha tayi sannan tace " kare da kud'in sa Alkaki ai sai nagaban k'warya , indai ka shirya biyana to zanzo maka yini , Alhaji yace " na shirya biyanki mutuk'ar zaki shayar dani zumarki , dan haka inaso gobe wajen sha d'aya na safe ki sameni a gate Hause d'ina mu more juna , Aysha tace " sha kuruminka zaka ganni in Allah yakaimu , nan suka shiga hira wacce rabi duk batsa yake mata tamkar ba Babban mutum ba......

*Washe gari*

Tunda Aysha ta tashi ta gyara ko 'inah na gidan nasu , Gogal tana zaune tana lazimi har Aysha ta kammala musu girki , zubowa tayi sukaci tare suna hira abinsu , bayan sun gama tayi wanke wanke sannan ta shiga wanka , tana fitowa ta shirya cikin shigar ta data saba yi , nan tabawa Gogal dubu biyu tace " ki rik'e a hannun ki ko zakiyi wani abun nidai sai nadawo , Gogal tayi mata adawo lafiya tare da addu'ar samun nasara a cikin rayuwarta da addu'ar samun miji nagari , Aysha tana fitowa ta nufi bakin titi abinta , motar Alhaji tagani yana jiran ta a bakin titi abun har mamaki ya shiga bata , tana zuwa ta shige abinta yaja suka cillah titi , suna tafe ya dube ta yace " Babyna yakamata ki cire hijab d'in naki dan naga kwalliyar da kikamin , murmushi Aysha tayi sannan tace " haba darling minty nawa ne zaka ga komai a bayyane , haka sukai ta hira har suka k'arasa gate hause d'in Alhaji Na Lamma , suna zuwa me gadi ya bud'e musy gate ya shige da motar sa ciki ....

Suna shiga suka fito suka nufi falor cikin gidan , suna shiga Aysha tabi falor da kallo dan yagama burgeta sosai , ita gidan ma gaba d'aya yagama yi mata sosai yadda takeso , komai ta tuna tayi wani shu'umin murmushi tana zama akan luntsume miyar kujera , Alhaji yace " Baby bari na shiga nayi wanka na fito ko , Aysha tace " to ina jiran ka saika fito , tana zaune tana chat har ya fito daga wankan , daga shi sai gajeran wando tib'i tib'i yataho wajen ta , take Aysha ta shiga cikin Camera tafara masa video batare daya kula da ita ba , yana k'arasowa ya d'auke ta cak yayi cikin bedroom d'in sa da ita , suna shiga ya ajiye ta kan gadon tare da cire mata

Hijab , tuni ya cire mata kayan jikin ta yayi jifa dasu , yana ganin ta haka yafara sambatu yana yaba halittar ta tamkar wani maye , daga nan suka afka babbar harka baji ba gani  , sai da suka shafe awa d'aya da rabi suna abu d'aya sannan suka tsaya hutawa , tare sukayi wanka abinsu sannan suka fito falor hutawa ,  suna zaune a falor Alhaji ya d'ora Aysha kan cinya sai shafar ta yake tamkar wata mage ,  sunyi nisa cikin wani salon wasan aka turo k'ofar falor , dukan su suka dubi k'ofar batare da wata damuwa ba , Farouq ne ya shigo cikin falor wanda idanunsa suka sauka akan abinda Daddyn sa yakeyi da Aysha , Aysha tana ganin Farouq tagane d'an gidan Alhajine tuni taji wani dad'i ya ratsa duk wata kusurwa ta jikinta , cikin ranta ta furta " lallai yanzu zanfara wasa yadda nakeso ,  maganar Alhaji ce ta katse mata tunani inda taji yace " My son. Me yakawo ka nan kuma ? nafad'a maka banason kana biyoni gate hause d'ina komai kakeso kamin waya kawai ,  Farouq wanda takaici ya kamashi na ganin Mahaifin nasa a haka yace " Daddy wayarka akashe take kuma ina san magana dakai ta gaggawa , Aysha ta kuma shigewa jikin Alhaji tana shafa masa ko inah na jikinsa tana magana k'asa k'asa " Alhajina ka sallamesa mu koma inda muka fito dan a matse nake sosai baji ka iya sarrafa mace , Farouq yanajin ta duk abinda take cewa sannan kuma yagane ta ,  jiyayi Daddyn nasa yace masa " kaje zuwa anjima zan nemeka dan kaga ina da uziri ,  Farouq ya fita fuu daga falor dama yasan Alhajin sa yana neman mata , amman tambayar daya shiga yiwa kansa a inah Alhajin yasamo Aysha ? kodai itace ta nemo Daddyn nasa dan ta d'auki fansar Abinda yayi mata , tabbas sai yayi maganinta tunda gashi har tafara shiga tsakanin sa da Daddyn sa dole yayi wani Abun.....

*Nagaji da maganar Rashin Comment*

*Kowanne sai dai ya karanta littafi kawai*

[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*

🤒🤒

_NA_

*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪

https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir Rahim*

_Page._   8

Fitowa Aysha tayi ta d'auki buta tashiga Ban d'aki , Arwala ta d'auro sannan tafito ta shiga d'akin Gogal , bayan ta idar da sallah sukaji ana sallama a k'ofar soro , amsawa Gogal tayi tare da fitowa dan ganin waye keyin sallamar ? Hameed ne a tsaye daga farkon soron yana kallo cikin gidan , yana ganin Gogal ya durk'usa yana gaida ta cike da girmamawa , Gogal ta amsa cikin fara'a tana fad'in " sannu da zuwa bari a d'auko maka tabarma ,  da sauri Hameed yace " kibar shi kawai Baba yanzu zantafi ba jimawa zanyi ba , dama naga wata budurwa a gidan nan tadawo daga makaranta shine na biyota amman tak'i saurara ta ,  Gogal tayi murmushi sannan tace " Kayi hak'uri d'an saurayi indai Sayyada ce baza ta tsaya ba , dan indai tadawo daga makaranta bata tsayawa ko inah indai ba cikin gida ba , amman bari nayi maka magana da ita  , Hameed yace " yau nagode sosai Baba Allah yajada ranki , Gogal tayi murmushi tanajin dad'in addu'ar da Hameed yayi mata ,  shigewa ciki tayi cikin ranta tana cewa " inama Aysha ta hak'ura da Farouq d'in dan itadai bai kwanta mata sosai ba , wannan fa kana ganinsa kasan yana da nutsuwa sosai.....

Aysha tana zaune tana karatun Alk'urani taji dawowar Gogal , duban ta Gogal tayi sannan tace " kina da bak'o a zaure dan haka ki tsayar da karatun in kin dawo sai kici gaba ,  Aysha ta rufe Alk'urani tana duban Gogal tace " haba dan Allah Gogal wlh ni bana son tsayawa da kowanne namiji yanzu , wani kallon mamaki Gogal tayi mata sannan tace " wai Sayyada zama zaki tayi babu aure ne ahaka ? kina kallo dai dagani sai ke muke rayuwa dole muna buk'atar ace muma muna da dangi , Aysha tadubi Gogal tace " to innayi aure shine zaki samu dangi kenan ? Gogal tace " k'warai da gaske mana  , dan kinsan Zaki dunga haifar 'Yan biyu biyu duk shekara , murmushi kawai Aysha tayi sannan ta mik'e ta fita zuwa zauren......

Hameed tagani a tsaye  yana kallon hanyar fitowar ta , cikin ranta tace " wannan dai inaji ya had'a iri da mayu shiyasa yake danaci , sallama tayi masa sannan taja ta tsaya abinta , Hameed ya amsa sallamar tare da cewa " kiyi hak'uri da yadda nadameki ba komai bane face Soyayya , dan Allah inaso kibani dama ko yaya ne insamu gurbi acikin zuciyar ki , inason ki kuma ba da wasa nake ba dan Allah ,  Sunana Dr.Hameed Buba ni haifaffen garin Kano ne amman a yanzu ina London ina aiki ,  amman duk Family d'ina suna nan dazama kuma nima ina kawo ziyara duk bayan wata uku ko shida ,  tunda Hameed ya fad'i sunan sa Aysha tasan waye shi , dan tana yawan jin sunan sa yana yawo a kafafen yad'a labarai ,  cikin zuciyar ta tace " Hameed Buba wanda kowacce mace take burin samu yazama mallakin ta , tabbas tasan ba soyayyar Allah zaiyi mata ba , tunda yakasance d'an masu kud'i gashi yana da babban Matsayi a Nageria , tabbas shima yazo wajen tane dan cika wani burin nasa nadaban ,  a zahiri kuma tace " to madallah nagode sosai da soyayyar ka , sai dai kayi hak'uri ina da wanda zan aura  kuma na masa Alk'awari ,  dan haka kahuta lafiya sai wani lokacin 'Dan samari  ta shige cikin gida abinta

...

Hameed sosai yaji rashin dad'i akan k'in amince masa da Aysha tayi , sai dai ya d'au aniyar jure duk wani wulak'ancin daza tayi masa mutuk'ar zata soshi , sallama yakuma yi musu a cikin gidan dai dai lokacin Aysha na cire hijab d'in ta , tsaki tayi sannan tace " wannan mayen mutumin wai bazai barni haka ba ne ? Gogal tace " wai dama bai tafi ba kika shigo cikin gida ? Aysha tace " munyi sallama dashi sai dai ke yake nema inajin , Gogal ta mik'e tana fad'in " Ni kuma bari naje naji mezai cemin , Gogal na fita Aysha tanufi d'akin ta tana duba cajin data saka , wayar tagani ta kawo dan haka tafara k'okarin shiga ta dubawa , jitayi Gogal na k'wala mata kira ta mik'e ta fita tana turo baki.....

Tana zuwa Gogal ta mik'a mata kud'in da Hameed ya bata , Aysha tace " wannan kud'in kuma na meye ? Gogal tace " dama yaron nan ne yabani duk danace yabarshi amman wlh haka ya dunga magiya sai dana ansa , Aysha ta irga kud'i dubu Ashirin cif tabawa Gogal tace " ki ajiye su a gunki bari naje ko taliya ce nasamo mana sai adafa , Gogal tace " nayi girki fa mantawa nayi bangaya miki ba , ga d'an waken ki can kitchen kije kizubo kidawo muyi magana , Aysha tace " to bari na anso k'wai dafaffe sai nadawo , fita Aysha tayi rashiga d'akinta ta d'auko wayar ta dan dama so take takaiwa me cajin lungun su ya saita mata duk wani Abu da akeyi a social media , tana zuwa tasamu wajen kuwa ba kowa sai kb shi kad'ai yana jin music , sallama tayi masa suka gaisa sannan tayi masa bayani abinda zai mata , Kb dama yana so ya dunga yiwa Aysha magana amman baisamu dama ba , yau jiyayi tamkar anyi masa albishir da gidan Aljannah , tambayar sa takuma yi ko yana sai da layi ? kb yace " ina saidawa nan tace yabata layin aitel da Mtn ta had'a biyu , wayar ta mik'a masa dan ya saita mata abubuwan datace , yana ganin wayar yace " wow masha Allah wayar taki tayi kyau sosai rai yakashe , Aysha murmushi tayi kawai batare da tace komai ba , nan Kb ya shiga saita mata komai datace tana buk'ata , har wanda bata ce ba sai da ya sai ta mata sannan ya shiga nuna mata su , dayake layin nata akwai rigester tuni yasa mata data , sunfi minty 10 yana nuna mata yadda abubuwan suke , nan yasata a group group na wassshpp tare da sai ta mata yadda zatayi , sosai Aysha tayi masa godiya ta kama hanya ta taho gida abinta , koda ta dawo tasamu Gogal na gyagyad'i abinta , Kafin tashigo sai da ta rufe musu gidan dan haka tana shigowa ta d'auko d"an waken ta tafara ci , sai da tagama sannan tayi sallar isha'i tayi wa Gogal sai da safe tashige d'akin ta , kan katifa ta fad'a tare da kunna wayar ta tafara chat , tunda ganan Aysha tafara had'uwa da Alhazawan birni take cin karen ta babu babbaka ....

Babu irin neman da Aysha batayi wa su Khalid da Farouq ba amman bata gansu ba , mutuk'ar Aysha taje Hotel wajen mutum zasuyi sex sai ta faki idon sa ta kunna camera tana musu video , duk wanda yayi mata rashin mutunci ko kuma ya hana ta kud'in da sukayi da ita zai bata sai tayi masa barazana da videon sa , haka maza suka shiga shakkar ta mutuk'ar kanason zaman lafiya , Duk wanda ya kwana ya hantse a social media yasan Babyn dad'i wato Aysha *'Yar Hannu* tunda take bata bayyana asalin fuskar ta sai dai randa kuka had'u zaka santa , ko hoton dp ta data sa hoton k'irjin tane daga ita sai breazia , duk wani namiji me lafiya

yayi tozali da Dp Aysha sai ya ji sha'awa sosai ,  iya yanzu Aysha a cikin Account d'in ta tana da kud'i kusan million d'aya da wasu d'aruruwa , dan duk wasu manya masu ji da fad'a tayi mu'amala dasu  , tazama babbar *'Yar Hannu*  kawai sotake tafara bawa maza gumba a hannu yanzu.....

_Wannan shine farkon labarin_

Aysha ta mik'e tare da share hawayen ta tace " banice na maida kaina *'Yar Hannu* ba , mutane ne suka maidani  saboda basu da wani buri da yawuce suyi iskanci dani , koda yaushe inna samu saurayi to babban burinsa ya d'aukeni yaje ya lalatani , ina shigar mutunci bantsira ba sannan ina gidan mu ma bantsira ba ,  wannan dalilin ne yasa nagane a yanzu maza da yawa basa son mace dan Allah sai dan wani Abu nata ,   Hameed yasoni kuma yayi naci sosai akan in saurareshi amman nak'i , saboda shi yakasance d'an masu kud'i kuma wanda yake da babban muk'ami , nikuma banson shiga cikin irin wanna family d'in saboda gudun janyowa kaina tsana ,  wannan shine sanadin da Hameed yadaina zuwa wajena , daga k'arshe ma yabar k'asar baki d'aya ......

*Cigaban labari*

*'Yar* *Mutan* *Kanawa* _Ce_😍🌹
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Farouq tamkar ya shak'o wuyan Aysha yakeji , cikin ransa yake fad'in " wannan wacce irin shu'umar yarinya ce lokaci d'aya ta maida Mahaifinsa haka ? muryar tace ta katse mata tunani yaji tana cewa " Alhajina inaso kasa wannan yaron naka ya koyamin motar dan kasan kwata kwata ban iya ba , washe baki Alhaji yayi yana fad'in " kwantar da hankalinki Baby ko yaushe kika shirya kiyi nagana sai yafara koya miki , wani murmushin mugunta Aysha tayi sannan tace " gobe nakeso mu fara dan inaso cikin sati d'aya na iya mota ta , Alhaji yace " to angama Baby da kamar k'arfe nawa zai dunga zuwa ? Aysha tayi d'an dum kad'an ta tafi tunanin lokacin da Farouq yake kaiwa yana bacci , dan yasha gaya mata babu abinda ya tsana a rayuwar sa kamar a hanashi baccin safe , dan haka tayi murmushin mugunta tace " inaso ya dunga zuwa k'arfe takwas na safe shine nake da lokaci , sannan ka sheda masa kar ya makara ko na minty d'aya dan banason jira , Farouq najin abinda take cewa wani takaici yakuma kamashi tamkar yasa ihu , duk duniya babu abinda ya tsana sama da a hanashi baccin safe , k'arfe takwas ai ko motsi baiyi ba bare yatashi , yanajin Daddyn nasa ya amince akan zai dunga turoshi , duban Farouq tayi sannan tace " jeka shigo motar ka dawo min da ita saitin k'ofar gidan mu , wurga masa mukullin tayi ya cafe sannan yashige yabar wajen ransa nayi masa babu dad'i........

Alhaji ya dubi Ayshe yace " Baby na cika miki duk wasu sharud'a plss nima inaso ki cikamin nawa , murmushi Aysha tayi sannan ta kashe ido tace " me kakeci na baka na zuba ? ai kasan bana sab'a Alk'awari insha Allah zaka ganni zuwa gobe , Alhaji Na Lamma kwata kwata baiso ace sai gobe ba a yadda yake a buk'ace , amman ganin yadda Ayshar take hukuma ce sai da rarrashi yasa ya amince akan hakan , nan yayi mata sallama akan zasuyi waya , Farouq ne yazo ya mik'o mata mukullin motar suka shige suka tafi shida Daddyn nasa , tamkar zai saka kuka haka Farouq yakeji har suka k'arasa jikin motar Daddyn nasa..........

Aysha na dawowa gida tasamu Gogal ta rungume tana murna , Gogal tace " wane abun arzik'in kika samu kike wannan murna haka Sayyada ? Aysha ta gyara zama tafara shiryowa Gogal k'arya tace " Malaman makarantar mune yau sukayi min kyau ta saboda gasara da nacinye ta musabak'ar karatu , yanzu haka ga motar can da gida me kyau a unguwar masu kud'i sunbani , Gogal tashiga juyi tana fad'in " Alhamdulillah Sayyada lallai ked'in me sa'a ce a rayuwa , inama su Hard'o suna raye da sunga abin dad'i , nan danan ta shiga sharar hawaye tare da fatar hanci tana fad'in " Allah ya nunamin ranar aurenki haka Sayyada , wasu hawaye ne suka gangaro a kuncin Aysha , cikin ranta tace " Allah sarki Gogal da kinsan ta yadda nasamu wannan abubuwan da baki yi murna ba , tabbas nasan duk randa kika san wacece Aysha zakiyi dana sanin yarda da ita da kikayi , Ayshar datake kamila ada yanzu ta dawo fasik'a , saboda yaudarar da maza sukayi mata tazama me k'azamar rayuwa , yanzu waye zai iya auren ta a hakan ? ba a aure ta ba tana kamila bare yanzu data zama fasik'a , kuka tasaka sosai ta fad'a jikin Gogal , dana sani ta shiga cikin rayuwar ta tana tsinewa Khalid da Farouq wad'an da sune sanadin komai , Gogal ta d'auka maganar datayi akan iyayen Ayshar take kuka

, itama kukan tashiga yi tana rarrashin Aysha kafin suyi shuru dukansu ,  tashi Aysha tayi ta nufi toilet domin yin wanka , bayan ta fito ta shirya sannan tace Gogal ta lek'o waje taga motar ta ta , Gogal ta fito taga motar sai santi take tana shafawa tare da addu'ar Allah yatsare , bayan nan Aysha tayiwa me shagon gidan nasu magana akan yasamo mata wanda ya iya motar sukai ta wajen gadi zuwa gobe ,  juyawa tayi zasu shiga cikin gida taji muryar Jabir yana cewa " Congrat Aysha ashe kinyi motar haka ba labari , tsayawa tayi cak tana waigowa da sauri saboda batason Gagal tagane ,  Jabir ya durk'usa ya gaida Gogal ta amsa masa cike da fara'a sannan tashige cikin gida ,  Jabir ya matso kuda da Aysha yana murmushi sannan yace " wanne Alhajin ne yayi mana kyautar motar me wanna tsada da kyau haka ?  had'e girar sama da k'asa Aysha tayi sannan tace "  wai me kake nema a gurina haka da kake bibiyata ne ?  Murmushi Jabir ya kumayi sannan yace " Soyayyarki nake nema kibani kawai ki huta dani ,  Aysha ta matso kusa dashi tace " inaso kasani  Soyayya bata da gurbi ko d'aya ana  gurin , ban shirya soyayya ba dan haka sama taka bazan yi taba , ga mata nan kala kala ban hanaka kulawa ba zaka iya zuwa ka nemi wata ko zakasamu amman bandani , juyawa tayi zata shige cikin gida taji yace " Aysha inaso kisani muddin baki karb'i tayina ba to tabbas Gogal zata san halin da kike ciki dan nasan komai naki kishirya cikin shiri , yana gama fad'ar maganar ya juya yayi tafiyar sa yabar Aysha baki bud'e tana kallon sa , ga wata zufa dataji tana karyo mata tamkar wacce aka watsawa ruwan zafi......
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}* ✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page._ 13

Koda Aysha ta shiga gida Gogal tasamu a tsaye a hanayar zaure , tana ganin Aysha tace " kinje gunsa kin sheda masa ba nan gidan bane ko ? Aysha tace " wallahi wai wata

budurwa ce tayi masa kwatance da nan gidan a matsayin gidan su , kinsan yanzu 'yan mata sun b'aci da k'aryar gida , wai sai su nuna wani gidan a matsayin nan ne gidan iyayen su , Allah ma da yarufa mana asiri ba wani mugun abun tazo ta ajiye mana ba , dan kwanaki a hanyar makaranta naga wata budurwa ta ajiye jariri a soron wani gida , shiyasa yanzu mutane dayawa sukeyin gate saboda gudun hakan , aikuwa Gogal ta hau salati tana tafa hannaye " yo wannan anyi lalatacciyar yarinya , taya zata wurgar da jariri baiji ba baigani ba ? ai tunda ta riga ta haifesa ai tagama me wuyar , Aysha tace " shiyasa kawai tunda munsami gidan can me gate kawai wanda mukoma abin mu ko zaifi mana sauk'i , Gogal tace " gobe ma mukoma kawai tunda kince komai akwai aciki , wani dad'ine yakama Aysha cikin ranta tana murna zata yi nesa da Jabir , dan yanzu shine yazama bara zana a cikin rayuwar ta baki d'aya ......

Har kusan biyar na yamma Aysha tak'i kunna wayar ta , har aka kira magriba sannan ta kunna abar ta , kamar jiran ta Alhaji Na Lamma yake sai ga kiran sa ya shigo , a hankali ta d'aga tana sallama , daga b'angaren sa yace " haba Baby wannan horo da kikayi min ai yayi yawa sosai , kwata kwata kinsa na haukace tamkar wani zautacce sai fama nake da waya a hannu ina nemanki , Aysha cike da gundurar ta da yayi tace " ai gani inajinka fad'i damuwar ka , yadda tayi maganar kasan ba mutunci atare da ita , Alhaji yace " yanzu dai bara nazo na d'auko ki ko zuwa shad'ayane sai indawo dake , bai jira amsar ta ba ya kashe wayar itama cilli tayi da wayar kan katifa ta fito waje abinta.......

Ba'afi minty 15 sai ga Alhaji Na Lamma yazo , yaro ya aiko akayi masa kiran Aysha lokacin suna zaune ita da Gogal suna hirar su akan tashin da zasuyi gobe , Gogal tacewa yaron " kaje kace gatan zuwa yanzu , Aysha bata musa ba ta mik'e tashiga d'akin ta ta d'auko wayar ta ta fito , tana fitowa taga Alhaji ajikin motar sa yana ganin tamkar ya rungume ta haka yakeji , tana zuwa cikin yauk'i tace " sannu da k'arasowa , Alhaji ya bud'e baki yana murmushi yace " yauwa sarauniya ta yakike ? cike da izza da gadara tace " lafiya nake , zagaya wa yayi ya bud'e mata k'ofar mota yana fad'in " shigo mutafi kar mu makara dan wallahi a buk'ace nake sosai , Aysha ta kallesa tace " Na Lamma kake ko me ? inaso kasani indai nayi sex da mutum so d'aya to bana maimai tawa , dan haka babu inda zani kuma baka isa kasa nakuma baka jikina ba , tsayawa cak Alhaji Na Lamma yayi yana duban ta , nisawa yayi yace " da gaske kike dan Allah ko tsokana ta kikeyi ? dan Allah karkimin irin wannan wasan dan a buk'ace nake sosai dake , in ma wani abun kike buk'ata to a shirye nake dana baki mutuk'ar zaki biyamin buk'ata ta , Murmushi Aysha tayi sannan tace " na tab'a yima irin wannan wasan ne ? to ni bana wasa mutuk'ar na fad'i Abu to har cikin raina , a fusace Alhaji ya juyo yana fad'in " ke karki rainamin wayo mana , dan kinga ina sha'awarki da yawa shine zaki dunga yimin irin hakan , to kirik'e jikin ki andaina buk'atar taki daga yau , kuma inaso kibani takardun gidana da motar d'ana dan bakiyimin Abinda zan mallaka miki suba , wata dariya Aysha tasa ka har da tafawa sannan ta nuna sa da yatsa tace " lallai Bakasan wacece ni ba shiyasa zaka fad'i hakan , duk abinda ya shigo hannuna baya fita dan ya riga da yaxama nawa , gidan ka da motar d'anka duk mallakina ne yanzu , dan haka kashirya tarar bak'i dan gobe zamu dawo sabon gidan mu wanda kanani nida kaka ta , Alhaji Na Lamma yadu beta yace " ai daman kamar nasan zakimin tashan cin irin naku na 'yan tasha shiyasa nabaki jabin d'in takardu , sannan motar ma dama ina shawarar yadda za'ayi tadawo min hannuna , to yanzu kuwa komai zai dawo hannuna tunda baki da ikon

mallakar kadara ta ,  Aysha tayi murmushi sannan tace " bisimillah karka fasa abinda kayi niya , jikina ne dai bazan bayar ba wanda nayi ma yayi kaje can kanemi wasu tsohon banza kawai , tana gama fad'ar haka ta juya tayi tafiyar ta tana wani takun isa har ta shige cikin gida , Alhaji Na Lamma da ido ya bita yana had'iyar miyau tare da wani takaici daya zo mishi akan abinda tayi masa ,  waya ya ciro daga Aljihun sa ya danna kiran wayar Farouq yace duk inda yake yazo yana son magana dashi.........

Aysha na dawowa cikin gida tasamu Gogal a kishingid'e tana cin goro , zama tayi a kusa da ita ranta fess sai murmushi takeyi , Gogal tace " harya tafi kenan ?  Aysha tace " Ae yatafi yace ma yana gaidake , murmushi Gogal tayi sannan tace " ina amsawa Allah ya tabbatar da Alkairi nima inhuta da zaryar nan tasu  , murmushi Aysha tayi tana sunkuyar da kai cikin ranta kuma tausayin Gogal ne yakamata .......

Wajen sha d'aya da rabi na dare lokacin Gogal tayi bacci , Aysha na d'akin ta tana chat d'in ta kamar yadda ta saba , jitayi ana buga musu gida da k'arfi tamkar za'acire k'yaure ,  mik'ewa tayi ta ajiye wayar ta fito tsakar gida , d'akin Gogal ta lek'a har lokacin baccin ta take hankali kwance , a hankali ta nufo soron gidan nasu tace " waye ?  daga k'ofar gida taji ance " kibud'e min inyaso zakiga waye  bataji tsoro ko kad'an ba ta zare sakata , Farouq ne a tsaye shi kad'ai yana wani huci tamkar zaki , duban juna suka shiga yi shida ita kafin yace " kishiga ki d'auko min takardun gidan da Daddyna yabaki tare da mukullin mota ta yanzu yanzu , murmushi Aysha tayi sannan tace " shine abinda ya aiko ka kenan ?  Farouq cike da k'uluwa yace " shi ya aikoni dan haka kije ki d'auko tunkafin jikin yagaya miki yanzu yanzu , Aysha tayi murmushi batare da ta kuma cewa komai ba ta juya cikin gida  , batafi minty 5 saigata d'auke da takardu da mukulli tadawo , tana zuwa ta mik'a masa sannan ta d'auko masa katin shedar dazaije ya d'auki motar a wajen gadi , tana gama bashi tace " gashinan zaka iya tafiya dan inason kulle gidan , murmushi Farouq yayi sannan yace " ashe dai kina da tsoro haka bansani ba ? kin samawa kanki lafiya dan dayanzu kingayawa 'yan garinku , yana fama fad'in haka ya shige abinsa yayi gaba , Aysha murmushi tayi sannan tace " yadda kazo ka anshi wannan abubuwan haka zaka dawo dasu a yanzu basai gari ya waye ba ,  rufe gidan tayi ta koma cikin d'akin ta......

Wayarta ta d'auko ta  bud'e data ta hau online , aikuwa taga Alhaji Na Lamma yana kai , murmushi tayi sannan tashiga cikin Videos tafara neman videon sa , tura masa tayi sannan a k'asa tayi rubutu kamar haka  :
_Ina so ka bud'e Video nan kagani yaka mata ace ansashi a Social Media dan wasu su d'au style_...

Tana gama tura masa ta sauka gaba d'aya daga online d'in , batafi minty 5 da sauka ba saiga kiran wayar Alhaji Na Lamma , kin d'auka tayi har sai da yayi mata kira biyar ,  Ana shidan ne ta d'auka tana kaiwa kunne taji yana fad'in " dan Allah karkimin haka plss , kome kikeso kifad'amin wallahi zanyi miki , in kikasa abun nan a Social media wallahi nashiga uku , ina da surukai a 'Yaya ga matana suma ga kuma abokaina da kuma jama'ar gari dasu ke ganin

mutuncina , koda bata ga Alhaji ba amman tasan duk inda yake yana cikin tashin hankali , dan yadda yake maganar kawai zakasan ba k'aramin kad'uwa yayi ba , muryar sa ta kuma ji yana cewa " dan Allah kitaimaka plss mekikeso inyi miki ? Murmushi Aysha tayi sannan tace " inaso ka kira wayar 'Dan ka yadawomin da duk abinda yazo ya karb'a yanzu , sannan kagaya masa lallai yazo to ya durk'usa yabani hak'uri akan abinda yayimin , mutuk'ar hakan bata faru ba to tabbas Videon ka gobe dashi za'a karya kumallo a Social media , dan ni bana shakkar dan anganni a haka tunda daman sana'a tace , kit takashe wayar batare da tajira cewar saba.........

*Comment* plss

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page_. 12

A hankali Aysha ta d'aga k'afar ta tashige cikin gida , d'akin ta tashige kai tsaye ta fad'a kan katifa tana nazarin magan ganun Jabir , a haka bacci yayi gaba da ita sai da safe ta farka , wayar ta ta d'auka ta kunna aikuwa test tagani kala kala suna shigowa cikin wayar ta ,

bata tsaya bi takan suba ta mik'e ta nufi band'aki....

Bayan tayo wanka ta fito ta shirya sannan ta nufi d'akin Gogal , tana shiga tasa meta tana shan kunu da k'osai , Gogal tace " sannu da tashi yau naga kin makara sosai , Aysha ta gaida Gogal sannan ta matso tafara shan kunun itama tana fad'in " nifa Gogal gani nake tunda mun samu gida gwanda yau mutashi daga unguwar nan , Gogal tayi jim sannan tace " nikam gani nake wanda mu zauna anan saboda yadda kika fad'i gidan yayi mana girma , Aysha tace " haba Gogal bawani girma da yayi mana zamu iya zama abin mu mu kad'ai , da sonake ma mutafi harda Habu me shago ya dunga kulawa da gidan , nan Aysha ta shiga tsara Gogal har tasamu ta amince nan da kwana biyu zasu koma sabon gidan....

Farouq tunda suka taho hanya yakasa yiwa Daddyn sa magana , sai da suka iso gida sannan yadubi Daddyn nasa yace " Daddy yanzu ni a wacce motar zan dunga yawo kenan ? Daddy yace " zansiya maka wata amman kayi hak'uri baza kasamu kamar taka ba sai dai wacce bata kai taba , Farouq kad'an yarage baisa kuka ba taya shi dayake son ci gaba za amaidashi baya , yanzu indai Abokansa suka ganshi da motar da bata kai tashi tsada ba ai sunsamu abin yin gulma , tabbas zai koyawa Aysha hankali tunda duk itace sanadin hakan , Yana fita daga motar yayi b'angaren sa duk ransa a dagule.......

Hameed tunda ya koma k'asar America yakasa komai sai tunanin Aysha , daga ya rufe idanun sa itace keyi masa gizo , tunda yadawo kwata kwata abokan aikin sa suka kasa gane kansa , Aleeya budurwar sa wacce suke aiki tare babu irin tambayar da batayi masa ba akan canzawar sa amman yace bakomi , kullum in yadawo daga wajen aiki bashi da burin daya wuce ya keb'e kansa yana tunanin Aysha , abinda ke damunsa rashin sanin yaya take da kuma rashin dabara dabaiyi ba ta anso number wayar ta , yanke shawara yayi na tahowa Nageria kawai kozai samu sauk'i inya ganta.......

Tunda garin Allah ya waye Aysha taji batason yau ko soro ta lek'a , d'akin ta ta koma ta kwanta tana danna wayar ta , kiran Alhaji Na Lamma ne ya shigo tana kallo amman tak'i d'agawa , sai dayayi mata kira biyar amman tak'i d'agawa , daya ke datar ta a bud'e take sai ganin test d'in sa tayi ya shigo ta whassp , nan ma ta bud'e tagani amman tak'i masa reply , Daga k'arshe ma ta kashe datar ta ta ajiye wayar tayi kwanciyar ta abinta , tana kwance taji yaro ya shigo yana fad'in " wai ana kiran Babyn dad'i a waje , a zabure Aysha ta mik'e tana fad'in " nashiga uku waye zai min wannan aika aika haka ? bata gama tsora ba sai dataji muryar Gogal na fad'in " wace ce kuma Babyn dad'i agidan nan ? kaje kace banan gidan bane kaji wannan suna haka mara amfani da ma'ana kuma , haka tai ta fad'a har yaron yafita , Aysha jitayi jikin ta na rawa tamkar mazari da sauri ta d'auko hijab tasaka zata fito takuma jin yaron yadawo yana fad'in " wai ance anan gidan take kuma tasan kanta , Aysha tayi saurin fitowa tana fad'in " kai wannan wanne irin abune haka ? muje naga wanne d'an iska ne yake mana wannan abu haka , Gogal itama ta fito tana fad'in " nima dai bari nazo naga waye me wannan aike haka da bashi da mutunci , Aysha da sauri ta dakatar da Gogal tana fad'in " bari naje nagano ki koma

kawai basai kin fito ba ....

Aysha na fitowa waje taga Jabir tsaye ya hard'e cikin k'ananun kaya abinsa , yana ganin fitowar ta ya fara wani shu'umin murmushi yana kallon ta , tana k'arasowa a fusace tace " wai kai me kake nema a cikin rayuwa ta haka da kake damuna ?  Jabir yayi murmushi sannan yace " kan ki nake nema inaso ki anshi soyayya ta ki huta dani kawai ,  tsaki Aysha taja sannan tace " idan kuma ban ansa ba fa ?  Jabir ya matso gaf da jikin ta yace " in baki ansa ba kuma kin san sauran zancen , dan duk duniya sai tasan wace ce ke , ta yadda kike shigar mutunci kina cin zarafin hijab da nik'af  , kina janyowa ana b'atawa masu irin wannan shigar taki suna , inaso kisani zan fad'a miki hanyoyin da zaki bi dan bin umarnina ki zauna lafiya , Aysha tace " inaso kasani ko kafita daga cikin rayuwata ko kuma insa afitar mun dakai , kuma soyayyace bazan tab'a yin ta dakai ba saboda kaima ba soyayyar Allah zakayi min ba ,  murmushi Jabir yayi sannan yace " kin tab'a gani anso karuwa soyayyar Allah ne ? ai tsakanin ka da ita kawai ka murji jikin ta ka shige kabarta a wajen ,  ni bani da kud'in da zan biyaki in murji jikin ki  amman inaso ko taya ya sainayi amfani dake ,  Aysha tace " hakan ba k'aramin kuskure zakayi ba kuwa a cikin rayuwar ka  , tana gama magana ta juya zata tafi taji yace " Babyn dad'i ki saurari tambayoyin da Kakarki zata miki akan wannan sunan , dan sai tasan komai game da rayuwar da kikeyi har wannan motar da aka baki kika yi mata k'arya ,   Aysha duk da tanajin tsoro amman haka ta dake bata nuna masa ba har ta shige cikin gida abinta..........

*In naga Comment inci gaba sannan in k'ara yawan typing*

_In kuma bakuyi ba intafi hutu sai bayan sallah ajini_

*'Yar* *Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page._ 14

Alhaji Na Lamma jikinsa har rawa yake wajen neman number Farouq , goge zufar dake zubo masa yayi tare da danna kiran number Farouq , yana d'agawa yace " Daddy na anso komai gani nama taho yanzu , Alhaji Na Lamma da sauri yace " maza ka juya ka koma mata da dukkan abinda ka anso , Farouq a tsorace yace " what Daddy in koma mata dasu kace fa ? Alhajin yace " Ae maza ka juya kamaida mata dasu nace , yana gama fad'ar haka ya kashe wayar yayi cilli da ita kan kujera ya mik'e yana zagaye d'akin nasa , tambaya ya shiga yiwa kansa " taya akayi wannan yarinyar ta shammace shi haka batare da yasani ba ? tabbas duk yadda zaiyi sai ya raba ta da wannan video ko zai samu sukuni , mutuk'ar wannan video yana tare da ita to zuciyar sa zata kasan ce cikin zullumi , haka yashiga kaikawo goge zufar dake zubowa jikin sa , duk ac dake aiki a d'akin nasa sai yaji kamar ba su saboda zafin dayake ji.........

Farouq juyawa yayi da kan motar yakoma gidan su Aysha , Farouq mamaki ne yakamashi ta yadda akayi Daddyn nasa yace akoma mata da komai , yana tafe yana nazarin wane irin Abu Aysha tayiwa Mahaifin nasa har ya sauko haka ? bai wani dad'e ba ya k'araso k'ofar gidan su Aysha , yana zuwa ya fito daga motar ya zo k'ofar gidan yashiga bugu da k'arfi tamkar zai karya musu k'aure , Aysha dama tana zaune tana jiran zuwan sa , tana jin yana wannan bugun ta mik'e a hankali tayo hanyar soron gidan nasau , tana zuwa ta zare sakata tana duban Farouq d'in , shima ita yake kallo cikin kwayar idon sa ta hango zallar tsanar ta , itama kuma anata idon hakane dan ta tsani Farouq sosai , wurga mata takardun yayi tare da mukullun motar ya juya zai tafi , Aysha tace " haka kake yiwa uwarka kenan inkaje bata abu ? a fusace Farouq ya juyo tamkar d niyar marin Aysha wayar sa ta shiga ruri , dubawa yayi yaga sunan Daddyn sa ya d'aga , yana d'agawa Alhaji Na Lamma yace " inaso kabata hak'uri akan abinda kayi mata sannan in zaka bata hak'urin inaso ka rissina tamakar yadda kakeyimin , Farouq wani abu yaji yatsaya masa a k'irjin sa tamakar ya had'iyi zuciya ya mutu , baice komai ba ya kashe wayar yana duban Aysha yace " menayi miki haka kika zab'i kiyi min hukunci ta wannan hanyar ? nabaki hak'uri akan abinda nayi miki nida abokaina amman kink'i saurarena , kuma ko a lokacin da nayi miki wannan abu ai naji ba a cike kike ba , kinga daman ked'in *'Yar Hannu* ce , murmushi Aysha tayi sannan tace " kayi abinda Mahaifinka yace kayi yanzu katafi , kasan dare ne yanzu hakan ba rana ba bare ka tsayar dani , Farouq ya rissina tamkar yadda mahaifinsa ya umarce sa yabata hak'uri sannan ya shige yabar k'ofar gidan da tarin tsanar Aysha , da kallo

Aysha ta bishi tana murmushi sannan ta maida k'ofa ta rufe tayo cikin gida abinta......

Washe gari
Aysha tana tashi tagama had'a musu abin kari , Bayan sun karya tayi wanka ta fito sannan tacewa Gogal " tanaso taje gidan da zasu koma d'in taga meye babu a ciki , Gogal tace " ai da samo mana masu kura kikayi suka zo suka dib'i kayan inyaso basai mun nemi komai ba , Aysha tayi murmushi tana duban Gogal tace " ai wahala zasu sha masu kura Gogal sai dai motar , amman bari naje dai nadawo sai muga yadda za'ayi , shigar ta ta tayi wacce tasa ba ta rufe ko 'ina na jikin ta tafice daga cikin gidan....

Tayi nisa a tafiyar ta taji ance " Malama Aysha *'Yar* *Hannu* , ko bata waiwaya ba tasan Jabir ne , dan yanzu kusan shine babbar matsalar ta a cikin rayuwa , duk inda tasa k'afa tasan yana bibiyar ta amman dole tayi maganin sa tun kan dare yayi mata , wata dabara ce ta fad'o mata kawai ta juyo tana murmushi tace " Malam Jabir manyan gari yakake ? Jabir cike da mamaki yace " lafiya lau nake kema ina fatan hakan kike ? Murmushi tayi sannan tace " gashi kuwa kagani , Jabir ganin Aysha ta saki jiki dashi yasa yafara tunanin ko barazanar da yayi mata ce yasa taji tsoro , cike da jin shi wanine yace " ina zuwa haka manyan gari ? murmushi Aysha tayi sannan tace " wata k'awa tace baban ta yarasu shine zanje mata gaisuwa , Jabir yace " Ayya Allah yajik'ansa in kindawo anjima sai muyi magana ko ? Aysha tace " babu damuwa sai nadawo d'in , Allah yadawo dake lafiya ya juya yabarta ta nufi titi tana dariyar mugunta......

Gate hause d'in Alhaji Na Lamma Aysha ta nufa , tana zuwa tasamu me gadin gidan a k'ofar gate a tsaye yana jin redio , tana zuwa tayi masa sallama ya amsa yana kallon ta tamkar wanda yaga wata halittar daban , Aysha tace " inason shiga gidan nan dan zan duba wani abu , Megadin ya dube ta sama da k'asa sannan yace " baiwar Allah taya zanbarki ki shiga cikin gida batare da nasanki ba ? kuma koda nasanki taya zan bud'e miki Alhalin Alhaji bai cemin in bud'e miki ba ? d'age nik'af d'in Aysha tayi tana kallon sa sannan tace " kashiga ka gayawa Alhajin kace me gidan ce tazo tanason suyi magana , mai maita wa Megadi ya shiga yi yana fad'in " Me gidan ce tazo , haka ya bud'e gidan da saurin sa yatafi isarwa da Alhaji sak'o.....

Alhaji Na Lamma yana zaune a falor sa yana shan ruwan lipton yaji shigowar me gadi , izini yamasa yashigo suka gaisa , nan ya sheda masa zuwan Aysha da kalmar datace ya fad'i , Alhaji Na Lamma najin ance Me gidace tazo ya mik'e da sauri tamkar zai tuntsira yayo waje , Me gadin nasa ma acikin falor yabarshi tsaye baki bud'e , cikin ransa yace " wannan wacce shu'umar yarinya ce tasa Alhaji wannan rawar jiki haka ? shima biyo bayan sa yayi suka fito wajen ........

Aysha na tsaye abinta sai k'arewa unguwar kallo take , cikin ranta tashiga yaba tsarin unguwar na rashin hayaniyar mutane , ga kuma gidaje masu kyan gaske tamkar a turai layin ,

muryar Alhaji ce ta katse ta da yace " sannu da zuwa Hajjaju , Aysha ta bisa da kallo daga shi sai gajeran wando kana gani kasan baisan ya fito ba , dariya ce taso kama Aysha amman ta maze cimin ranta tana fad'in " tsohon banza kawai maganin ku ai , dan kuna da kud'i sai kurunga amfani da hakan kuna lalata yaran mutane , kana da Matanka amman saika had'a da bibiyar matan waje , a fili kuma ta amsa masa ciki ciki tamkar batason maganar , bud'e mata k'aramar k'ofar yayi yace " bisimillah mushiga daga ciki ko sai muyi magana , shigewa Aysha tayi batare da tace dashi uffan ba abinta.......

Sai data shiga falor tasamu guri ta zauna tana kuma k'arewa falor kallo , tabbas gidan yayi kyau sosai dan yagama burgeta shiyasa takeson gidan , Alhaji Na Lamma shima zama yayi yana duban ta cike da kulawa , Aysha ta gyara murya tace " anjima nakeso mudawo gidan nan shine nazo nagayamaka kayi sauri ka kwashe duk wasu abubuwanka masu muhimman ci daga ciki , sanin kan kane nida Kakata zamu dawo cikin gidan kuma batasan yadda akayi nasamu gidan ba , Alhaji Na Lamma yace " duk yadd kikeso haka za'ayi yanzu kuwa........
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*
🥴🥴

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Alhamdulillah_

*Am* *Back* ✍

_Page._ 16

Aysha sosai ta maida hankalin ta tana kallon Farouq , duk da bawata maganar arzik'i yake mata ba ba laifi ta fahimci wani abun , kusan awa d'aya suka kwashe yana nuna

mata sannan suka d'auko hanyar dawowa gida......

koda suka zo k'ofar gate d'in gidan ya tsaya batare da ya shiga ba , itama batace masa uffan ba ya sauka daga cikin motar yayi tafiyar sa ,  fitowa Aysha tayi taje ta k'wank'wasa k'ofar gidan , Habu ne ya zo da sauri ya bud'e mata yana fad'in " sannu da zuwa har kundawo kenan ? Aysha tayi murmushi tace " wallahi har mundawo  ashe in mutum ya nutsu ma babu wuya koyan motar , murmushi Habu yayi yana fad'in " Allah yasa anfara a sa'a Aysha tace Ameen......

Komowa tayi ta shiga cikin motar ta zauna sannan ta kunna tashigar da ita ciki , a laifi sosai Aysha tana da basira  , shiyasa ko a makaranta malaman ta suke alfahari da ita .....

Jabir sosai yake zuwa club club wai ko Allah zai sa yaci karo da Aysha , sai dai kwata kwata bai san zuwa club baya cikin layin Aysha ko kad'an ,  ganin yajera kwana biyu yana yawon neman ta yasa yagaji ya hak'ura da zuwa , sai dai sosai Aysha tabashi mamakin yadda a wannan karon tafishi wayo ,  tabbas duk inda take a fad'in garin nan sai ya nemo ta , zai nuna mata shima ba kanwar lasa bane ......

Kwata kwata Aysha ta manta da wani Jabir  wanda tayiwa lak'ani da d'an sa'ido , Rayuwar su sukeyi ita da Gogal da Habu cikin kwamciyar hankali ,  gashi kullum sai Farouq yazo sunfita koyan motar , yanzu haka  har ta iya sosai amman tak'i tabarsa ya huta....

Gogal sosai ta murje tayi wani kyau abinta , abinka da farar fata tamkar katab'a ta jini ya fito , kullum tana cikin ac ga kwana cikin ac ba ruwan ta da sauro , sosai Aysha take kulawa dasu wajen cin abinci medadi , duk da yanzu hankalin Gogal yana kan Aysha akan yadda taga tana kashe kud'i ,  kwata kwata Aysha ta manta da yadda take bida komai a b'oye kar Gogal tagani , yanzu har wayar ta babba ta bayyana ta tana fito da ita ,   yauma kamar kullum suna zaune a falo  suna kallo Gogal hankalin ta nakan Aysha wacce ke danna wayar ta tanayin chat d'auke da murmushi a fuskar ta ,  ganin kwata kwata ta maida hankalin ta ga waya yasa Gogal yin gyaran murya tace "  wai  Sayyada yaushe kika samu wannan Aba haka ? Aysha sai da taji hanjin cikinta ya ya mutsa kafin tayi ta maza tace " Batawa bace Gogal , ta Asma'u k'awar nan tawa ce na aro ta , kinsan ina koyan motar to dole sai da irin wayoyin nan zan iya ,   Gogal dayake ba sanin kai tayi ba tuni Aysha ta zage tashiga shirya mata k'arya , Gogal duk da ta yadda da Aysha d'ari bisa d'ari amman sai tasamu zuciyar ta dayin rawa akan Maganar Ayshar , haka dai tabar abin aranta batare da takuma cewa Uffan ba.......

Hameed kusan kullum sai yaje Unguwar su Aysha , amman kullum indai yaje zaisamu gidan yadda yabarshi , yauma yana zuwa hakan ce ta kasance kamar kullum , tsayawa yayi yana nazari sai ganin wani yaro yayi zai wuce , kiran sa yayi yaron yazo Hameed yace " dan Allah k'anina ko kasan inda masu gidan nan suka tafi ? yaron yace " wallahi tashi sukayi kuma bansan inda suka koma ba ,  Hameed ya maimai ta kalmar tashi sannan yace " kozaka shiga wancan gidan ka tambayo min inda suka koma , yaron ya kalli gidan sannan ya kalli Hameed yace " ai gidan mune kuma bamu san inda suka koma ba , nan Hameed ya zaro d'ari biyar

yabawa yaron yana fad'in " ungo to nagode kaji , yaron ya ansa yana godiya shikuma ya juya yanufi motar sa yatafi ....

Alhaji Na Lamma yana zaune a falon sa na sama yana nazarin wasu takardu , Farouq ne ya shigo d'auke da sallama abakin sa sannan yasamu waje ya zauna , gaida Mahaifin nasa yayi cike da girma mawa sanna yace " Daddy ina son yin magana dakai , Alhaji Na Lamma yadubi d'an nasa wanda yaga ya rame sosai yace " ina saura ranka , Farouq yanisa sosai sannan yace " Daddy dan Allah meye had'in ka da wannan yarinyar da har take irin wad'an nan abubuwan ? murmushi Alhaji Na Lamma yayi irin nasu na manya yace " cool down my luvly son babu abinda ya had'amu da ita kawai dai kabar wannan maganar banason kadamu , Farouq sosai yaji rashin dad'in yadda mahaifin nasa yake neman mai dashi k'aramin yaro , duban Daddyn nasa yakuma yi sannan yace " a gaskiya Daddy bazan iya hak'ura ina kallon k'aramar yarinya tana juya ka yadda takeso ba , zan je nasa meta ko wacce za'ayi wallahi sai dai ayi , mik'ewa Farouq yayi a fusace zai fita Alhaji Na Lamma yayi saurin dakatar dashi da cewa " Farouq karka kus kura kace zakaje wajen Aysha , ko kamanta laifin da kayi mata kai da abokan ka ne ? shuru Farouq yayi tare dayin k'asa dakai , cikin zuciyar sa yafara fad'in " lallai wannan yarinayar ta wuce tunanin sa wato har ta sanar da Daddyn sa abinda suka mata , baigama tunani ba yaji Daddyn nasa nacewa " inaso kafita daga sabgar Aysha , tsakanin ka da ita koya mata motar sai kuma in ta buk'aci kayi mata wani aiken , dan haka ka kiyaye banson insake jin wani abin ya b'illo , k'asa dakai Farouq yayi sannan ya amsa da to ya fice daga d'akin......

Da kallo Alhaji Na Lamma ya bi bayan Farouq , cikin ransa yace " laifinka yafi yawa sosai agun Aysha fiye da nawa laifin , nasan saboda tasan kai d'ana ne tazab'i ta rama abinda kayi mata ta wannan sigar , tabbas nasan dole wata rana Dole zata gyaru tadaina rayuwar da take , Allah yagani inasonta da aure a yanzu inda zata amince min amman nasan baxai yuwuba ma , Gashi ta sabamin da jikinta kuma haryanzu banji jiki me dadi irin saba duk irin neman matan danayi.....

Hameed yau tunda yatashi yake shaawar zama a k'ofar waje dan ya k'arewa unguwar tasu kallo , kujera ya fito da ita ya zauna tare da lapton d'insa yafara danna wa , dai dai lokacin Aysha tayi shigar ta ta hijab har k'asa tare da saka Nik'af ta fito wai zataje makaranta , tana fitowa tafara kalle kalle tamkar me neman wani abin , dai dai lokacin Hameed ya d'ago da kansa yana duban saitin wajen da Aysha take , da sauri ya mik'e yana kallon inda take sosai , cikin zuciyar sa yafara magana " tabbas wannan in ba Aysha bace to 'yar uwar tace , dan irin yadda Aysha take shigar ta itama wannan d'in haka takeyi , gashi yanayin jikinsu d'aya anya bazaije yaga fuskar taba ko Ayshar sace ? ......
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Alhamdulillah Ala Kulli Halin🙏🏻_

_Page._ 15

Aysha tace " wannan me gadin inaso ka sallamesa dan bana buk'atar sa , sannan kajawa Farouq d'anka kunne lallai karya kus kura ya tako mana cikin gida , Alhaji Na Lamma tana magana yana kallon ta tamkar ya janyota ya shak'eta ta mutu kowa ya huta , tamkar Aysha tasan me yake ayyana wa tace " kanajin tamkar ka shak'eni na mutu kowa ya huta ko ? to kasani ko ka kashe ni dole bazaka tsira ba , dan komai da mukayi k'awata tasani kuma tana da videon komai a gunta itama , murmushi Alhaji Na Lamma yayi sannan yace " meye ya kawo maganar kisa kuma Allah ma ya kiyaye ni ko kiyashi ban tab'a kashewa wa bare kuma mutum , mik'ewa Aysha tayi tana nuna masa ko ajikin ta maganar sa sannan tace " ni zan tafi sai wani lokacin in mun sake had'uwa , dan banaso ko sau d'aya naga k'afar ka agidana mutuk'ar na tare , sannan wannan kujerun karka kwashe su ina son su da kayan kallon nan , Alhaji Na Lamma yace " duk nabar miki su babu damuwa , ni da shawarar da nakeso muyi itace me zai hana ki amince kawai muyi aure da irin wannan rayuwar , nayi Alk'awarin yi miki duk abinda kikeso mutuk'ar kika amince min , Aysha ta dubi Alhaji Na Lamma sosai sai sannan tafara k'are masa kallo ganin wani k'aton tumbin sa , gashi wani bak'ikk'irin dashi sai wani murmushi yake shi ala dole ya burgeta , Itama murmushin tayi sannan tace " kayi hak'uri Alhaji ka riga ka makara , bazan auri wanda nasan d'an sa kafin nasan saba , da sauri Alhaji Na Lamma ya dube ta alamar son jin k'arin bayani " ta d'aga kai alamar da gaske take tace " tabbas Farouq yasan ni shima tunkafin nahad'u dakai , kaga bazan iya aurenka ba kuma koda aure zanyi gaskiya banajin zan iya auren ka Alhaji , dan haka nabarka lafiya sai wani lokacin , tana gama fad'ar

hakan bata jira cewar saba ta fice daga cikin Falor gaba d'aya......

A ranar su Aysha da Gogal suka tare a gidan Alhaji Na Lamma , da suka tashi tarewa basu gayawa kowa ba dan Aysha tace basai kowa yasani ba dan kar ayi musu shune tunda anga sun sami ci gaba , Habu me shagon gidan su harshi suka tare agidan saboda yana da kirki kuma suna shiri sosai dasu , motar Aysha tasa Alhaji ya tura Farouq ya d'auko ta ya kawo mata gidan da zummar fara koya mata motar cikin satin .......

Hameed tunda ya sauka a airpot yake jin wani sanyi yana ratsa zuciyar sa , tabbas zaiyi k'ok'arin shawo kan Aysha wannan lokacin , dan yana sonta sosai bayajin zai barta takuma kufce masa , a haka direban gidan su yazo ya d'auke sa suka nufi gida ....

Jabir Sai dare ya nufo gidan su Aysha dan jin maganar data ce masa zasuyi , yana zuwa yasamu gida a rufe da k'aton kwad'o , shima shagon Habu haka yake a rufe da k'aton kwad'on , har wajen k'arfe goma yana k'ofar gidan yana jiran yaga ta inda zasu b'illo , ganin sha d'aya har ta gota yasa yabar k'ofar gidan yatafi......

Washe gari haka yakuma zuwa k'ofar gidan kamar yadda yabarsa haka yagansa , tunani ya shiga yi akan ina suka tafi haka har suka kwana ? yana tsaye yaga wani yaro zai shiga jikin gidan yace " zonan kaji , yaro yazo Jabir yace " dan Allah k'anina kasan inda masu gidan nan suka tafi ? yaron yace " Gogal tashiga gidan mu jiya tace tashi zasuyi zasu koma wani gidan , Jabir yace " tashi kuma ? yaron yace Ae , Jabir yace " kasan inda suka koma dan Allah ? Yaron yace " wlh bamu san ina suka koma ba , dan bawanda yarakasu bare aga gidan , Jabir yace " to nagode sosai k'anina kaji , Yaron yatafi abinsa yabar Jabir tsaye yana kai komo , cikin ransa yace "dama tasan tashi zasuyi shiyasa ta tsaya ta saurareni jiya harda cemin wai zamuyi magana , tabbas duk inda kuka koma saina nemoki Aysha bazan tab'a k'yaleki ba......

Aysha tunda suka koma Gogal keta mamakin girman gidan , Habu kansa yayi mamakin ace wai a makaran ta Aysha aka bata kyautar gidan , dan shifa dama tuntuni yana zarginta dan dai bashi da hanyar tuhumar ta , Gogal sosai ta jinjinawa wanda yabawa Aysha kyautar wannan gida haka , ta dubi Aysha tace " gaskiya kowaye yabaki kyautar gidan nan yana da mugun kud'i sosai , wannan gida kamar gidan masu kud'i , yakamata ace kin kaini wajen sa nayi masa godiya dashi da malaman naki , Aysha sosai taji fad'uwar gaba amman sai ta dake tace " dama sonake sai mun nutsu muje kiyi musu godiya dan kwanan na ma zamu kuma yin wata musabik'ar , itace wacce in Allah yabani naci to kujerar makka za'abani , wata zabura Gogal tayi tace " Makka fa Sayyada ? Aysha tace " E mana Gogal , to kowannan gidan da motar ai sunfi kujerar Makka tsada , Gogal tace " Alhamdullilah Allah yasa kici kinga sainaje a madadin ki in sauke farali , nan Aysha ta shiga tsara Gogal zancen k'arya da gaskiya ita kuma tana yadda.......

Yamma nayi Hameed ya shirya cikin shigar sa ta Alfarma , sai zabga k'amshi yake tamkar wani sabon ango ya nufo gidan su Aysha , yana zuwa yaga gidan rufe da k'aton kwad'o , take yaji k'irjin sa ya buga yafara addu'ar Allah yasa ba tashi sukayi daga gidan ba , haka yagama zama amman ba wanda yazo wucewa ma bare ya tambayesa , haka ya juya ya tafi jiki a sanyaye yana jin tamkar ya fashe da kuka..........

Aysha ta kira Alhaji Na Lamma akan aturo mata Farouq zai fara koya mata motar , basu fi minty Ashirin da waya ba saiga Farouq yazo , koda aka sheda mata zuwan sa sai da ta b'ata lokaci kafin tafito , ta sanar da Gogal zata fara koyan motar gashinan anturo me koya mata , dayake Gogal tasan Farouq shiyasa Aysha tace dole sai dai yasaka face mark da glass kar Gogal tagane sa , haka kuwa akayi suka fice koyan motar tana rainawa Farouq hankali.......

Lokacin da suka fita a motar daga layin shi kuma Hameed lokacin ya shigo , dan shima a cikin unguwar gidan su yake haka ya shiga gida duk jiki a sanyaye ......

Aysha kuwa Farouq ko kanzil yak'i yace mata , kawai jan motar yake baya nuna mata yadda zatayi ta koya , tuni ta kira Alhaji ta sheda masa yadda suke , kiran sa yayi ya shiga masa fad'a sosai ala dole yafara nuna mata yadda zata iya motar.........

*Insha Allah gobe zanyi muku 'Yar kishiya*
_Rik'on Me Hak'uri_

*Comment* plss

*'Yar* *Mutan* *Kanawa* _Ce_😍🥰
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🥴🥴

_NA_
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_page._ 17

Kwata kwata Aysha bata kula da Hameed ba , wayar ta ta zaro a cikin jaka tana danna kiran number wani Alhaji da sukayi promise zasu had'u , tana kara wayar a kunnen ta shikuma Hameed yana k'arasowa d'auke da sallama a bakinsa , da sauri Aysha ta juyo tana duban wajen da akayi sallamar , gaban ta ne ya fad'i ganin Hameed cikin zuciyar ta tashiga tambayar " taya wannan mutum yasan gidan nan ? kuma dama har yanzu yana nan kenan ita har ta manta dashi ma , katseta yayi da cewa " baiwar Allah ko bakya amsa sallama ne ? tattaro nutsuwar ta tayi sannan tace " wa'alaikas salam , Hameed take ya gasgata lallai Aysha ce wannan , wannan muryar ta ta ko a mafarki bazai tab'a mantawa da ita ba , cike da nishad'i yace " malama Aysha dama kina nan ? Aysha tunani tafara akan tace masa ba ita bace ko kuma tace masa tayi aure yayi hak'uri , a hankali ta furta " kayi hak'uri ina da aure yanzu kar mu sab'awa Allah , wani abu Hameed yaji ya soke shi a zuciya ya mai maita kalmar " aure yaushe kikayi aure Aysha ? da sauri tace " banfi wata d'aya ba dan Allah kayi hak'uri Allah yabaka wacce tafini , tana gama maganar bata jira cewar sa ba tashige abinta , dan bata so ko kad'an yaja ta da wata maganar gudun kar yaganeta , da idanu Hameed yabi bayan Aysha da kallo cikin zuciyar sa yana nazarin kalmar ta wai tayi aure , tabbas zai koma unguwar su yayi bincike sosai akan maganar ta tunda su dai sunce tashi sukayi , kuma dole yasa ido a cikin unguwar nan dan tabbatar da maganar tata.........

Kamar kullum yau ma Aysha ba makaranta taje ba , hotel d'in Green palace taje gun Alhajin ta da sukayi alk'awarin had'uwa , tana zuwa tasamesa yana jiranta daga shi sai gajeran wando , yana ganin ta yashiga yasar baki yana mata kirari " wani far Aysha tayi da ido tana neman guri ta zauna a gefen gadon , Alhaji Bashir ya dubi Aysha yace " 'Yar Hannu meye kuma na sakomin wannan k'aton Hijab d'in ? Murmushi Aysha tayi sannan ta mik'e ta cire Hijab d'in nata , daga ita sai wata rigar bacci ce a jikinta wacce da ita wanda babu , Alhaji Bashir naganin haka ya susuce yafara k'ok'arin janyo ta jikinsa , turesa tayi tana wani irin kashe masa idanu , da sauri yafara surutai yana fad'in " haba babyna so kike ki kasheni da sonki kitaho jikina mana inji d'umin jikin naki , hannu ta mik'a masa tana fad'in " banji alart d'ina ba ai , Alhaji Bashir a rud'e yace mata " kifad'i komai kikeso zan mallaka miki mutuk'ar zaki bani jikin ki , murmushin k'eta Aysha tayi sannan tafara masa wasu salo wanda ya fitar dashi daga hayyacin sa , wayar sa ta d'auka ta shiga number account d'in sa , take tayiwa kanta transfer ta 1 million , sannan ta goge komai takuma shiga yi masa video yana tub'e , kwata kwata Alhaji Bashir baya hayyacin sa baisan tanayi ba , a haka suka fara aikata iya shegen su......

Jabir sosai yake yawon neman Aysha Hotel Hotel ,    duk inda yaje sai ya tsaya a k'ofar Hotel d'in yana ganin shige da ficen mutane , kamar kullum yau ma a Hotel d'in Green palace yaja yasamu guri ya zauna ,  yana zaune yana ganin masu shige da fice kala kala tamkar wani d'an jarida,   dai dai lokacin Aysha tagama komai sunyi sallama da Alhaji Bashir ta fito ,  tana fitowa kamar ance ta hangi k'ofar shigowa ta hango Jabir zaune suna hira da security , da sauri ta lab'e a wani guri tana maida numfashi ,  cikin Zuciyar ta tace " wai wannan mutumin shikuma me yakawo sa nan ?  tana tsaye a wajen tana lek'awa har ta shafe minty Sha biyar bai tashi ya tafi ba , duba a gogo tayi taga yamma tayi sosai lokacin komawar ta gida yayi , dabara ce ta fad'o mata ta kiran Farouq akan yaje ya d'auko mata motar ta yazo ya d'auke ta ,  aikuwa hakan tayi  Farouq  yana d'aga wayar bai musa mata ba ya amsa da to kawai ya kashe wayar......

Kamar yadda ta buk'ata haka Farouq yayi yazo ya d'auketa suka fice daga Hotel d'in ,  sai dai me ? suna fita ya kulle glass d'in motar ya d'auke hanya yashiga gudu da ita tamkar zasu tashi sama ........

Hameed tuni ya bayyana a unguwar su Aysha yana tambayar ko Ayshan tayi aure ?  sai dai duk wanda ya tambaya sai yace masa ba aure tayi ba tashi sukayi ,  sai da ya tambayi mutun uku sannan ya gasgata ya d'auko hanyar dawowa gida........
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A)✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Har Aysha ta shigo cikin gida tashige d'akin ta Habu a tsorace yake , dan yagama tsorata sosai duk da yaga babu abinda yafaru da Ayshar , mamaki yashiga yi cikin zuciyar sa yana tunanin wanda yazo gun Aysha a tsohon daren nan haka , haka dai yaja jikin sa ya nufi d'akin sa tare da rufo k'ofar........

Washe gari sai wajen shabiyu sannan Farouq ya kawo wa Aysha motar ta , sosai yanayin Farouq ya canza duk jikinsa yayi sanyi , Harya juya zai tafi sai kuma yadawo , Aysha ta dubesa tace " lafiya kuwa ko akwai maganar da zaka fad'a ? Farouq ya nisa sannan yace " Dan Allah Aysha kiyi hak'uri ki yafemin Abinda nayi miki , nasan saboda hakan kike ramawa akan Mahaifina , Murmushi Aysha tayi sannan tace " Farouq ina yafewa duk wanda ya zalunceni , sai dai gaskiya bazan tab'a yafewa wanda yayi sanadin lalata rayuwa ta ba , kafi kowa sanin wacece ni farkon had'uwar mu , amman a yanzu kunriga da kun canzamin rayuwa zuwa wani bagiren daban , batare da takuma magana ba ta shige cikin gidan idanun ta cike da k'wallah , Farouq da ido yabi Aysha sannan ya shiga jin haushin kansa , tabbas yana da Babban laifi akan komawar Ayshar haka , duk da yajita ba dai dai ba amman tana da kyawawan halaye , dana sani yashiga yi tare da tsanar duk wani namiji me hali irin nasa......

Tunda Aysha ta shige gida d'akin ta ta nufa kai tsaye , tana zuwa tafad'a kan gado tana zubda hawaye , duk duniya babu wanda ya cuceta sama da Khalid , duk randa Allah ya had'ata da Khalid to tabbas sai tashiga rayuwar sa ta ruguza komai , abinda yasa ta ma sauran mazan datake bi take musu haka saboda ai suma duk amanar Matan su suke ci , kuma da sannu saita gyara musu zama mutuk'ar sun shigo gonar ta , da zarar ta kammala duk wani abubuwan ta to zata nutsu waje d'aya sannan ta tuba , da wannan tunane tunanen bacci yayi awon gaba da ita....

Ruma tunda tadawo gida take ta murnar tayi k'awa , Sai bawa Hajiyar su labarin irin kyan da Aysha k'awar ta take dashi , Hajiya Shafa tace " kefa Ruma Allah yayiki da k'aunar mutum me kyau tuntuni , daga had'uwa da yarinya sai kifara d'oki kina lissafe lissafe , dariya Ruma tasa tana fad'in " Allah Hajiya dan dai baki ganta bane wlh tayi kyau sosai , Hajiya Shafa tace " Allah yabarku tare keda ita , yanzu kitashi kije kiyi wanka dan Khalid nasan yana hanya , Murmushi Ruma tayi tana fad'in " Nifa nagaji da yawa banajin zanyi tad'i yaud'in nan , Hararta Hajiya tayi tana fad'in " magulmaciya anaso ana kaiwa kasuwa , tund'azu yazo shine Daddyn ki ya aikesa super market ......

wacece Ruma ?

'Ya d'aya tilo a gurin Alhaji Kabeer da Hajiya Shafa , ita kad'ai Allah yabawa iyayenta shiyasa suka d'auki son duniya suka d'ora mata , duk abinda Ruma keso shi suke so koda kuwa abin yakasance badai dai ba , Khalid yaron Alhaji Kabeer ne yakasan ce yabashi yadda sosai a kasuwan cin su , tunda Khalid ya k'yallah ido akan ruma yaji duk duniya inba da itaba bazai iya

soyayya da kowa ba , sun shak'u sosai tsakanin su kuma kowa yasan da wannan soyayyar tasu , wannan kenan......

Bayan Aysha ta tashi daga bacci wanka tashiga tayi sannan ta fito , shiryawa tayi da irin shigar ta tafito ko abinci bata tsaya ta ci ba tace wa Gogal " zataje asibiti duba Baban k'awar , Gogal bata hana ta fita ba sai fatan Allah yadawo da ita lafiya......

Motar ta ta nufa ta bud'e ta shige tare da kunnah ta ta fice abinta hankali kwance , tana tafe tana direving hankali kwance taji wayar ta na ruri , dubawa tayi taga nunber bata santa ba kwata kwata , da har zata k'i d'agawa sai kuma ta d'aga tana fad'in " waye bangane number ba ? Ruma da murnar ta tace " Ruma ce wacce muka rage miki hanya , Aysha tad'an saki fuska tamkar suna ganin juna tace " haka zakice Kawata , barka ki da wannan lokaci , yagajiyar ku dafatan kunje gida lafiya ina godiya sosai da kulawa , Ruma cike da fara'a tace " haba sai kace wani Abu dama kiranki nayi nafad'a miki anjima zamu kawo miki ziyara nida Wanda zan aura , Aysha cike da jin dad'i tace masha Allah to indai nadawo zantab'oki a waya , yanzu ina hanya zani dubiyar Baban k'awata , Ruma tace " ayya babu komai kiyi masa sannu sai kindawo , sukayi sallama ko wacce ta kashe wayar , ......

Dai dai Danger aka tsayar dasu Aysha ta tsaya tana duba wayar ta , to dayake batasa Nik'af ba shiyasa bazatayi wuyar ganewa ba ga wanda yasanta , hankalin ta kwata kwata yatafi kan wayar ta dayake taga kafin a sake su sutafi za'a d'an jima , Dai dai lokacin Jabir shida Abokinsa suna kan Lifan suka tsaya dai dai jikin motar ta , aikuwa Jabir kamar ance masa kalli cikin motar aikuwa ya hango Aysha zaune akan sit d'in Direba , wata zabura yayi yana fad'in " Aysha dama nasan mutuk'ar kina garin nan wata rana saina ganki , da sauri ya dira daga kan Lifan d'in abokin nasa yana nufar motar , Kamalu yashiga k'walawa Jabir kira yana fad'in " Jabir ina zaka haka kuma ? ina kwata kwata Jabir bai ma san Kamalu na kiran saba , Jabir na k'arasowa jikin motar ya furta Aysha , aikuwa Aysha ta juyo tana kollon wajen da ake kiran ta , ido suka had'a da Jabir take gabanta yafad'i , da sauri ta d'age glass d'in duk ta rufesu , tamkar mahaukaci Jabir haka yashiga jijjiga mata murfin mota , adai dai nan kuma aka saki hannu alamar su wuce , aikuwa da gudu Aysha taja motar ta tamkar zata take Jabir ta wuce abinta , da sauri Jabir ya koma ya haye Lifan d'in Kamalu yana fad'in " dan Allah Kamalu ka bimun bayan waccan motar , duk inda tayi inaso kabita dan Allah kayi gudu sosai ...........

Tofah✍🏻

[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR* *HANNU*

🤒🤒

_NA_

*Zee* *MD*

*WOMEN* *WRITERS* *ASSOCIATION* 📚
(Domin Marubuta Mata)
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Page_. 18

Gudu sosai Farouq yake da Aysha a cikin motar , Aysha kallon sa kawai take taga iya gudun ruwan sa , dan da alama har yanzu bai san wace ce ita ba ,  sai da suka fara fita daga cikin gari sannan yaja ya tsaya yana huci tamkar wani kububuwa , duban ta yayi yace "  me kike tak'ama dashi da har kike raina mana hankali nida Mahaifina ?  shuru Aysha tayi tana kallon sa kafin tasa hannu ta zuge jakar ta ta d'auko cingum ta jefa a baki ,  wani haushine ya kuma kama Farouq yaji tamkar ya shak'eta ta mutu kowa ya huta ,  wata tsawa ya daka mata yana fad'in " ba magana nake miki ba ne ?  murmushi Aysha tayi sannan tace " inaso kasani ko Na Lamma wato Uban ka bai isa ya titsiyeni a gaba ba yanamin tambayoyi ,  wani Mari Farouq ya sakar mata tare da fad'in " ki iya bakin ki dan kinsan sarai ubana ba sa'anki bane ,  Aysha rik'e kuncin ta tayi tana duban Farouq sosai tare da mamakin irin k'arfin halin sa ,   duban ta yayi yana huci sannan yace " inaso wannan yazama last wornig da zan miki akai na da kuma Mahaifina , nabaki nan da kwana biyu ki had'a kayanki kibar wannan gidan , sannan kuma komai da kikasan na Mahaifina ne to inaso ki ajiyeshi a cikin gidan kar ki fita dashi ,  in kuma kika k'i ji to tabbas bazaki k'i gani ba ,  banza shasha sha 'yar tasha wacce batasan kanta ba ,  Aysha tamkar mutum mutumi haka ta koma sai idanu kawai da ta zubawa Farouq ,  fitowa yayi daga motar ya zagayo b'angaren da take ya bud'e tare da finciko ta waje ,  fad'uwa tayi a gefen titi har kanta sai da ya bugu , tana kallo ya bud'e motar ya shiga ya fige ta da gudun tsiya yabar ta a wajen ......

Aysha ta dad'e a haka a wajen kafin tayi yunk'urin mik'ewa , duban dare yafarayi gashi kuma tafiyar da nisa yasa ta fara k'ok'arin tsaida abin hawa ,  dayake amfara fita daga cikin gari sosai yasa ta kasa samun abin hawan ,  sai can taga wata motar gida ta taho da gudun gaske zata wuce , da sauri Aysha ta shiga sama mata hannu alamar ta tsaya ,  harya wuce can kuma

yadawo da baya har ya k'araso wajen ta ,  suna zuwa dai dai inda take direban ya zuge glass yana fad'in " lafiya kuwa baiwar Allah ?  Aysha tace " dan Allah katai makamin ka shigar dani cikin gari kar dare yayimin anan ,  ganin irin shigar ta ta kamala yasa Direban yace "bisimillah shigo ,  godiya Aysha ta shiga yi kafin ta zagaya baya ta bud'e ta shiga ,  tana shiga taga ashe a bayan akwai wata matashiyar budurwa wacce baza su wuce sa'anni ba da ita ,  da sauri Aysha tayi mata sallama  suka gaisa , dayake itama budurwar tana da sakin fuska tuni tasaki jiki tana jan Aysha da hira , duk da ran Aysha a b'ace yake ba laifi ta d'an saki jiki sunyi hira kad'an , basu fi minty goma ba suka shigo gari  nan budurwar ta tambayi Aysha inane inda zata sauka ? Aysha tace " ina nassarawa G.R.A daga farko farko , nan budurwar tace " muma wajen nan muke kinga kawai sai mu sauke ki kawai a gida ,  haka akayi kuwa dan suna zuwa layin su Aysha tanuna musu k'ofar gidan da zasu sauke ta ,  Kafin ta sauka Budurwar nan tace " to k'awata baki gayamin sunan ki ba har zamu rabu kuma , Aysha tayi murmushi tace " sunana Aysha  kefa yasunan ki , Murmushi tayi sannan tace " suna me dad'i  , ni sunana Ruma  daga yau kinxama k'awata in babu damuwa ,  nan sukayi musayar number sannan tayi musu godiya suka wuce.......

Aysha na shigowa gida Gogal ta hau fad'a " haba  Sayyada wannan dare da kika kai na lafiya ne kuwa ?  nan Aysha ta karyar da akai ta shiga shimfid'owa Gogal k'aryar wai sunje gidan gwamna ne yau sunyi masa godiya akan kyaututtukan da suka samu ,  sannan ta k'ara da fad'in " wallahi Gogal in Allah ya ci damu Hajjin nan mu biyu zamuje ta , dan har k'ara jadda damin malaman mu sukeyi , Gogal ta yashe baki tana fara'a kafin tashiga addu'ar Allah ya tabbatar ,  bayan Aysha tagama shigar da Gogal ta nufi d'akin ta danyin wanka.......

Tana shiga cikin d'akin tafad'a kan gado sannan ta fashe da kuka , sai da tayi kuka me isar ta sannan ta share hawayen ta , tashi tayi ta zauna tafara tunanin yadda zata k'onawa Farouq rai , yadda zata saka farouq yin nadama a rayuwar sa ,  ta dad'e tana sak'awa da kwancewa kafin ta tsayar da abinda zatayi masa , wani murmushi tayi sannan ta mik'e tashiga wanka abinta.......

Farouq sai jin wani nishad'i yake  , yana ganin yadda yaga Aysha ta yi shuru to tafarajin tsoronsa ,  a hankali ya furta " k'aramar karuwa kawai , yarinya k'arama tabi tasa mutane a damuwa , tabbas yasan Daddyn sa ma akwai wani abu a k'asa tsakanin sa da ita , dan in bai manta ba lokacin da yafara ganin ta ai a jikin Daddyn yaganta a zaune ,  to koma dai meye ai bai kamata tazama barazana a rayuwar saba ,  kuma koda yakaita gun birthday ai bashine yafara amfani da ita ba , dan koda ya shigeta yajita a bud'e bare tace shine yafara sanin ta , kuma ai ita kanta tasan ya wuce ajinta , tana 'yar matsiyata kuma uwa uba gata basu da wasu dangi yace zai aure ta , ai tasan bazai yuwuba  ko a mafarki , haka Farouq ya shiga gari da motar sa yana fantamawa tare da nunawa abokai motar sa tadawo........

Hameed tunda yadawo cikin layin su yafara bincike , duk da baisan daga wanne gida Aysha ta fito ba amman yatsaya dai dai inda suka tsaya yafara tambaya , sao dai duk jefi jefin mutanen da yake tambaya suna fad'in su basu san wata me irin wannan sunan ba , abinka da unguwar masu dashi , kwata kwata babu mutane da yawa wad'an da zai tambaya , masu gadin gidaje daman yake tambaya kuma duk sunce basu santa ba , haka yagaji ya nufi cikin gida abinsa.....

Bayan Aysha tayi wanka ta d'auro arwala tare dayin sallar magriba da isha'i , fitowa tayi suka ci Abinci suka tab'a hira da Gogal sannan tace bacci takeji tayi mata sai da safe tanufi d'akin ta...

Tana shiga tahaye gadon ta tare da d'auko wayar ta , whaspp tahau tafara chat abinta hankali kwance , duba number Farouq tayi tagansa Online yana chat abinsa , murmushi tayi sannan tashiga folder d'in videos wanda take ajiye bad'alar datakeyi , tana shiga takamo videon datayiwa Alhaji Na Lamma ta d'aukoshi , tana tashi ta turawa Farouq tare dayin rubutu a k'asan videon kamar haka : _Farouq kenan yaro man kaza har kai wani k'waro ne a wannan harkar ? ina kaje aka sanka ina kaje kayi suna ? inaso kasani ga wani Video nan ko zai d'ebema kewar wannan daren kafin gobe ka tsinceshi a social media yana yawo , indai zaka ci gaba da tab'a Aysha to sababbi ma na tafe wanda zaka koyi style sannan zan turawa budurwar ka wacce kakeso ka aura yar gidan Senetor dan taga sirikinta itama ta koyi style a wajen sa , nabarka lafiya kayi bacci a nutse kaji , daga farkar Na Lamma_...

Tana gama tura masa ta kashe datar tare da kashe wayar baki d'aya ta kwanta ,.......

Farouq yana ta chat da budurwar sa wacce yake masifar so , sai wani nishad'i yake suna ta soyewa abinsu , sak'o yagani yashigo da bak'uwar number , tsaki yaja yana fad'in " wai ko yaushe matan arewa zasu gane sudaina biyo maza prvt yakuma jan tsaki , da kamar bazai bud'e ba amman ganin pic d'in dayake kan dp yaja hankalin sa , hoton k'irjin mace ne akai sun cika sunyi mak'il dasu abin sha'awa , wani miyau ya had'iya kafin ya shiga cikin contact d'in , yana shiga yaga anturo masa video aikuwa hannun sa har rawa yake akan ya bud'e ko blue film aka turo masa , yana bud'ewa yafara cin karo da fuskar Daddyn sa yana wani irin nishi , nan yagansa haihuwar uwa da uba kan yarinyar da ita baya ganin fuskar ta kwata kwata sai iya jikin ta da Daddyn nasa ya kare jikin shima ba'agani sosai , wata irin zufa ce tashiga karyo masa sannan yafara karanta rubutun dake k'asan , wata zufa ce ta karyo masa tare da wani irin fad'uwar gaba , kiran wayar budurwar sa ne yashigi take yaji gabansa ya fad'i kodai ta tura mata d'in ? k'in d'aga kiran yayi har ya katse wani yasake shigowa , sai da tayi masa miss call five batare da ya d'aga ba , gashi tana ganin sa online kuma ta turo masa sak'o amman yak'i mata reply , tuni Farouq ya shiga kiran number sai dai kwata kwata tak'i tafiya akashe ake cewa , duk irin ac da fankar dasuke aiki a d'akin amman Farouq gumi yakeyi , jifa yayi da wayar kan katifa kafin ya durk'ushe a wajen , wacce irin yarinya ce wannan haka ? meyasa tashigo rayuwar su shida Mahaifinsa ? tabbas intasaki wannan video wallahi sungama kunya ta a idon duniya , Mahaifinsa d'an kasuwa ne kuma gashi yana tab'a siyasa , sannan gashi da surukai da dama yanzu wannan videon ya fita 'Yayan sa ma ya janyo musu fitowa daga gidajen

su , goge wani gumi yayi da hannun sa sannan ya furta " why Daddy zakayi haka da 'Yar cikin ka ? shiyasa kenan take musu barazana da tare da karb'e dukiyar Daddyn nasa , dole yaje yasa meta a daren nan dan ya bata hak'uri karta fitar da wannan videon , da sauri ya mik'e ya d'au mukullin motar tare da ficewa dagashi sai singlet da gajeran wando batare da ya lura ba ,.......

Aysha sosai take dariyar mugunta duk da k'asa k'asa takeyi , tuni Farouq har yazo unguwar su Aysha saboda mugun gudun dayakeyi , Allah ne ya kawosa lafiya kawai amman ya shari gudu , yana zuwa yashiga buga gidan tamkar zai karya k'auren gate d'in , Habu dayake a wajen gate d'akinsa yake tuni ya rud'e sayake b'arayi ne , kuka yafara yana fad'in " shikenan na bani na lalace kwad'ayi na ya janyomin , jin bugun yayi yawa yasa Habu rarrafowa yana neman hanyar cikin gida , Wannan bugu a kunnen Aysha akeyin sa dan tasan ko waye keyin bugun , murmushi tayi sannan ta sakko daga kan gadon ta nufo k'ofa , sai da tafara lek'a d'akin Gogal taganta tana bacci sannan ta nufo k'ofar waje , karo taci da Habu yana rarrafe tamkar k'aramin yaro tare da kuka wiwi , dariya ce ta kamata tafara cewa " Habu lafiya naganka haka ? Habu cike da yin magana k'asa k'asa yace " Hajiya Aysha bakiji b'arayi na buga gidan nan ba , murmushi tayi sannan tace " ba b'arayi bane bak'o nayi bari naje nagansa , Habu yadube ta yace " bak'o kuma a wannan daren ? karfa kije wallahi b'arayine , murmushi tasake yi sannan tace " wai to in b'arayin ne ai har sa shigo su kashemu indai takai za'abi , juyawa tayi ta nufi k'ofar gate d'in tazare sakatar , tuni Habu ya shige gida a guje shi dai bai yadda ba , .......

Aysha na bud'e gida sukayi ido biyu da Farouq wanda yayi wuri wuri dashi , d'auke kai tayi tana me fad'in " lafiya malam zakazo mana cikin dare kana mana wannan irin bugun ? Farouq cike da nadama yace " dan Allah kiyi hak'uri Aysha wallahi nasan nayi miki ba dai dai ba , dan Allah karkimin horo da abinda zai hanani yin sukuni a duniyar nan plss , Aysha tana waiwayo wa ta d'auke Farouq da wani wawan mari sannan ta kuma bashi d'aya a d'aya kuncin , sannan tace" inaso kasani Farouq mutukar so kake in hak'ura to saika durk'usa gwuiwoyinka a k'asa kaban hak'uri , sannan koma me nazama ai kaine siklar hakan ko kamanta in tuna maka , har gida kazo kasameni da niyar aurena zakayi ashe ba haka abun yake ba , haka ka d'aukeni kaje ka kaini wajen abokan ka kuka ketamin mutunci , hakan bai yi maka ba ka wulak'an tani sannan kuma karabu dani , kuma in baka sani ba Babanka banice nashiga rayuwar sa ba shine yashiga tawa dan haka dana fahimci Mahaifinka ne nikuma na b'ullo masa tahaka , shine zaka d'aukeni ka kaini bayan gari sannan kasa hannu ka mareni tare da kirana da ballagaza , to wannan daka gani kad'anne daga cikin irin videon dana yiwa Mahaifinka , kuma mutuk'ar kace zaka kuma tab'ani to tabbas zaka dunga tsintar su d'aya bayan d'aya a social media , dan suna nan nasa musu episode episode sai ka kiyaye , Farouq har k'asa ya duk'a yana bawa Aysha hak'uri tare da yin alk'awarin bazai k'ara yi mata makamancin abinda yayi ba , sannan yayi mata alk'awarin fita daga dukkan al'amuran ta , Aysha ta dubesa tace " shikenan sai a kiyaye , ra juya zata shiga cikinngida , da sauri ya mik'a mata mukullin motar ta yace ' gashi kiyi hak'uri karki turawa budurwar tawa videon plss , murmushi tayi sannan tace bazan tura ba amman gaba in ka kuma hakan wallahi itace zata fara kallon episode 2 kafin kai kagani , kumq

mukullin mota ka koma da ita gobe in ka kaita car wash sai ka kawomin abata sai da safe , batajira cewar saba ta komar da gate d'in gidan ta rufe abinta.........

*Nagode Sosai masu bibiyar book d'ina , masu min magana ta prvt ina k'ara godiya sosai da sosai , Masoyana ina Alfahari daku a duk inda kuke*😍😘😍😘🤝🌹

_Masoyana kune ni inbaku nima babu ni_🌹

*Taku a koda yaushe*

_'Yar Mutan Kanawa_ 🤝🌹
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🥴🥴

_NA_
*Zee* *MD*

*WOMEN* *WRITERS* *ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir  Rahim*

_Page._ 20

Kamal yashiga bin bayan Motar Aysha tamkar zasu tashi sama , Aysha naganin haka tasamu wani waje ta faka motar sannan ta fito a fusace , dai dai lokacin suma su Jabir suka k'araso wajen sai maida numfashi yake , saukowa yayi da sauri yana nufo wajen ta ya shiga fad'in " Aysha meyasa kike guduna ? meyasa bakyaso muhad'u dake ?

Aysha ta dubesa a wulak'an ce tace " meye had'ina dakai ? taya zaka shiga rayuwata duk inda nayi kadunga bina ko kana bina bashi ne ? Jabir ya gyara tsayuwa yana duban Aysha yace " Aysha ina sonki sosai kuma son danake miki shine dalilin dayasa nake bibiyar Al'amarinki , inaso kisani wallahi duk abubuwan danake fad'i akanki da kuma tona miki asirin danace zanyi a gun kakarki ina fad'a miki haka ne dan ki shiryu , tun farkon had'uwa ta dake zuciya ta takamu da soyayyarki , dan Allah Aysha ko sau d'aya ne kibani dama na nuna miki soyayyar dana ke miki plss , Yadda Jabir ke magana da kuma irin kalaman da yayi ba k'aramin tasiri yayi a zuciyar Aysha ba , duk wani haushin sa datakeji sai gashi tasamu kanta da sakkowa , ganin yanayin ta ya canza hakan yabawa Jabir daman k'ara shigar da kansa...

Aysha k'ofar gidan ku nan ne yazamo wajen zamana a koda yaushe , kullum sai na dunga ganin kamar zanganku kundawo zaku bud'e gidan , Kullum cikin yawo nake a gari ko Allah zai had'ani dake , sai yau Allah ya cikamin burina na ganinki , dan Allah Aysha ki fahimceni wallahi da gaske nake inasonki sosai , Aysha ta dubesa ido cikin ido dan ganin ko zata hango aibun Jabir , Jabir bashi da makusa dan kyakkyawa ne ajin k'arshe , gashi cikakken Namiji dashi komai ya had'a matsalar sa kawai rashin kud'i , dan kana ganin sa kasan bashi da abun yi ko ayanayin sittirar sa , sunfi minty 3 a haka sannan Aysha tace " naji duk maganganun ka kuma zan duba nagani sai muyi magana , Jabir yace " to yanzu kifad'a min inda kuka koma plss inaso inzo sai muyi maganar , Aysha cikin ranta tace " nan fa d'aya dan bazan aminta dakai da wuri ba har sai na gwada ka , a fili kuma tace " ni babu inda muka koma kawai Gogal tana garin mu nikuma ina Hotel da zama , kawai kabani number ka sai muyi magana , Jabir batare da yakawo komai ba ya karantawa Aysha Number sa , bayan tasa Number tayi masa sallama ta shiga motar ta tayi gaba abinta......

Kamal ya dubi Jabir yace " Abokina gaskiya wannan yarinyar me zafi ce , a inah kasamo ta haka dan ko yadda ka rud'e kad'ai yasa na tabbatar da tana da muhimman ci a gunka , murmushi Jabir yayi sannan yacewa Kamal " Aysha ta daban ce a cikin mata Abokina , tuntuni zuciya ta tayo farautar ta , duk da nasan tafi k'arfina amman ko soyayya mukayi ai nasan nayi nasara , Kamal ya dubi Jabir yace " Kasan irin wannan matan wallahi ba matan yara bane , koda sun auri yaran to sai dai in yakasan ce yaro da kud'i abokin Manya , Jabir yace " nima kasan me zan zama agaban ko zanyi kud'in da sai na auri balarabiya ma , Kamal yasa dariya yana fad'in " kana zaman lungun Abokina ? sai katashi kafara nema dan irin wannan matan ko siyan turare suka had'a ka dashi wallahi aikine , nan suka hau lifan d'in su suna hira wacce dukan ta akan Aysha ne........

Wajen shopping Aysha taje nan tashiga d'ibar abubuwan da zatayi amfani dasu , tana dube duben ta taji muryar da bazata tab'a mantawa da ita ba wato muryar *Khalid* , jiyowa tayi a hankali tana kallon inda taji maganar ai kuwa Khalid ne shida wata budurwa wacce ta juya

baya bata ga fuskar ta ba , da sauri ta kauda kanta tare da yin gaba tashiga wani b'angaren , lek'en su tashiga yi dan tana son ganin fuskar budurwar dasu tare da Khalid d'in , duk yadda taso taga budurwar abun ya faskara dan kwata kwata ba wajen take kallo ba , ita kuma gashi batason Khalid d'in yaganta da sai taje taduba fuskar budurwar tagani , tana tsaye har suka gama siyayyar suka juya zasu bar gun , koda budurwar ta jiyo sai Aysha taga face mark ne a fuskar ta tare da wani siririn glass , dafe kai Aysha tayi na rashin ganin cikakkiyar fuskar yarinyar , haka suka fice daga Shopping d'in batare da ta ga fuskar taba , bayan fitar su itama zuwa tayi ta biya kud'in kayan ta sannan ta fito......

Koda Aysha ta dawo gida duk ranta a mutuk'ar jagule yake , dan duk abinda zai tuna mata da Khalid bata k'aunar sa a cikin rayuwar ta , Khalid shine sanadin lalacewar ta , yadda ta tsani Khalid haka ta tsani mutuwar ta , Khalid ya cuceta yakuma yaudare ta ya lalata mata rayuwa , hawaye ne yashiga zubowa daga idon ta tashiga tuno yadda yake mata dad'in baki lokacin suna tare , kwanciya tayi dan jin yadda kanta ke sarawa bacci ne yayi gaba da ita batare da ta shirya ba .......

Hameed waya yake da Asibitin sa nacan k'asar London , neman sa suke sosai saboda tarin marasa lafiya da sukayi yawa , nan ya shiga basu uziri tare da sheda musu k'arshen wata yana tafe , yana kashe wayar Hajiyar sa ta dube sa tace " Yakamata ace ka koma aikin ka Hameed , ni haryan zu bansan abinda yadawo dakai k'asar nan ba alhalin lokacin zuwanka baiyi ba , Habeeb ya dubi Hajiyar sa yace " nafad'a miki akwai aikin da nazo yi Hajiya amman nakusa kamma lawa , Hajiya tace " Allah ya taimaka kuma inaso kafin katafi kaje gidan Kawun ka ku gana da Abida , kaga wata da wowar da zakayi kawai sai dai ayi maganar aure tunda itama nasan lokacin ta kammala karatun ta , Hameed nan da nan fuskar sa ta canza dan kwata kwata bayason anayi masa zancen wata Abida , to kawai yacewa Hajiyar tare dayin hanyar fita daga falor , da ido Hajiya ta bishi cikin ranta tana fad'in " yanzu kamar kai Hameed sai anta yi maka maganar aure , Allah ya kyauta yaku saka kagane.........

Ruma bayan sun dawo daga Shopping ita da Khalid suka zauna hira a babban palor gidan , Ruma ta dubi Khalid tace " My one amman kana ganin in nakaiwa k'awata wannan shopping d'in zataji dad'i ? Khalid yayi murmushi yana duban Ruma sannan yace " taya bazata ji dad'i ba kuwa , ni wallahi Baby har tsoron wannan k'awar taki nake , daga had'uwar ku duk tabi ta shiga ranki ko kulawa kindaina bani , daga munfara zance kin ringa zancen had'uwar k'awarki da cewa kaza kaza , kin manta kema me kyau ce kuma kema gwana ce wajen sace zuciyoyin mutane , Murmushi Ruma tayi sannan tace " bazaka gane irin yadda ta shiga raina bane , kuma ai kasan matsayinka daban yake a guna babu abinda ya canza , kawai dai nasan K'awata ta had'u kuma ta shiga raina dayawa , har sauri nake k'arfe hud'u tayi muje gidan su sai kagan ta ka tabbatar da nayi had'add'iyar k'awa , Murmushi Khalid yayi sannan yace " ai k'arfe hud'u da ita ake magana dan haka sai ki fara shiryawa ,......

Aysha baccin ta take sosai hankali kwance abinta , Gogal sau biyu tana lek'owa cikin d'akin tana ganin bata tashi ba , ana fara kiran sallar la'asar Aysha ta farka d'auke da salati a bakin ta , toilet kawai ta fad'a don yin wanka tare da d'auro arwala , bayan ta fito tazo gaban mirror tashiga shiryawa , kwalliya tayi bamai yawa ba sannan tasaka kayan ta , atamfa tasa riga da siket wacce ta anshi jikinta , Aysha akwai k'ira shiyasa maza dayawa suke susucewa indai suka kalli k'ugunta ,  bata d'aura d'an kwali ba kawai wani k'aramin gyale ta yafa ta nufo palor....

Samun Gogal tayi tana kallon tashar Arewa sun sako wani film , zama tayi a d'aya daga cikin kujerun Palor tana fad'in Sannu da hutawa Gogal ,  Gogal ta dubeta tace " ke zanyiwa sannu da hutawa Sayyada , yau naga kinsha bacci sosai tunda zuwana d'akin ki sau biyu kina bacci , Aysha tace " kaina ne yakemin ciwo shine nasha magani na kwanta , Gogal tace " ayya Allah ya sauwak'e amman ya daina ko ?  Aysha tace ea yadaina tunda nayi bacci ,  Gogal tace " kitashi kije kitchen ki d'auko abinci sai kici watak'il harda yunwa ma , Aysha tace " me kika dafa mana ? Gogal tace " shinkafa da wake sai kuma na yanka kayan lambu da k'wai dafaffe , Aysha tanason wake da shinkafa shiyasa ta mik'e da sauri ta nufi hanyar kitchen , sallamar Ruma itace ta tsayar da Aysha tare da juyawa tana kallon inda akayi sallamar , Ruma tagani a tsaye tana murmushi , itama Ayshar Murmushi tayi tana nufo wajen Rumar tana fad'in " oyoyo K'awata sannu da zuwa , Shigowa ciki sukayi Ruma ta zauna tana fad'in " kinganni da zumud'i ko bari banyi kin kirani kince kindawo ba nataho , cike da jin kunya Aysha tace bandad'e da shigowa ba nayi wanka zan kiraki sai gaki , a zuciya kuwa Aysha ta manta da wata Ruma ma   musamman da ranta ya b'aci akan had'uwa da Khalid ,  gaisawa sukayi sannan Ruma ta durk'usa ta gaida Gogal , da fara'a Gogal ta amsa gaisuwar Ruma tare da yi mata sannu da zuwa ,  Aysha taje cikin kitchen ta d'ebowa Ruma ruwa da lemuka ta kawo mata ,  Gogal tashi tayi tabar musu waje , Ruma ta dubi Ayshs tace " nida wanda zan aura mukazo fa , yana waje cikin motar kizo muje ku gaisa , Aysha tace " Masha Allah kice da Mijin namu kike tafe bari na d'auko Hijab d'ina sai muje mu gaisa ,  Ruma tace " haba k'awata wanne irin hijab kuma nida nakeso yaga k'awata yasan babu k'arya ta had'u  , badan Aysha taso ba tacewa Ruma to muje amman sai dai na tsaya daga ciki kishigo dashi harabar gidan , Ruma tace " na yadda nan suka fito harabar gidan ,  Ruma ta fita waje dan shigo da Khalid ita kuma Aysha ta zagaya dan d'auko kujerun da zasu zauna ,  lokacin data d'auko kujerun guda biyu a lokacin suma suka shigo cikin gidan , tunda ga nesa Aysha ta hango Khalid jere da kafad'ar Ruma suna hira cike da so da k'auna , kujerun ne suka fad'i daga hannun ta da sauri ta dafe k'irji , wato Khalid shine wanda Ruma zata aura ? ashe dama Ruma ce tagani d'azu a wajen Shopping ita dashi ?  to yanzu yazatayi yadda Khalid bazai gane taba ?  wata zuciyar tace mata  ai yanzu da da ba d'aya bane , lokacin da Khalid yasanki kina salaharki koda yaushe cikin Hijab da Nik'af , yanzu kuma kin canza tunda kin k'ara girma komai na jikin ki ya fito sannan kin k'ara haske da gogewar fata , da wannan shawarar Aysha ta nutsu ta saita kanta tare da nufo wajen da suke tsaye ,  murmushi tashiga yi dan kar su fahimci komai , kuma tanason ta nunawa Khalid ba ita bace yadda zaifi sakin jiki , tana k'arasowa shima Khalid ji yayi gaban sa ya fad'i , cikin ransa yashiga fad'in " wannan tamkar Aysha duk da a yanzu baisan inda suke ba ,  Aysha cike da saita murya tace " barka da zuwa Mijin K'awata ,  wani Murmushi Khalid ya k'ak'alo yana fad'in " Barka kadai K'awar mu dafatan munsame ku lafiya , ajiye masa kujera tayi tana fad'in " bisimillah kazauna sannan ta ajiyewa ruma itama , juyawa tayi tace ina zuwa bari na d'auko tawa nima sai musha hira , tana juyawa

Khalid yabi mazaunan ta da kallo yana had'iyar wani mugun yawu , tabbas wannan ta cika mace irin wannan k'ugu haka , inama itace zai aura da yakwashi gara , har Aysha ta k'ure idon Khalid na hanyar da tabi , Ruma sai magana takeyi amman baisan tanayi ba , duban sa tayi taga inda yake kallah take taji wani kishi ya soketa , a tsawace tace " wai me kake kallo ne haka ina magana kamin shuru ? firgigit yayi yana fad'in " wallahi yanayin gidan yayimin kyau shine nake kallon ko inyi irin wad'an can bukkokin anamu gidan , Ruma taja ajiyar zuciya tace " nima gidan ya burgeni sosai yakamata kayi mana irin bukkar , Khalid yayi murmushi yana fad'in " angama gimbiya ta yadda kikeso haka za'ayi , dai dai lokacin Ayshs ta taho rik'e da kujera a hannun ta , ido Khalid ya kuma zuba mata inda ya hanyo dukiyar fulanin ta sun cika riga a tsaye k'yam suna kallon sa , Ayshs dataga yadda yake kallon ta tuni tafara karkad'a ko inah ns jikin nata , take Khalid yafara jin wani Abu na yawo a jikin sa......

[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🥴🥴

_NA_
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 22

Khalid yana kai Ruma gida ya dube ta yace " My luv ni zanje gida zuwa Bayan isha'i insha Allah zanzo ko , Ruma ta langab'ar da kai sannan tace " Haba My Baby naga ai magariba tayi kawai kashigo kaci abinci kayi sallah kaga basai ka koma gida ba , Khalid cike da k'aguwa dason yatafi dan yakoma gidan su Aysha yace " sorry My Wifey yanzu zandawo kedai

kawai ki shirya min abinci me dad'i , yana fad'in haka ya shige motar da sauri dan bayason ta tsareshi da surutun ta ,  yana jan motar Ruma na d'aga masa hannu har yafice daga cikin gidan ,.....

Aysha na zaune suna hira da Gogal , rabin hirar duk akan Ruma ne  Aysha kebawa Gogal labarin Ruman , Sai hirar su suke cike da nishad'i suna dariya  , Habu ne ya katse su d'auke da Sallama abakin sa , amsawa sukai yadubi Aysha yace " kinada bako  a k'ofar gate yana jiranki , Aysha ta maimaita kalmar Bak'o kuma ni yake nema ? Habu yace " ke yake nema dan har na shigo dashi nabashi kujera yana harabar gidan , Gogal da saurin ta tace " kaje kace masa gatanan zuwa , Habu ya amsa da to sannan ya fice daga Palor ,  Aysha tadubi Gogal tana turo baki tace " nifa bani da wani bak'o dazai zo gashi kince ace ina zuwa haka mukayi dake ? Gogal ta mik'awa Aysha dak'uwa tana fad'in " ungo naki Aysha wai meyasa bakyason kiyi aure ne ? to wallahi ahir d'inki nagaji da ganinki a gabana , dagani sai kefa muka ragewa junan mu  , tun kina yarinya nake kewar dangi wasu sun mutu wasu kuma ban san ina suke ba , yanzu Aysha in kikayi aure Allah yabaki yara ai zanji dad'i , inaso kafin nabar duniya nabarki a hannun wanda zai zamo komai naki Aysha , Aysha sosai jikin ta yayi sanyi tadubi Gogal tace " kimin addu'a Allah yabani miji nagari shine kawai burina , nan tq mik'e ta nufi d'aki dan d'akko gyale taje taga waye yazo kuma da me yazo......

Khalid yana zaune sai latsa wayar sa yake hankali kwance Aysha tafito , tunda ga nesa tagane waye dan haka taja ta tsaya tana duban sa , murmushi tayi cikin ranta tana fad'in " tabbas  me hali baya canza hali koda ya shekarw d'ari baka gansa ba to halin sa nanan ...

Ganin duk tsayuwar ta bai san ta fito ba yasa ta nufi wajen sa cikr da yanga , d'agowa yayi yana kallon ta tare da zubawa k'ugun ta kallo , ganin yadda ya zubawa k'ugun nata idanu yasa ta kuma jujjuyashi har ta k'araso ,  sallama tayi cikin kissa da kashe murya sannan tace " ina fatan dai lafiya ?  Khalid ji yayi tamkar ya rungumota dan muryar ta tama abin sauraro ce , a kasalance ya amsa " lafiya lau Aysha dama wani muhimmin abune yakawoni wajen ki , Aysha taja kujerar dake kusa dashi ta zauna tana fad'in " Bisimillah inajinka ,

Khalid yace " dan Allah anan garin kike tun asali ko kuma zuwa kikai ?  Murmushi Aysha tayi sannan ta gyara zama tace " gaskiya ni banfi wata biyu da zuwa garin kano ba , amman asalina ni 'yar garin yobe ce acan iyayena suke nan nazo gidan uncle d'ina ne ,  Khalid wata ajiyar zuciya yayi jin ba Aysha bace kawai sunan ne yazo d'aya dakuma kamar su , amman wannan ai tafi Aysha kyau gogewa tare da cikar jiki ,  murmushi yayi mata sannan yace " dan Allah kuma baku da wasu dangi anan garin dan kina min kama da wata dana sani ? Aysha cikin zuciyar ta wata irin tsanar Khalid takeji , haka ta daure tabashi amsa da cewa " gaskiya banda Uncle d'ina bamu da kowa agarin nan  kuma matar sa har yanzu bata haihu ba , wata ajiyar zuciya yaja sannan yace " tabbas kama ce kawai dan waccen ma a wajen Kakar ta take , kuma sana'ar k'osai sukeyi talakawa ne sosai , basu da wasu dangi masu kud'i ma bare ince kun had'a dan ganta ka ,  Aysha sosai takejin zafin maganganun Khalid tare da wata tsanar sa a ranta , murmushi tayi sannan tace " shikenan dama abinda yadawo da kai kenan ? Khalid yayi murmushi yace " ea kuma a'a dan gaskiya inaso mu k'ullah abota kibani phone number ki  ,

amman dan Allah karki fad'awa Ruma kinsan bazataji dadi ba , cikin zuciyar Aysha tace " anzo wajen yanzu wasan zai fara , a fili kuma tace " taya zan gaya mata dama ina neman wanda zai dunga fita dani ina ganin gari dan bansan ko inah ba , Khalid jiyayi kamar yatshi yafara taka rawa , cikin ransa yake fad'in " dole na kore k'ishirwata a wannan lafiyayyan jikin , a fili kuma yayi wa Aysha godiya tare da ansar contact d'in ta , yana gama saka number kiran Ruma na shigowa cikin wayar sa , wani guntun tsaki yaja cikin ransa yana fad'in " mace babu aji sai nacin bala'i , shifa kawai ya yarda zai auri Ruma ne saboda kud'in Mahaifin ta dan yasan tunda ba d'a namiji garesa ba kuma itace babba a gidan komai wajen sa zai dawo , shiyasa yake ta kwantar musu da kai yana kuma sanin komai nasu ....

Nan ya d'aga yana cewa tayi hak'uri tabashi minty 30 gashinan , bai jira tabashi amsa ba ya katse wayar tare da duban Aysha , murmushi tasakar mai tana fad'in " k'awata ce takira kenan ? kai ya d'aga alamun ea sannan ya mik'e yana fad'in " ni zan zo na tafi sai ki shirya gobe mufara fita ko , Aysha ta mik'e tana turo k'irji tare da yin wata mik'a wacce indai namiji lafiyayye ne sai sandar sa ta mik'e , aikuwa tuni Khalid yayi mutuwar tsaye yana kallon k'irjin Aysha , jiyayi tamkar ya kai musu cafka ganin yadda suke tsaye k'yam suna kallon sa , lura da Aysha tayi ya fita a hayyacin sa yasa ta matso gab dashi tana fad'in " mezan sa a number taka ? sosai jikin ta yake gugar nasa jikin take ya duburbur ce yana fad'in " kisaka Kha lid , sunan ma ya kasa had'eshi saboda yanayin daya shiga , nan Aysha tayi masa sai da safe ta juya tana kad'a d'uwawu tayi cikin gida.......

Binta yayi da ido yana kuma kallon girman mazaunan ta har ta k'urewa ganin sa, da k'yar ya iya saita kansa yasamu yabar cikin gidan nasu.......

*Bayan kwana biyu*

Tuni Aysha da Khalid sun d'inke ko yaushe suna tare , kullum yana hanyar zuwa gidan su tare da d'aukar ta sufice wajen shan ice cream da sauran su , duk zuwan dayake bata bari ya shigo saboda kar tsautsayi yasa yaga Gogal shirin ta ya lalace , kuma duk fitar dasuke kullum cikin cewa Gogal tafita koyan motar dan haka bata samun wata matsala ,...

Ruma sosai tashiga damuwar canzawar da Khalid yayi , dan kullum bata samun wata kulawa daga garesa , ko waya suke basa minty 5 sai yace mata yana zuwa shikenan bazai k'ara kiran ta ba sai dai ko ita takirashi , haka zaita shimfid'a mata k'aryar wai kwana biyu aiki yamasa yawa shiyasa amman tayi hak'uri yakusa dawo wa dai dai , Ruma ta yadda da k'aryar da yayi mata shiyasa bata kawo komai ba ta amince masa ,....

Ranar da sukayi wata fita sosai Khalid yasamu had'in kan Aysha ta yadda ya tab'a jikin ta , murna sosai ya shiga yi a zuciyar sa yana fad'in " da sannu zan kai wajen da nakeso , itama Aysha a zuciyar ta tace " ka kusa zuwa inda nakeso kazo , lokacin da Khalid yake tab'a kirjin Aysha a cikin motar yana kai bakin sa a lokacin ta faki idon sa ta shiga yi masa Vedio , bayan sun rabu dashi tasamu layin ta wanda yake a k'asa ta d'ora ta nemo number Ruma ta whaspp ta tura mata wannan videon , yana shiga ta cire layin tare da ajiyeshi tana murmushin mugunta

,....

Ruma tuntana yadda da uzirin da Khalid ke bata har tadaina , gashi Daddyn ta yace mata kwana biyu Khalid baya zama sosai a kasuwa , kullum da wuri yake ficewa daga kasuwar , zama tayi tana nazarin can zawar sa da yayi lokaci d'aya , tamkar wacce aka zabura ta mik'e ta nufi d'akin ta dan d'auko wayar ta , kiran Aysha zatayi dan taje gidan su tabata shawara akan Khalid dan gaskiya tunanin sa na
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*WOMEN* *WRITERS* *ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 21

Ruma sai magana takeyi takuma jin shuru , d'agowa tayi a hankali ta tana duban sa nan taga hankalin sa gaba d'aya baya gunta , duban inda yake kallo tayi taga Aysha rik'e da tire a hannun ta ta nufo wajen nasu , wani kishi Ruma taji ya rufe ta ta yadda Khalid yake kallon Aysha , da k'afa ta zunguri Khalid firgigit yadawo hankalinsa , dai dai lokacin Aysha ta k'araso d'auke da murmushi tana fad'in " kuyi hak'uri na barku shuru ko , duk da nasan kuna nan kuna hirar ku irin ta masoya , Murmushin yak'e Ruma tayi dan kwata kwata Khalid ya b'ata mata rai , zama Aysha tayi tana ajiye lemukan data kawo musu , duban Khalid tayi tace " bisimillah Angon Ruma ga abin sanyi kasha , Khalid jin maganar Yasake tabbatar wa da kan sa lallai wannan Aysha ce , dan babu abinda ya ragu a muryar ta sai dai kawai yadda ta goge sosai tamkar wata 'yar bariki , duban ta yayi yana murmushi yace " muna godiya sosai k'awar mu ,

Ruma dai bata tanka ba dan har yanzu tanajin zafin abinda Khalid d'in yayi , sai yanzu taga haukar ta na tahowa da saurayin ta gidan  su Kawa ,  duba da irin yadda Ayshar ta had'u  komai yaji ajikin ta babu Namijin da zai ganta batare da yakuma duban ta ba ,  ganin tayi shuru Aysha tace " Kawata lafiya kuwa naga kinyi shuru ?

Ruma tayi murmushin yak'e tace " kaina ne yake sarawa yana ciwo , Aysha tace " Ayya sannu bari nashiga na samo miki magani sai kisha , Ruma tace " kibarshi ma ai yanzu zamu tafi inyaso naje gida sai nasha ,  Aysha tace " habadai tun yanzu zaku tafi  kuma gashi ko lemon dana kawo muku baku sha ba , Ruma tace " kiyi hak'uri zanzo miki zuwa na musamman sai muyi hira amman yanzu kinga kaina ciwo yake , Aysha dayake ta fahimci abinda yasa Ruma canzawa lokaci d'aya kawai murmushi tayi tace " to shikenan Allah yabaki lafiya sai munyi waya ,  Khalid kwata kwata baiso su tafi yanzu ba dan gaskiya yanaso yaita kallon Aysha ko zai ga abinda yakeso yagani , haka ya mik'e jiki a sab'ule suka tafi.......

Murmushi Aysha tayi bayan fitar su sannan tace " yarinya tabbas zaki wahalar da kanki akan wannan fasik'in ,  har yanzu Khalid bai canza hali ba duba da yadda yayi ta kallona , amman lokacin canzawar sa yayi dan yanzu wasan nata kanshi zai juyo.......

Tunda Ruma suka baro gidan su Aysha ba wanda yace da wani kanzil , ita tanajin haushin sa na irin yadda yadunga kallon Aysha shikuma yanajin haushin ta na yadda tak'i bari su dad'e , ganin shurun yayi yawa yasa Ruma yin magana "Khalid meyasa muna tare dakai amman idanunka na wajen da ba muhallinka ba ?  Cikin zuciyar sa ya furta indai zanga mace irin wannan a gabana ai bazan iya duban ki ba Ruma , a fili kuma yace " haba My luv amman sanake ko labari zaki iya rubutawa akaina ki shedar halina , kinfi kowa sanin waye ni sannan kinfi kowa sanin irin k'aunar dana ke miki ,  ko sch d'inku kinsha min k'orafi akan bana sakarwa k'awayen ki fuska , meyasa yanzu zakimin wani kallo daban ? karki manta abinda yasa nasaki jiki a gurin wannan k'awartaki saboda yadda naga kin d'aukaketa ,  amman insha Allah ko hanyar gidan su bazan k'ara ba tunda har hakan zai fara shiga tsakanin mu , tuni Jikin Ruma yayi sanyi tafara dana sanin zargin Khalid d'in datayi ,  cikin siririyar murya tace " kayi hak'uri Dear idanuwa na sun rufe a kan ka shiyasa ,  ganin yadda Ruma ta sauko yasa Khalid cigaba da shigar da ita " bakomai my luv ai nasan kishine akan abinda kike so kikayi amman ki sa aranki ke kad'ai ce mace tafarko kuma ta k'arshe data samu gurbin zama a zuciya ta , daga ke kuma bana buk'atar kowacce mace duk kyanta , wani dad'ine ya rufe Ruma tuni tasaki jiki tashiga zubawa Khalid kalaman soyayya tare da alk'awarur ruka da dama in sunyi aure , Shima haka yashiga tsara ta da nuna mata bayan ita baya buk'atar kowacce mace a rayuwar sa ,  cikin zuciyar sa kuwa Allah Allah yake yakai ta gida yadawo wajen wannan me kama da Ayshar dan yanaso ya tabbatar da wacece ita , ...

Hameed yau ma ya fito da k'udirin sake duba Aysha  , dan kiran da ake masa a k'asar London yayi yawa so yake yakoma , gashi abun yana neman kaishi ga kwanciya ciwo , dan kusan kullum baya bacci sai tunanin Aysha  wanda yazamar masa jiki ,  yana k'ok'arin fita daga

get d'in gidan su ita kuma Abida tana k'ok'arin shigowa , karo sukayi kowanne yaja da baya yana duban d'an uwan sa , Abida cike da so da k'auna ta dubi Hameed tace " Yaya Hameed ina yini , Hameed batare da ya dube ta ba yace " lafiya sannan yasa kai ya fice batare da yakuma bi takan ta ba , da idanuwa ta bishi tanajin wani sonshi na k'ara shiga ranta , tabbas Yaya Hameed ya had'u sosai ga kyau ga kud'i ta ko inah yayi , a hankali ta furta " duk yadda zanyi nasameka sai nayi Yaya Hameed , dan kaine irin mijin da nakeson kasancewa dashi miji na nunawa sa'a wanda ko wacce mace zata so samun irinsa.......

Hameed na fita yashiga tsaki yana fad'in " mace ayita kwata kwata bata da aji , samun waje yayi nesa da gidan su ya zauna yana dube dube tamkar me hango wani abu , gani yake kamar zaiga Aysha ta b'illo ta wani gidan ...

Koda Aysha ta shiga cikin gida tuni tafara karatun yadda zata fara yak'ara Khalid , tabbas duk duniya babu wanda ta tsana sama da Khalid , duk wani shirin ta na rayuwa shine ya rusa mata shi , tabbas zai gane Aysha da da ta yanzu ba d'aya bace , sai ta nuna masa yanzu ita cikakkiyar *'Yar Hannu* _Ce_ ..........

Kuyi maneji plss🤝

[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*

🤒🤒

_NA_
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Bayan sun kammala cin abincin Aysha ta dubi Ruma tace " 'yar uwa ta inaso in kuma baki shawara akan ki rage saka damuwa aranki , kici gaba da addu'a komai zaizo da sauk'i in sha Allah ,  nan Aysha tashiga bawa Ruma shawar wari tare da nasiha me saka nutsuwa  , sosai Ruma tasamu nutsuwa har tasaki jiki suka shiga hira , sai Bayan sallar Isha'i sannan Ruma tamik'e tare da yiwa Gogal sallama zata wuce gida , Aysha ta yafo gyale zata rakata titi  suka jero suna hira har suka fito daga gate d'in gidan ,  suna  fitowa waje suka ci karo da Hameed yana fitowa daga motar sa , kwata kwata Aysha bata ganeshi ba shiyasa ta d'auke kanta tana bawa Ruma labari , da sauri Hameed ya k'araso yasha gabansu yana fad'in " Barkan ku da wannan lokacin , tsayawa sukayi turus Aysha tana duban sa  , jitayi k'irjin ta ya buga saboda ganin fuskar Hameed  , tabbas bayan Jabir  anaci to lallai wannan Hameed d'in shine na biyu a shugaban  'yan naci , Ruma ce ta amsa masa da fad'in " Barka kadai bawan Allah , ya kalli Aysha yana murmushi yace " haba Aysha kin wahalar dani sosai kinsa nafara fita hayyacina ,  babu irin neman da banyi miki ba amman sai yanzu Allah yasa zan ganki , Aysha itama dai murmushin ta d'anyi tana fad'in " kayi hak'uri ina zuwa zan takawa 'yar uwata zuwa bakin titi ,  Hameed yayi murmushi yace " muje mana mu taka mata baki d'aya ai nima 'yar uwata ce ,  nan ya jera da su yana kusa da Aysha wacce yake jin bayaso tayi masa nisa ko kad'an , a haka suka k'arasa bakin titin unguwar da babu nisa  me napep suka tarar mata Hameed yabiya kud'in Ruma tamusu sallama ta tafi , ....

Juyowa sukayi tare Hameed sai jan Aysha yake da hira amman tak'i sakin jiki , wayar hannun tace tashiga ruru kiran Khalid yashigo , har ta yanke bata d'aga ba sake kira yayi akaro na biyu , Hameed yadube ta yace " wayarki fa ake kira yakamata ki d'aga kiji ko kiran nada muhimmanci ,  murmushin yak'e Aysha tayi sannan tace " nasan Gogal ce ke kirana tunda taji shuru , Hameed bai wani damu da jin hakan ba duk dayasan ba lallai Gogal d'in ce me kiran nata ba ,  suna k'arasowa k'ofar gidan Aysha ta kallesa  suka had'a idanu dan shima idanun sa akanta yake ,   wani abu taji ya ratso ta kanta har jikin ta , batasan meyasa batason had'a idanuwa da Hameed ba , yana da kwarjini da cikar haiba gashi ingarman namiji ,  a Hankali ta furta " ni zan shiga gida dan akwai abinda zanyi ,  Hameed yadube ta sannan yace " Aysha wajen ki nazo yakamata ki tsaya ko sau d'aya ne kibani lokacin ki maganar da nazao da ita tana buk'atar zama ,  ji tayi bazata iya yi masa gaddama ba samun bakin ta tayi da cewa to kashigo daga ciki sai muyi maganar ,  aikuwa Hameed ji yayi tamkar ya taka rawa jin Aysha ta yadda su shiga daga ciki suyi magana , ada in yazo gidan su tana lek'owa tagansa zata juya abinta , amman gashi yau yasamu matsayin da har tace yashigo , suna shiga gidan sai da ya yaba tsaruwar gidan , amman yana mamakin taya Aysha suka dawo wannan gidan kodama Alhaji Na Lamma d'an uwan sune ? dan shidai yasan asalin gidan na Alhaji Na Lamma ne tunda suna gaisawa sosai , dan akwai wata jinya da Alhajin yayi lokacin yana gari shine yake dubashi sosai har yasamu lafiya ,  maganar Aysha ce ta katse masa tunani tace " bisimillah ka zauna ina zuwa

, Hameed yaja kujera ya zauna fuskar sa d'auke da murmushi , juyawa Aysha tayi ta nufi cikin gidan   Hameed ya raka ta da lumsassun idanun sa , cikin zuciyar sa yana tasbihi ga ubangijin da ya halicci kyakkyawar surar Aysha , dan ko ta inah Aysha ta had'u musamman idanuwan ta da dirin jikin ta , har ta shige ciki idanunsa  na kan hanyar data bi tamkar ita yake kuma gani  , bayan kamar minty 5 saiga Aysha ta fito sanye da hijab d'in ta har k'asa tayi ainahin shigar ta , hannun ta rik'e da tire wanda yake d'auke da lemo da ruwa a kai , tana k'arasowa tayi masa sallama sannan ta ajiye tiren hannun ta kan d'an madai daicin table dake gaban sa ,  itama kujerar ta janyo ta zauna sannan ta dube sa tace " Bisimillah ga ruwa kasha ,  Hameed yayi murmushi sannnan ya d'auki ruwan yana cewa " nagode sosai da wannan karramawar taki , ruwan yasha sannan ya ajiye yana duban ta  a hankali ya furta " Aysha inso kibani aron minty 10 in gabatar miki da kaina ,  tun daga lokacin dana had'u dake zuciyata takamu da sonki sosai kullum innazo gareki bakya bani lokaci , a haka har na tattara nakaoma k'asar danake aiki wato London ,  koda nakoma mai makon in rage tunaninki sai ma k'aruwa da yayi dan kullum dake nake kwana araina , kwata kwata nadaina samun nutsuwa indai bansamu na keb'e nayi tunanin ki ba , ahaka har nafara gazawa game da aikina  ina samun matsalaloli sosai , kinsan anaso koda yaushe yakasance likitoci suna samun nutsuwa dan su samu damar kulawa da mara lafiyar su , tunda na fahimci nima me jinya ne yasani na tattaro nadawo gida nageria ,  sai dai wacce nadawo domin ta bata san inayi ba dan ina durowa k'asar nan na nufi gidan ku amman ina zuwa nasamu gidan a kulle ,  Aysha naje gidan ku yafi a k'irga amman kullum a rufe yake , na tambayi 'yan unguwar ko sun san inda kukaje sai suce suma basu sani ba , nasha zaga gari Aysha akan nemanki amman Allah bai had'a ni dake ba sai yau d'in nan , duk naganki kwanaki amman kika nuna bake ceba haka yasa na k'yaleki naci gaba da bibiya har Allah yasa na samu nasara ,  zamowa yayi daga kan kujera yad'an matso kusa da ita yana magana a hankali " dan Allah Aysha ki taimaka ki anshi soyayyata ko zan samu sauk'i daga rad'ad'in da zuciya ta kemin ,  ina sonki da gaske kuma inaso kizama matata uwar yayana ,  Aysha tunda Hameed yafara magana taji duk kalaman sa suna ratsa jikinta , tabbas tasha ganin maza da yawa kuma tayi rayuwa dasu amman meyasa shi dayake  mata magana takejin ta har cikin jikinta ? kodai shidin masoyin tane na gaskiya  shiyasa takejin hakan ?  tabbas badan tayi alkawarin bazatayi aure a rayuwar taba da babu abinda zai hana ta ansar soyayyar Hameed , sai dai kash bazata tab'a aure a duniya ba dan har yanzu bata yadda da soyayyar maza ba kawai tana kallon sune mayaudara wadan da basa son mace dan Allah sai dan wani abu nata ,   ........

*Kumin hakuri wlh nafita unguwa bansamu yin typing dayawa ba*✍🏻
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 23

Aysha ta dubi Khalid tace " kasan da wa mukayi waya ? Khalid ya girgiza kai yana fad'in " taya zan san da wa kikayi nasan dai mace ce , Murmushi Aysha tayi sannan tace " Mutuniyar ka wai zatazo yau in ina gida , Khalid ya tab'e baki sannan yace " nasan indai tazo to sai tayi zan cena , kinsan Allah Baby ni nafison inyi rayuwa da wa yayyiyar mace irin ki , inason inga budurwa ta tana bani kulawa kamar yadda kike bani , Ruma babu abinda ta iya sai k'auyan ci itafa ko romance bata bari muyi , kullum sai ta runga cewa in k'ara hak'uri in mukayi aure tazama tawa komai sai yadda nayi dashi , ...

Aysha tuni taji wani ciwo a zuciyar ta yataso , tabbas ko wacce mace me mutunci babban burin ta shine ta tsare mutuncin kanta , amman ita ta k'arfi da yaji aka b'ata mata mutuncin ta , ta sanadin haka yanzu gashi ta lalace ,hawaye ne suka cika mata idanun ta tayi saurin maidasu , dan bata so ko da wasa Khalid yasan damuwar ta , Khalid yaci gaba da magana " kin san wani Abu Baby ? Aysha ta girgiza kai alamun a'a , yace ko sau d'aya bantab'a son Ruma ba , saboda bata d'aya daga cikin Matan da nake da burin aura , kawai ina kulata ne dan kud'in Baban ta , kuma sannan ina son dukiyar kaf tazama tawa nan gaba bayan babu shi , Aysha ji tayi wata tsanar Khalid ta nunku a cikin ranta , tabbas Khalid azzalumine kuma sai takawo k'arshen zaluncin sa nan ba da jimawa ba , Murmushi tayi nasu na asalin 'Yan duniya ta dubesa tace " to meyasa ka yadda zaka aure ta bayan kuma bata d'aya daga cikin matan da kakeso ka aura ? Murmushi Khalid yayi sannan yace " Baby ai kinsan a k'ark'ashin Mahaifinta nake kinga da kunya 'yar sa ta nuna tana sona nak'i amincewa , da zarar komai yadawo hannu na zan iya rabuwa da Ruma ko kuma na auri wacce rai na keso , Aysha tace " gaskiya kai d'in ka iya buga game amman karkaje fa ayi maka Babban bugun da ya wuce naka , Dariya yasa yana fad'in " waye zai bugani alhalin ba wanda yasan meye a zuciya ta indai bake ba dana fad'a miki , kuma ni nasan ina da tabbacin bazaki fad'awa Ruma komai ba , Aysha tayi murmushi tace " haba Dear taya zan tona maka asiri , ai in nayi haka tamkar na tonawa kaina asiri ne nima , kadaina ma fad'in haka dan kasan ni taka ce kai nawa ba ta yadda za'ayi inga wani abu da zai zo ya kawo maka matsala batare da na kaudashi ba , haka Aysha ta karkace tashiga yiwa Khalid

dad'in baki sosai , nan yayi mata alk'wari komai takeso tafad'a zai siya mata , ...

Aysha tanajin haka ta kashe masa ido tace " account d'inka da zurgi kenan My Dear ? Khalid cike da shauk'in so yace "2 milloine acikin account d'ina yanzu , sai kinsan dayake ban dad'e dafara zuwa kasuwar ba , kuma ahakan ma ina had'awa da cuwa cuwa batare da me wajen ya lura ba , nan Aysha taji sirrin Kud'in da Khalid yake dashi , Murmushi tayi cikin ranta tace " yanzu zaka fara rabuwa da 1 Million kafin nan da kwana biyu ka rabu da sauran ma , cike da kissa Aysha tace " ni yanzu abinda nakeso kawai shine muje kasiyamin zobunan gold da sark'a dan ina son du sosai , Khalid ganin irin yadda Aysha ta kwanto jikin ta ajikin sa ga Na shanun ta rabin su duk sun fito yasa shi rud'ewa tare da cewa " muje Baby angama ,......

Jabir tunda suka rabu da Aysha yake ta dakon kiran ta amman shuru , gashi ya gwada layin ta amman baya tafiya kwata kwata , damuwa ya shiga sosai tare da fad'in " wato wayo Aysha tayimin batare da nagane ba , meyasa na yadda nabar ta ta tafi batate da nabi bayan ta ba ? tabbas indai yakuma ido biyu da Aysha bazai barta takuma raina masa hankali ba , kuma ai yagane number motar ta dakuma kalar motar tabbas zai ci gaba da neman ta tamkar yadda yayi kwanaki , .......

Yau saura kwana biyu Hameed yabar k'asar Nageria , hankalinsa sosai yatashi ganin har yakusa tafiya bai samu Aysha ba , yaje sau biyu unguwar su Aysha yana ganin ko Allah zai sa yayi sa'a sundawo , sai dai ko kad'an basu dawo ba kullum gidan arufe yake , yauma yana zaune a k'ofar gate d'in gidan su yana chat da wani abokin sa a can k'asar London , kwana biyu zaman cikin gidan baya masa dad'i saboda Hajiyar sa ta damesa da Maganar Abida , shikuma har ga Allah bason maganar yake ba , shifa indai ba Aysha ba haryanzu baiga macen data yi masa ba , dan acan ma London akwai mata wad'an da suke son sa sosai amman duk yak'i basu fuska........

Koda su Aysha sukaje wajen saida sark'ok'i , sai da Khalid ya siya mata na Million d'aya da dubu Hamsin , dan zab'a tayi sai dataji masu kud'i dayawa tace su takeso , Khalid sosai yaji fitar kud'in amman gudun kar ta gane ya dake tamkar wani Alhajin Birni , da suka taho hanya tasa shi ya biya da ita wani Shopping Mall tayi siyayyar dubu d'ari nan ma ya biya , Khalid suna fitowa ya nuna shima yanaso tabashi jikin ta dan haka su biya Hotel yakama musu waje , ko kad'an Aysha bata damuba dan dama jiran wannan ranar take , dan tasan daga wannan ranar bazai k'ara ganin Nonon ta bama bare jikin ta , haka sukaje Hotel Khalid ya kwashi gara sosai ,kusan sumewa yayi saboda sambatu dan iya jin dad'i yajishi a tare da Aysha , sai yake ganin ko nawa ya kashe mata bai fad'i ba ganin yadda ta rud'ashi shima , sosai yayi mamakin yadda Aysha ta k'ware wajen iya wasanni ,ko dayake bazai mamaki ba ganin ta wayayyiyar Yariya wacce tagaji da had'uwa, haka suka gama d'ebewar su sannan sukayi wanka suka nufo gida......

Aysha tun a farkon layin su tasa Khalid ya sauke ta , koda zata fita daga motar sai da Khalid yace " Babyna yaushe zamu kuma had'uwa ne ? dan gaskiya kinjiyar dani wani dad'in

da ban tab'a ji ba sai sau d'aya , Murmushi tayi sannan tace " sau d'aya Dear ashe katab'a yin sex ? Khalid yace " natab'a kwanciya da wata yarinya duk ba'ason ranta ba mukayi kuma shine farkon yina nima bana cikin nutsuwa amman haryanzu abin na raina , Aysha wani abune yataho mata ya tokare k'ahon zuciyar ta , kallon sa tayi cike da tsana tace " Saboda me ya tsaya maka arai kuma alhalin kace ba'ason ranta kayi ba ? jin yadda tayi maganar yasa ya dube ta , sai sannan Aysha tayi saurin ankarewa ta sassauta muryar ta tace " sorry Dear tausayin yarinyar naji ,amman meyasa kayi mata haka Alhalin bataso ? Murmushi yayi sannan yace " gaskiya sha'awarta tadameni kullum in muna tare to sai kinga abata a mik'e saboda yadda nake shaawar ta , ban daina jin hakan ba har sai randa na kusan ce ta , tana kuka tana magiya amman haka idona ya rufe na keta mata mutuncin ta , Aysha jitayi kamar a lokacin Khalid yake keta mata mutunci , hawaye ne ya cika idon ta wanda ta kasa iya maidasu , tabbas Khalid ya zalince ta dan shine sanadin komawar ta wannan rayuwar , yanzu waye zai aure ta a irin wannan rayuwar tata ? Meza tacewa Yaranta dazata haifa nan gaba ? taso ace Mijinta wanda zai aure ta shine zaifara sanin ta a duniya , amman Khalid ya rusa mata duk wani shirin ta ya lalata mata rayuwar ta , yasa taci gaba da sab'on mahaliccin ta , duk da tashiryu bayan zubar da cikin da tayi wanda yayi mata , Farouq shine ya maida ta ruwa shima yasa ta koma *'Yar Hannu* , tabbas Khalid azzalumine ya cuceta a rayuwar ta , jin tayi shuru yasa Khalid yin magana yace " meye naji kinyi shuru My Baby ? wani guntun Murmushi tayi sannan tace " wallahi danaji abunda kayiwa Yarinyar nan sai na tuno da wani Malamina a makaranta nima da yayimin fyad'e , Khalid yace " ayya sorry Baby kice mugun malami shine yafara yi mana hanya , nima kinsan Allah nine nafara yiwa yarinyar nan hanya , daga baya tasamu ciki nikuwa nayi mata korar kare , dan a ganina taya za'ace daga kwanciya sau d'aya wai ciki yashiga ai tazo da iskanci , sotake na aure ta ganin bata da wani asali gasu talakawa ba k'aruwa yasa na yi mata fata fata muka rabu , Aysha jitayi in bata yi saurin fita daga motar Khalid ba to tana gab da had'a masa jini da majina , shiyasa tayi saurin d'aukar kayan ta tace "muyi waya My dear , bata jira cewar saba ta fice da sauri abinta , Khalid ko ajikin sa bai kawo komai ba sai ma bin Mazaunan ta dayayi da kallo yana kuma wassafo dad'in daya sha ajikinta.......

Hameed yana zaune kamar ance masa ya kalli hanya ya hango Aysha ta nufo ta wajen dayake , da sauri ya mik'e yana murza idanun sa itace dai ba gizo take masa ba , kwata kwata Aysha bata kula da Hameed ba har tazo ta gifta ta gaban sa , haka yashiga binta batare da yayi magana ba , sai datazo k'ofar gidan su lokacin Habu na zaune yanajin radio ta wuce shi yana mata sannu da zuwa , da yauwa ta amsa ta shige ciki abinta shikuma Hameed yaja ya tsaya gana yiwa Habu sallama.........

*Ina mutukar Son Comment d'inku Masoyana*
_Yin Comment shine ke k'ara mana k'aimin yin Typing_✍🏻✍🏻

*Saina jiku*

*'Yar Mutan Kanawa*
_Ce_ 🌹😘🥰
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 24

Habu ya amsa sallamar Hameed yana duban sa , Hameed yace " Abokina dan Allah inaso kamin magana da wacce ta shiga gidan nan , Habu ya dubi Hameed tabbas yaso gane fuskar sa saboda yana yawan zuwa gun Aysha da dad'ewa lokacin suna wancan gidan , Habu ya nisa sannan yace " gaskiya yanzu ta dawo daga Makaranta nasan ba lallai ta fito yanzu ba , sai dai ko kabari zuwa anjima in ta huta sai nayi mata magana , Hameed ya dubi Habu sannan yace " nan ne gidan su kenan ? Habu yace ea.

Hameed yayi wata ajiyar zuciya kafin yace " nagode abokina xuwa anjima zan dawo nasan lokacin ta huta , nan yayi wa Habu sallama ya juya cike da murna ya nufi gida , tabbas yau yasan zai kwana cikin farin ciki na ganin wacce ya dawo Nageria domin ta , duk da yaso ace bai baro k'ofar gidan ba har sai yaganta , amman gudan Habu yace masa bazata fito yanzu ba yasa ya hak'ura , dan haka yanzu in anyi sallar Magriba zai shirya yaje gareta ya bayyana mata abinda ke zuciyar sa.....

Aysha tana shiga tasamu Gogal na zaune tana kallo , bayan tayi mata sannu da gida ta

shige d'akin ta dan ta watsa ruwa , tunowa tayi da siyayyar da tayi a motar Khalid tayi sauri d'aukar waya tashiga kiran sa , yana d'agawa yace mata " Babyna me kayan ruwa ya akayi kin barni da tunaninki tunda kika tafi , wani murmushin takaici Aysha tayi jin sunan da yaki rata dashi , cike da kasalalliyar Murya tace " My D nayi mantuwa a cikin motar ka , murmushi yayi sannan yace " nima sai yanzu nagani dan haka ni mantuwar nan tamin dad'i dan ko bakomi na sake dawowa na kalli kyakkyawar fuskar Mata ta , Wani abu Aysha taji ya tsirga mata a kwanyar kanta , ada lokacin datake Ayshar ta sanda takeson Khalid indai yace mata matar sa har wani dad'i takeji , amman a yanzu tamkar yasa mata dalmar wuta , dan ji tayi takuma tsanar sa a ranta , shurun da yaji tayi shine yasa yace " naji kinyi shuru Aysha ko nayi laifi dan naki raki da sunan Mata ta ? Da sauri Aysha tace " taya zanyi fushi naji ka kirani da kalmar da nadad'e ina jiran ta daga bakin ka , duk a tunani na kawai muna abota ne amman bazaka iya auren mace irina ba , Khalid ya zaro ido tamkar yana gaban Aysha yace " ni asuwa da zan k'i mace kyakkyawa irinki , ina kallon kaina ne kawai a wanda basu isa ki aura ba saboda yanayin ki da kuma irin gidan da kika fito , Murmushin mugunta Aysha tayi sannan tace " kadaina cewa haka My D kasan shi so baruwan sa da haka , sai dai ina ganin in mukayi haka tamkar zamuci amanar Ruma ne , Khalid yace " dan Allah kidaina saka wannan bagidajiyar a lissafi nifa nafad'a miki ko sau d'aya ban tab'a son taba , kinsan manufa ta akan ta ki kwantar da hankalin ki kawai kibani had'in kai , Aysha tace " karka damu Nawan nabaka , wani tsalle Khalid ya buga kafin yace " ina nan hanya in anyi sallar isha'i nasan lokacin Ruma tazo ta tafi , Aysha tace " shikenan sai kazo ta katse wayar sannan ta shiga wanka......

Tana fitowa takira Ruma a waya ta sheda mata ta dawo , bayan ta shirya cikin doguwar riga ta nufo palor wajen Gogal....

Tana zama suka shiga hira take shedawa Gogal takusa daina koyarwa a Makaran ta , Gogal ta dube ta tace " kin sami mijin aure ne Aysha da zaki daina koyar wa ? Murmushi Aysha tayi sannan tace " ina dai kan hanyar Samu sai ki kuma tayani da addu'a , Sallamar Ruma itace ta katse su daha hirar su , shigowa tayi tasamu guri ta zauna tana gaida Gogal , ta amsa tare da tambayar ta iyayen ta suna lafiya , Ruma tace "lafiya lau suke suna gaidake , hannun Ruma Aysha taja suka tashi suka nufi cikin d'akin Ayshar......

Koda shigar su Ruma ta dubi Aysha tace " zakiyi mamaki jin cewar inason muyi magana dake , Aysha ina da k'awaye sosai da wanda muke Sch d'aya da kuma wanda suke cikin Family d'in mu , amman bantab'a jin soyayyar su araina ba kamar yadda lokaci d'aya naji soyayyarki , tun had'uwar mu naji kin shiga raina sosai tamkar wacce muka fito ciki d'aya , dan Allah Aysha inaso kibani shawara akan Soyayyata da Khalid , tunsan da mukazo gidan nan naku nida shi har yau ban kuma samun kan sa ba , kullum da irin uzirin da yake bani kwata kwata ko kirana bayayi a waya , gashi in nakirashi nan ma sai ya katse yace aikine yayi masa yawa , kuma yau d'in nan da safe Daddy ya tabba tar min da rashin zaman sa sosai a kasuwa , narasa me ke damun Khalid kwata kwata da ya canza lokaci d'aya , hawaye ne suka taru a idanun Ruma ta rik'e hannun Aysha tam taci gaba da magana " wallahi Aysha ina mutuk'ar k'aunar Khalid shiyasa na damu , Aysha tausayin Ruma ne ya rufe ta cikin ranta tace " tabbas na tausayawa Zuciyarki data kamu da Soyayyar wanda yake Gaibu , a fili kuma ta zame hannun Ruma daga nata tana mik'ewa tsaye , juyawa tayi tana kallon mirrow wanda take hango Rumar ta ciki tana

share hawayen ta , a hankali Aysha tace " shawara 'Daya zan iya baki a yanzu itace ki hak'ura da Khalid , kallo ta Ruma tayi sannan tace " meyasa zakice narabu dashi ? Aysha cikin ranta tace " saboda baku dace dashi ba , shi mugune azzalumi ke kuma salaha ce me mutunci wacce tafito daga gidan mutunci , a fili kuma tace " Abinda yasa nace kirabu dashi bawai ina nufin kirabu dashi kidaina kulashi ba a'a inaso kibashi nan da kwana biyu muga yadda za'ayi , indai har cikin kwana biyun nan bai zo wajen ki ba to tabbas Khalid ya canza budurwa sai mu shirya d'amarar k'wato shi , Ruma tayi shuru tana nazarin maganganun Aysha , tabbas Aysha gaskiya tafad'a mata dan Mumyn ta ma sai da tace mata hakan , dan haka cike da gamsuwa ta yarda da shawarar Ayshar ta shirya yin hakan , Aysha ganin ta amince yasa tace " gaskiya Ruma inaso ki rage damuwa dan kin rame sosai , dubi yadda kika fige tamkar wacce tayi jinya , Ruma tayi murmushi sannan tace " wallahi wanda inyi jinya akan yadda zuciyata ke gasuwa , Aysha tayi tsaki sannan tace " wallahi soyayya batayi ba , shiyasa bana d'orawa kaina wannan tension d'in dan bazan iya ba , iya kacina da maza kawai in anshi 'yan canji na inbar su , dan nasan wallahi soyayya b'ata lokaci ne kawai , Ruma ta kalli Aysha tana mamakin kalmar da ta fad'a , a hankali tace " Aysha wai kina nufin kice baki tab'a Soyayya ba ? kuma wanne canji kike karb'a a wajen maza har kika fi fifitashi akan Soyayya ? Aysha tayi murmushi tace " amsar tambayar ki nanan tafe nan bada jimawa ba , dai dai lokacin aka kira sallar Magriba , toilet Aysha ta fad'a tayo arwala tare da shimfid'a sallah ya dan gabatar da sallah , Ruma da yake fashin sallah take shisa bata mik'e ba har Aysha ta idar , duban ta Aysha tayi sannan tace " kizo muje muci abinci dan yunwa nakeji ni , Ruma tace " sai da naci abinci nataho kawai muje kici kirakani hanya zan tafi , Aysha tace " malama muje kawai muci abinci tare , nasan bawani abinci kika ci ba kina wannan damuwar , haka suka fito palor suka samu Gogal ta tashi , kan Dinning Aysha ta kallah aikuwa Gogal gar tagama girki , Ruma tace " gaskiya Aysha bakida murunci nasan girkin nan Mama ce tayi , zama sukayi kan Dinning Aysha na bud'e kular abincin , dambun shinkafa tagani wanda yaji kayan lambu wada tattu sai k'amshi yake , tuni Aysha taja filet ta zuba musu suka fara ci............

[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
(Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 26

Shurun da Aysha tayi ba k'aramin tayar da hankalin Hameed yayi ba , duban ta yayi cike da sallama wa aran sa baza ta soshi ba ko kuma wani ya riga sa , a hankali ya furta " kinyi shuru Aysha plss dan Allah kidaure kice min wani abu wallahi zuciya ta gab take da bugawa , k'wayar idanun sa ta kallah nan ta hango zallar soyayyar ta da k'auna , tabbas dagaske yake yana son ta amman baza tayi saurin yadda dashi ba , dan lokaci da Farouq yazo mata kusan shima da irin wannan salon yazo mata , dan haka haryan zu tarasa yadda ake gano soyayyar gaskiya , duk da idanun Hameed sosai ya fallasa abinda ke cikin zuciyar sa , jikin ta a sanyaye tace masa " inaso kabani lokaci plss komai na yanke zakaji ni , Hameed ya dubi Aysha kamar zaisa kuka yace " inajin kafin lokacin d zaki d'ibar min kibani amsa ta to zaki iyajin zuciya ta ta buga na mutu , dan Allah Aysha ki tausaya min zuciya ta bak'uwa ce a soyayya , akan ki tafara so kuma akan ki zata k'are shi ki tausaya min , Aysha tace " kabani ko zuwa gobe ne sai muyi magana , komai na yanke zakaji kuma kadaina damuwa sosai kar ka rauna ta zuciyar ka , sosai Hameed yaji dad'in kalmar k'arshe da Aysha ta furta masa , bayan sun tab'a hira yayi mata sallama tare da ansar phone number ta......

Hameed na tafiya Khalid yazo ko gida bata shiga ba , yana k'araso wa ya janyo ta jikin sa yana shin shinar ta kamar wani bunsuru , ture sa tayi da k'arfin ta sannan ta shiga magana " haba Khalid a cikin gidan mu fa kake meyasa kake min irin hakan ? yanzu in wani yagan mufa shikenan ka janyo min magana , Murmushi yayi sannan yace " Sorry Babyna kinsan in kina tare dani ji nake kamar ko da yaushe in kasan ce cikin lallausan jikin naki , tab'e baki Aysha tayi sannan tace " ina kayana suke ? Khalid yace " Muje daga motar sai muyi hira daga nan ki d'auko abinki , Aysha samun kanta tayi da jin tsoro batason meyasa bataso Hameed ya ganta tana irin wannan rayuwar ba , a gaskiya baza ta fita tashiga motar Khalid ba gudun kar Hameed yaganta , tunda bai b'oye mata komai ba ya sheda mata a cikin unguwar gidan su yake shima , kallon Khalid tayi sannan tace " bazan iya zance ba yau saboda kaina yana min ciwo , kasan dai yau tunda rana muke tare don haka kayi hak'uri zuwa gobe , Khalid bai so haka ba kwata kwata dan so yayi su shiga motar ko k'irjin ta yasamu yasha zai rage ruwan marar sa da yataru , amman sanin halin Aysha in batason abu to bazatayi ba yasa ya k'yaleta , juyawa yayi ya nufi cikin motar ya d'auko mata ledojin kayan ta , yana kawo mata ta ansa tana fad'in " yakama ta fa kaje wajen Ruma dan tadamu dayawa , Khalid yaja tsaki sannan yace " k'yaleta dan Allah wallahi saboda takurar ta nakashe wayata , Daddyn tama ya kirani nayi masa k'aryar banajin dad'i kwana biyu , Murmushi Aysha tayi sannan tace " yakamata dai ka duba ta ko sau d'ayane , tsaki yaja sannan yace " mezan samu a tare da ita in ba kayan haushi ba , kwata kwata bata wani waye ba kullum kanta a duhu yake , kawai ki share ta zan d'aga wayar ta in ta kira ince mata banjin dadi , Da haka sukayi sallama Aysha ta shige cikin gida abinta , shikuwa

Khalid yana tsaye ya k'urawa Mazaunan ta idanu har tashige abinta Sannan yatafi......

Tunda Aysha ta shiga gida tayi sallah sannan ta kwanta , sai dai ko alamar bacci bataji saboda daman ba baccin takeji ba , tunanin Hameed ne ya dami zuciyar ta dan dagaske ta gano zallar k'aunar ta a k'wayar idanun sa , itama tun sanda ya taimake ta taji acikin zuciyar ta ya kwanta mata , Abinda yasa take share sa sabida tana jin tsoron maza , duba da yadda ko wanne namiji in suka had'u dashi bashi da buri sai ya kusan ce ta da iskan ci , amman zata fallasa masa kanta ta sanar dashi ko wacece ita , in har yaga zai amince mata to in kuma jin hakan zai nisan tasu dama ita bata saka akai ba , da haka tagama tunanin ta tare da d'auko wayar ta ta kunna data , tana hawa Whaspp taga tarin sak'onni daga maza kala kala , haka tashiga duba na dubawa tana share wad'an da basu da amfani ......

Ruma tana komawa gida bayan tayi wanka ko abinci bata kallah ba , dan dambun dataci a gidan su Aysha ya k'osar da ita , Mumyn tace t dube ta tace " wai Ruma ko kun samu sab'ani da Khalid ne naga kwana biyu baya zuwa ? Murmushin takaici Ruma tayi sannan tace " ko d'aya Mumy kawai dai bansan me yake damun sa ba kwana biyun nan , Daddy ma yace ko kasuwa yanzu baya zuwa sosai kuma inna kira sa a waya baya d'agawa , Mumy tayi shuru tana nazari kafin tace " tabbas to akwai wani abun amman kiyi masa test ko zaki samu kiji meke damun sa , Ruma tace to Mumy zanyi masa insha Allah , daga haka ta mik'e tayiwa Mumyn sai da safe ta nufi d'akin ta .....

Tana zuwa ta bud'e data ta hau Whaspp , sak'onni ne suka shiga shigowa saboda dad'ewar datayi bata hau ba , duk wad'an da suka mata magana k'awayen tane sai wata Number guda d'aya wacce bta san taba taga kamar anturo mata pic , kamar zata wuce sai kuma ta fasa ta dawo tashi ga , tana shiga cikin pic d'in k'irjin ta sai da ya buga ganin wanda yake jikin pic d'in , Khalid tagani yana shan Nonon wata budurwa wacce bataga fuskar ta ba , zoom d'in hoton tayi ta k'ara tabbatar da ba gizo ida nun ta keyi mata ba , a hankali ta furta " Khalid dama haka kake ? shiyasa ya guje ta saboda tak'i yarda su kauce hanya , kullum burin Khalid yatab'a jikin ta , takan ce masa yayi hak'uri suzama Mallakin juna har gajiya sai yayi da ita , wato bazai iya hak'ura har lokacin da zasuyi aure ba sai da yaje yana neman mata , hawayen dake gangaro wa a fuskar ta tayi saurin gogewa , tabbas Khalid ba mijin aure bane tunda ya kasance fasik'i , tamkar zata kira Aysha sai kuma ta fasa gudun kar ko tayi barci ta dameta , number da aka turo mata sak'on tashiga kira , sai dai akashe ake ce mata haka tai ta gwadawa amman ana sheda mata tana kashe , number Khalid tashiga kira tana ring amman fir yak'i d'agawa , tabbas ta hak'ura da Khalid koda shine autan maza , kuka sosai Ruma take tanajin tsanar Khalid na ratsa jikin ta , ta yanke wa ranta ba wanda zata sanar wa da abinda tagani , kawai dai baza ta k'ara kula Khalid ba itama ta hak'ura da sonshi koda zai kashe ta , da wannan tunanin Bacci b'arawo yayi gaba da Ruma......

Washe gari Aysha na tashi ta d'auki layin da ta turawa Ruma hoto tasa akan waya , tana shiga whaspp taga alamar Ruma taga sak'on da ta tura mata , murmushi Aysha tayi sannan ta

d'auki layin datake amfani dashi tashiga kiran Ruma , dai dai kokacin Ruma na zaune a cikin d'akin ta na tunani , koda kiran AYSHA yashigo da sauri ta d'aga tana jin wasu zafafan hawaye na zubo mata , murya a sanyaye tace " Yar uwa dafatan kin tashi lafiya ? Aysha tanajin muryar Ruma tasan kuka tasha kuma tasan wannan pic d'in data gani ne zai sa ta kukan , Aysha tace " lafiya lau natashi 'Yar uwa sai dai kuma tunda naji muryar ki nasan 'Yar uwa ta tana cikin damuwa , ina fatan ba akan wannan Guy d'in kike damuwa , plss 'Yar uwa banason kidunga saka damuwa aranki , haka kawai ya saka miku ciwon zuciya yazo ya gudu ya barki , aikuwa Ruma me jiran k'iris tuni tashiga rera kuka tamkar 'yar goye , kukan da Ruma keyi har cikin zuciyar Aysha , dan har ga Allah itama tana k'aunar Ruma , dan haka takeso tayi ta rabata da Khalid ko hankalin ta ya kwanta itama , nan Aysha ta shiga kwantar wa da Ruma hankali har tasamu tayi shuru , duk da Ruma bata shedawa Aysha abinda yasa ta kuka ba , itama kuma bata tambaye ta ba tunda tagane sak'on ta datakeso ta isar ya isa , nan sukayi sallama tare da yi mata alk'awarin itama zatazo gidan nasu gobe , ......

Bayan sungama waya da Aysha Ruma tasake gwada number da aka turo nata pic , ga mamakin ta sai taji number ta shiga ba bata lokaci , sai da ta kusa katsewa sannan aka d'aga tamkar ba'ason magana , Ruma tace "naga sak'on da aka turomin da wannan Number , sai dai inaso in sanar miki ko kad'an ban damu ba , shida ma namiji ai inyayi abu ado ne agaresa kuma hakan bazai tab'a mana soyayyar mu ba , inaso kisani in so kike ki rabamu to ina me tabbatar miki da kinyi kad'an , yanzu nafara son Khalid har sai yazamo mijina , Murmushi taji anyi mata cike da gadara da isa sannan aka furta " haba 'yan mata ki kama bakin ki , ai Khalid ya ruga da yayi miki nisa sai dai ki hangesa , kuma wannan pic din ba komai bane akan abinda muke yi da Khalid , inhar kina so ki tabbatar da waye Khalid to gobe da misalin k'arfe biyar na yamma kizo Taheer gate place hotel zaki abinda zai baki mamaki , kitt aka kashe wayar batare da ta yi magana ba , Ruma sake bin wayar tayi amman sai jitayi har ankashe , badan tanason Khalid tace haka ba kawai tanaso tagane ko shiri ne ko kuma gaske ne , amman lallai gobe sai taje Taheer Hotel taga abinda akeson tagani , dan itama tanaso takama Khalid da hujja wacce zata tabbatar masa da tasan waye shi , .........

*Comment* plss

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 🌹💞💔
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_

*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 29

Tabbas Jabir ya wuce duk tunaninta , Mamakin yadda yasan sirrikan ta tashiga yi , koda yake bazatayi mamaki ba duba da tun farko dama tasan shu'umine sosai , shiyasa tun farko taji jinin ta bai had'u dashi ba amman duk da haka sai bibiyar ta yake , yanzu gashi yana neman janyo mata Gogal tayi fushi da ita , kuma hakan ba k'aramin tashin hankalin ta bane dan ko kad'an batason Gogal tayi fushi da ita , duk duniya bata da kowa sai Gogal itace gatan ta itace duk wani farin cikin ta , da ita tabud'i ido tun tasowar ta dan haka dole ta guji duk wani abunda zai b'ata ranta , gashi Dr. Yace mata tana gab da kamuwa da matsala a kwakwalwar ta , duk da Aysha ta k'udur ta aran ta bazata k'ara aikata zina ba tunda har shirinta na k'arshe yau takeson kammala shi , Amman tuni taci Alwashin tabbas saita koyawa Jabir Hankali dan haka itama zata bibiyesa batare da yasani ba , ......

Wayar tace tashiga ruri ta duba dan ganin me kiran nata , Khalid ne haka ta katse batare da ta d'aga ba , wata tsanar sa ce ke nunkuwa a zuciyar ta duk sakon na duniya , zama tayi a bakin gadon ta tashiga tunanin yadda zata samu wacce zata tura Hotel anjima , tabbas tasan Ruma zataje Hotel d'in dan ko iya wayar da sukayi ya tabbatar mata da hakan , whaspp d'in ta ta bud'e tashiga wani group datake ciki , duk wad'an da suke group d'in *'Yan Hannu ne* dan daga masu yin lez sai masu neman maza , duk da bata magana a group d'in amman sukan biyota Prvt tallata Hajar su , duba Contact d'in su tashiga yi d'aya bayan d'aya , tsayawa tayi a Contact d'in wata tsaleliyar budurwa me suna Leeemah , take Aysha ta kunna data tare da shiga direct Message tace mata Hy , aikuwa taci sa'a Leeemah na kan online tuni ta dawo mata da Reply na Hy My dear you'r welcome , Aysha tace " kozan iya magana dake in babu damuwa ? Leeemah tace " bawata damuwa Uwar ruwa ina jinki , sunan da Aysha ke amfani dashi shine Uwar ruwa , Aysha tace wani aiki nakeso zakimin yaud'in nan inba damuwa ? Leeemah tace "

fad'i komai kikeso kan ki tsaye zanyi miki shi ,  Aysha tace yanzu dai kina wane gari dan inji , Leemah tace "Ina garin Kano unguwar Gadon k'aya ,  Aysha tace " gud inaso kimin wani aiki anjima a Hotel d'in Taheer gate palace , Leemah tace angama Uwar Ruwa  fad'i yadda aikin zai kasance , Nan Aysha ta sheda mata tana so su had'u a Hotel d'in k'arfe hud'u da rabi dai dai , daga nan zatayi mata bayanin yadda zata yi aikin , take Leemah tayi Na'am nan suka gama magana ,  Aysha kafin ta kashe datar ta ta kuma nemo Number Ruma ta tura mata voice d'in muryar Khalid , wanda yake fad'in bason ta yake ba kawai saboda kud'in Mahaifin ta yake kulata , amman da zarar ya aure ta yasamu kud'i to zai auri kalar matar da yakeso , harda yadda yake cutar Mahaifin Rumar a kasuwa batare da yasani ba , duk voice d'in da sukayi sai da Aysha ta turawa Ruma sannan a k'asa ta rubuta " ko zaki iya sheda wannan muryar waye ? daga haka ta kashe datar ta ta sauka gaba d'aya daga kan Whaspp d'in ......

Wajen k'arfe Uku Aysha ta shirya cikin shigar ta ta kamala tafito , d'akin Gogal tashiga tasa meta a zaune tana jan cazbi , durk'usawa Aysha tayi sannan tace " barka da wannan lokacin Gogal ya jikin naki ? ba yabo ba fallasa Gogal tace jiki da sauk'i , Aysha tace "Allah yak'ara miki lafiya da nisan kwana me amfani ,  Gogal bata amsa da Ameen d'in data saba ba tayi shuru , Aysha takuma risinawa tace " ga Abinci can a kan Dinning nadafa miki ni zan wuce makaranta ,  Gogal batare da ta dube ta ba tace " Allah ya kiyaye  Aysha ta mik'e ta fita......

Koda ta fito sai da tagama dube duben ta bataga kowa ba sannan ta kama hanyar fita bakin titi , wayar ta ta ciro tashiga kiran number Leeemah ,  tana d'agawa tace mata gatanan tana shirin fitowa itama , nan Aysha ta kashe wayar sanan ta kira number Khalid , yana d'agawa yace " Sweet yau kwata kwata kin ki bari naji muryarki dayawa , muna fara waya kike katsewa kodai nayi laifine ? murmushi Aysha tayi sannan tace " babu laifin dakayi yau nayi busy ne sosai ,  to Babyna ina fatan baki gaji da yawa ba dan kinsan yau zan danneki dayawa ,  Aysha wani takaici taji ya kamata amman sai ta dake tace " bangaji ba My Baby kasan akan ka zan jure komai ,  Khalid cike da murna yace " dama zakiyiwa Uncle d'inki dabara da munkwana tare mufaran ta ran juna sosai ,  Aysha tace " karka damu zan gwada nagani ko zai barni ,  Khalid har wani shauk'i yake yana ce mata shifa tun yanzu zai shirya dan ya matsu da yawa , itama tace masa yanzu zata shirya taje takama musu d'akin tunda ya turo mata kud'in ,   nan sukayi sallama Aysha tana duban wayar tana murmushin mugunta.....

Ruma wajen k'arfe uku ta d'auki wayar ta tana shiga Whaspp , sak'onni ne suka shiga shigowa cikin wayar a ciki ta kuma ganin number da aka turo mata pic d'in Khalid ,  hannun ta har rawa yake wajen bud'e sak'on taga me suka sake turo mata ,  tana bud'ewa taga Voice guda uku ajere , tuni ta bud'e bayan ta karanta rubutun k'asa ,  Muryar Khalid tashiga ji yana bai yana yadda yake shirya komai ,  jikin ta har tsuma yake tanajin wata iriyar tsanar Khalid , bayan duk tagama ji ta mik'e da saurin ta ta nufi d'akin Mumyn ta ,  tana zuwa ta kunna mata Voice d'in Muryar Khalid itama tashiga ji ,  bayan tagama ji ta kamo mata hotunan da aka turk mata tare da sheda mata ance k'arfe Biyar taje Hotel d'in Taheer taganewa idon ta komai ,  nan Mumyn ta tashiga salati tare da cewa bari takira Daddy ta sanar masa dan suma suje Hotel d'in dan tabbatar wa ,  aikuwa koda suka sanar masa cewa yayi sutaho Hotel d'in su had'u acan dan shima dama yagaji da abinda Khalid d'in keyi masa na rashin zuwa kasuwa , ashe ashe akwai

abinda ya taka shiyasa yake haka , .....

Tuni Ruma da Leeemah sun Bayyana a Hotel d'in Taheer , tana gama kama d'aki ta nemi Number Ruma ta tura mata Room number d'akin , ciki suka shiga nan ta tsarawa Leeemah komai yadda zata tafiyar dashi , basu dad'e da zuwa ba saiga Khalid ya iso sai faman zabga k'amshi yake , akan idanun Ruma da iyayen ta ya fito daga motar batare da yagan suba ya nufi Reception.........

*kumin Comment kuga ruwan Typing*✍🏻😜😝😝
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

*NA*
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 27

Washe gari tunda safe Aysha take shirya yadda Khalid zai shiga hannu , tunowa tayi da jiya yace mata 2m .A account d'in sa kuma sunje shopping ta cinye masa 1m da dubu d'ari uku , ya siya mata gold sark'a da kuma zobuna , yanzu in ta auna cikin Account d'in Khalid saura dubu d'ari Bakwai , dole yanzu zata shirya cinye sauran canjin daya rage masa ,

dan bataso ko canji ta bar masa bare yaji dad'in cutar wasu agaba , tanaso ta maida shi talakan k'arfi da yaji tunda dama motar dayake hawa ta gidan su Ruman ce Yake d'auka , wata dabara ce ta fad'o mata da sauri ta d'auki waya zata kira Khalid , wata Number tagani ana kiranta da ita , da kamar bazata d'aga ba sai kuma wata zuciyar tace d'aga kiji ko waye , d'agawa tayi tare da yin shiru batayi magana ba , daga cikin wayar taji muryar Hameed yana fad'in Assalamu Alaikum , muryar tasa tuni ta ratsa duk wani sassa na jikin ta , idanuwan ta ta lumshe sannan tace " wa'alaikas salam , Hameed wata ajiyar zuciya yaja dan duk a tunaninsa baza ta d'aga wayarsa ba amman sai gashi ta d'aga , My Angel dafatan kin tashi lafiya kuma ina fatan dai ba bacci kike na tashe ki ba ? Murmushi Aysha tayi karo na farko a rayuwar ta dataji 'Da namiji ya burgeta , kuma wannan shine karo na farko da aka tab'a kiran ta tare da tambayar ta tashi lafiya , duk Namijin da zai kira ta sai dai yace mata A inah zasu had'u ko kuma yana Hotel kaza tazo tasa mesa , baruwan su da tambayar lafiyar ta su dai kawai burunsu tazo su aikata Fasik'an ci , karo na biyu dataji ta tsani zina dan bata da wata riba sai dai k'arshe ma ka had'u da tarin dana sani , a hankali ta furta masa " natashi lafiya kaima ina fatan hakan daga gareka , Murmushi Hameed yayi har Aysha najiyo sautin yace " lafiya lau nima natashi sai dai zuciya ta datake d'auke da farga da tarin k'alubale , Aysha ta d'an fito da ido a tsorace tamkar yana gaban ta tace " wanne irin Fargaba da k'alu bale kuma ? murmushi yayi sannan yace " Zuciya ta tana jiran amsar da zata samu daga gareki kinga kuwa dole na kasance cikin fargaba , Murmushi tayi sannan tace " kar kadamu komai zai zo da sauki kawai dai kajira lokacin yayi , Hameed yace " lokaci ya kusa tunda zuwa anjima zanji komai dan haka yau kisa aranki kina da mara lafiya mai buk'atar tallafin ki , murmushi ta kuma yi tace " sai najika ta kashe wayar batare da tajira yace mata wani abun ba , kallon wayar tayi tamkar me gano Hameed d'in aciki tace " in na biye masa sai yaja zancen da hira har nazo na furta abinda zuciya ta bata yanke ba , .......

Number Khalid ta nemo sannan ta shiga kiran sa , sai dai har ta katse bai d'auka ba ko baya kusa da wayar ko kuma yana bacci , ajiye wayar tayi sannan tafito palor dan ganin ko Gogal ta fito , bata gan ta ba hakan yasa ta shiga kitchen ta hau girka musu abinda zasuyi kari dashi , Kunun gyad'a ta dama tare da soya musu dankalin turawa , tana gamawa ta d'auko ta ajiye akan dinning sanna ta d'auki na Habu ta mik'a masa , koda ta shigo cikin d'akin ta ta koma sannan ta fad'a wanka toilet , tana fito tasaka wasu riga da wando pakistan , rigar takawo mata har gwiwa wandon kuma daga k'asa n sa ya d'an tsuke amman kayan sosai sunyi mata kyau , wani hijab d'an k'arami iya kafad'a ta d'auka ta zura tare da fito wajen Dinning , Ganin Gogal tayi a zaune itama tana shan Kunun gyadar , tana zuwa ta gaida ta sannan tace " ai tund'azu na fito naga baki fito ba , Gogal tace " natashi ne jikin nawa babu dad'i shiyasa , amman yanzu naji sauk'i tunda gashi nafito ina karyawa , Aysha tace " kwana biyu ma ai bakizo munje ganin likita ba , bari mugama karyawa yanzu sai muje kiga likita dan ciwo tun yana k'arami ake tarar sa , Gogal batayi musu ba dan tanason ganin likitan itama , Bayan sun kammala Gogal ta mik'e zatayi wanka ta shirya su tafi , Aysha kuma ta shigs d'akin ta ta kuma gyara jikin ta tare da feso turare sannan ta fito , zama tayi a palor jiran fitowar Gogal......

wayar ta ce ta shiga Ring ta d'auka dan ganin waye me kiran nata , Khalid tagani tayi murmushin mugunta tare da d'agawa cike da kissa , Hy Babyna kankana uwar ruwa kinsan har mafarkin ki nayi wallahi jiyan nan kin bani dad'i , kusan sumar dani kikai fa gaskiya ina

kwad'ayin ki yauma ki daure muhad'u , Aysha tayi wani murmushin mugunta sannan tace " kar ka damu ai ni takace kuma kaima nawa ne komai kakeso zanyi maka , in ban faranta ranka ba ran wazan faran ta My Dear ,, wani dad'ine ya kama Khalid tare da wani shauk'i , tabbas bazai yi gangancin rabuwa da Aysha ba saboda ta ko'ina tagama had'uwa , katse masa tunani tayi dacewa Babyna inason kamin wata alfarma  dan nasan nafi k'arfin komai agurinka ,  Khalid yace " inajinki Babyna fad'i kome kikeso indai ina dashi to zanbaki ,  Aysha tace " Wata Auntyna ce tayi order kaya shine aka rik'e mata , yanzu haka sunce mata indai zasu sakar mata kaya to dole sai ta turo musu da kud'i  dubu d'ari shida da Hamsin ,  kuma kwata kwata kud'add'en hannun ta basu kai hakan ba , shine tamin magana akan in nemo mata dan Allah zuwa lokacin da zasu sakar mata kayan nata , Kayan 10M. tayi order da zarar ansakar mata kayan zata baka kud'in ,  Khalid yayi d'an dum sannan yace " Babyna kinsan kwata kwata kud'in Account d'ina yanzu saura dubu d'ari Bakwai , dama jiya na fad'a miki ko nawa ne aciki kuma kinga kinyi siyayya a ciki ,  amman bakomai ai nima Auntyna  kuma banaso ace Babyna tana damuwa , dan nasan indai ban baki ba wani zaki ce saki tambaya nikuma ina kishin hakan , nan Aysha tashiga yiwa Khalid godiya tare da masa dad'in baki  , tuni ya shagalce yaji ko 20M. Ta tambaya zai bata tunda ta wuce haka a gunsa , dan shi yagama tsaida magana ita zai aura tunda ga yadda ta sarrafashi jiya ta gama dashi , yayi sex da mata da yawa amman ba wacce ta iya sarrafashi tamkar Aysha , gata Allah yayi mata baiwar ni'imah tamkar k'orama , a kasalan ce yace " Babyna ki turomim account d'in da zan sa kud'in , Aysha ta amsa masa da zata turo sannan tace " kawai ka turomin dubu d'ari Bakwai d'in sai in ciri dubu Hamsin d'in naje nakama mana Hotel anjima , aikuwa ba musu Khalid na rawar jiki ya turawa Aysha duka dubu d'ari bakwai d'in ,  koda Aysha taji kud'in sun shigo tayi wani murmushi sannan tace " taka ta k'are Khalid sai wani kokacin , Aysha bazaka sake ganin koda tafukan hannun ta ba bare yakai ka da ganin jikin ta ,   tasan yanzu bashi da ko ficika a account kuma yau zai zama tarihi a gidan su Ruma , ....

Gogal ce ta fito suka fice harabar gidan , motar Aysha tashiga tare da bud'ewa Gogal  , Gogal da k'yar ta yadda ta shiga saboda cewa tayi Aysha bata iya motar ba zataje ta yar da ita , Habu yana dariya yace " aikuwa ta iya sosai Gogal kishiga kawai Allah ya tsare sai kun dawo , Da Ameen Gogal ta amsa tana shiga  sannan tace " kijanina hankali nidai , .........

Sorry kuyi hakuri😰😰
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR  HANNU*
🥴🥴

_NA_
*Zee MD*

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 30

Yana shiga ya kira number Aysha , tana d'agawa ya tambaye ta Room number d'akin datake , nan ta fad'a masa ya kashe wayar ya nufi d'akin....

Tuni Aysha tashiga toilet yayin da Leeemah ita kuma ta haye gado tana lulleb'e jikin ta da bargo , Khalid yana zuwa ya tura k'ofah dan ta sheda masa k'ofah a bud'e take kawai yashigo , koda ya shiga ganin Aysha akan gado kawai yafara cewa " wato Babyna har kingama shiryawa ni kike jira ko ? da k'yar Leemah ta 'iya kwai kwayon muryar Aysha tace " haba Dear kawai kataho nima a duk na zak'u kai kawai nake jira , dayake kanta na cikin bargo shiyasa baidamu da canjin dayaji muryar ta tayi ba , tuni yahau cire kayan jikin tare da fad'in "Babyna ko tayin cire kaya babu kin wani shige bargo , hayewa gadon shima yayi tare da shigewa cikin bargon , dai dai lokacin su Ruma da iyayen ta suka banko k'ofar cikin d'akin , dayake ya manta bai rufo shiyasa suka sameta a bud'e , shima kuma adai dai lokacin yaga fuskar Leeemah yabud'e bargon cikin furgici , aikuwa idanun suka had'a da Alhaji Ashir da Mumyn Ruma da ita kanta Ruman , da sauri Khalid ya rintsa idanu yana jiran yaga wai ko mafarki yake , sai dai jin Muryar Alhaji Ashir ya tabbatar masa da ba mafarki yake ba idanun sa biyu , Alhaji Ashir yace " Nagode wa Allah daya nunamin halinka tunkafin na had'a zuria dakai , duk cin amanar da kake shirin yimin kuma naji komai , azzalumi macuci duk kud'adena dakasan ka d'iba kadawo min dasu , nabaka nan da awa 24 in bahaka ba zansa a kullemin kai , samnan Mota ta dakake yawo kana dibar matan bariki kuna yawon banza kabani mukullin abata na wuce da ita , Ruma ta kallesa da mugun kallo tace " Mayaudari Munafiki Allah ya tsareni daga tarkon ka ta sanadin Karuwar ka , ta kalli Leeemah tace " nagode miki da yadda kika farkar dani daga baccin danake , kika cireni daga duhu zuwa haske kika rabani da auran Fasiki Macuci , ina miki fatan shiriya daga wannan rayuwar da kika saka kanki kema , tana kaiwa nan ta fice daga cikin d'akin tana jin wani abu me zafi a k'irjin ta , tabbas Khalid ya cuceta da ya dasa mata son shi aranta , tasan kafin fitarsa dole sai tasha wuya ,....

Alhaji Ashir ya nufi kan dirowar gado ya d'auki mukullin motar sa ya fice daga d'akin , dama Mumy tunda Ruma ta fita itama tabi bayan ta suka fice dukan su daga d'akin.......

Khalid kallon sa ya maido kan Leeemah yace " dan Ubanki wace ce ke ? tuni ya fito daga cikin bargo yana neman abinda zai doki Leeemah dashi , da sauri Aysha ta fito daga toilet tana fad'in " dakata Khalid karka kuskura kadake ta , jiyowa yayi yana duban Aysha sai sannan yafara tunanin duk makircin tane itace ta had'a masa wannan shirin , kallon ta yashiga yi tare dajin wata tsanar ta aransa , Cikin kakkausar murya ya furta " menayi miki kika sakamin da irin wannan abun ? kin tozartani a idanun sirikaina sannan kin zubarmin da mutunci , inaso ki fad'amin dalilin ki nayi min wannan tozarcin haka , wani shu'umin Murmushi Aysha tayi sannan ta zauna a gefen hannun kujera tace " Khalid kenan Manyan gari , Inaso kasani Nice Ayshar Gogal wacce ka lalatani , kaine namijin da yafara ketamin mutuncina , ka Yaudareni ka wulak'antani sannan daga k'arshe ka gujeni , ta sanadin abinda kamin yasa nazama *'Yar Hannu*, tundaga lokacin jikina yazama abin hutawa ga Maza masu hali irin naka , sai dai duk iskancina inayin sane akan taku , na dad'e ina jiran wannan ranar da zatazo ace gashi kazo hannuna amman ban samu ba sai yau , kad'auka kaci bulus ko ? ka d'auka Ayshar da ka lalata bata duniya ma ko ? to kasani na rok'i Allah yakawoni wannan ranar da zan d'au fansa akan ka , kuma daga rana irin ta yau natashi daga sunan *'Yar Hannu* nakoma Asalin sunana Sayyada Aysha , wata zufa ce ta karyowa Khalid jin Ayshar Gogal ce wacce yayiwa Fyad'e har tasamu ciki tazo masa da maganar cikin ya koreta , To ya akayi yakasa gane itace ? taya tazama wata hamshak'iyar mace haka ? wannan gidan datake to gidan waye sanin da yayi musu basu da kowa kuma basu da komai , to gidan waye wannan d'in datake a cikin sa ? kuma ina Gogal tabbas yasan ya aikata wa Aysha ba dai dai ba dole hakkin ta ya bibiyesa......

[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 28

Tunda suka fara tafiya Aysha ta kunna karatun Alk'ur'ani me girma , sabanin indai ita kad'ai zata fita sai dai tasa Music tana ji , a haka har suka k'araso Cikin Asibitin , samun waje Aysha tayi ta faka motar sannan suka suka fito ita da Gogal suna takawa har cikin harabar zaman masu ganin likita , wajen bud'e files Aysha taje tagama biyan kud'i sannan tadawo su ka zauna suna jiran kiran Dr. ....

Ba'afi Minty 5 ba aka kirasu suka shiga ciki , Bayan tambayoyin da Dr yayi wa Gogal akan yadda takejin jikin nata tashiga bashi bayani yana rubutawa , nan ya shiga baya shawarwari game da yadda zata kula da jikin ta , ya sheda mata hawan jini gare ta kuma yana neman tab'a mata kwakwal wa mutukar bata daina saka damuuwa aran ta ba , Aysha ta dubi likita sannan ta dubi Gogal tace " tunanin me kikeyi haka da har yake neman rikita kwakwal warki ? dan Allah Gogal kirage saka damuwa aranki duk duniya kinsan bani da kowa in bake ba , kema kina so narasaki ne ? Gogal tayi murmushi sannan tace " Aysha mutuk'ar bakiyi aure ba to tabbas bazan daina damuwa ba , Aysha tace " Aure lokaci ne Gogal indai lokacin yi yazo ko nashirya ko ban shirya ba to tabbas zanyi , nidai kici gaba da yimin addu'a Allah yazab'amin miji nagari , Dr yayi murmushi yana duban su dan sun burgeshi sosai , nan yace da gaskiyar Hajiya gaskiya yakamata ace k'anwata kin yi auren nan dan Hajiya tasamu farin ciki , Aysha tayi murmushi tana cewa " zanyi lokaci Dr . Nan suka mik'e yabasu kati tare da ce ma Aysha lallai su siyi magun gunan ta dunga sha , ....

Bayan fitowar su Aysha ta shiga wajen sai da magunguna ta siyo samnan ta fito , tana fitowa suka nufi wajen da motar su take zasu shiga , kamar daga sama Aysha taji ana k'wala mata kira " Aysha Uwar ruwa kankana uwar dad'i daga ina zuwa ina ? cak Aysha ta tsaya wata zufa tana karyo mata , Gogal itama juyowa tayi tana kallon wanda yake kiran Ayshar da wannan sunan , Jabir ne a tsaye ya hard'e hannun sa a kan k'irjin sa yana zuba mata wani murmushi tare da shu'umin kallo , Aysha tayi ta maza ta dake tana d'auke kai tamkar bata gansa ba , murfin motar ta ta bud'e tare da cewa Gogal " shigo mutafi Gogal kinga ana rana kar ta dameki da yawa , Gogal tace " waye wannan d'in ? kuma wanne suna naji yana kiranki dashi haka ? Aysha tace " anya dani yake kuwa dan ni bantab'a ganin saba ma sai yau , sai dai ko nayi masa kama da wata wacce yasani ne , Jabir yayi wani shu'umin murmushi yace " Hajiya barka da wannan lokacin ya gida , Gogal tadubesa sannan tace " lafiya lau amman yaro inaso insan kai waye kuma meye had'in ka da jikata naji ka kirata da wani banzan suna ? Murmushi Jabir yayi sannan yace " ki tambayeta zakiji komai daga bakin ta nabarku Ify , yana gama kaiwa nan ya dubi Aysha ya kashe mata ido tare da barin wajen , Aysha jitayi tamkar tabi bayan Jabir ta rufesa da duka saboda abinda yayi mata , Gogal zubawa Aysha idanu tayi tana mata kallon tuhuma tabbas akwai abinda Aysha keyi wanda bataso tasani , in ba haka ba taya zai kirata da irin wannan sunan haka , Aysha duk jikin ta yayi sanyi ganin irin kallon da Gogal keyi mata ,

Gogal xagayawa tayi ta shiga motar yayin da Aysha ta d'an tsaya tana nazarin yadda zata kare kanta a wajen Gogal , a haka ta shiga motar taja su suka bar harabar asibitin.......

Tunda suka taho har yanzu Gogal batayi magana ba kuma bata kalli inda Aysha ke tuk'i ba , Aysha cikin ranta sai tsinewa Jabir take da irin abinda yayi mata , a haka suka k'araso cikin gidan Gogal ta fice daga motar tashige cikin gidan abinta , Habu sai sannu da zuwa yake masu amman ko kallon sa Gogal batayi ba ta shige , zama Aysha tayi a cikin motar ta tana jin tamkar kar tashiga cikin gidan , me zata cewa Gogal ta kare kanta ta nuna mata batasan Jabir d'in ba , ta dad'e a zaune a cikin motar kafin ta fito tashiga cikin gidan gwuwa a sab'ule , ...

Tunda Gogal ta shiga cikin gidan take zagaye palor gidan , tabbas dole akwai abinda Aysha ke b'oye mata , ita kanta akwai wani abun in Aysha tayi sai tashiga mamakin Ayshar , tana tsaye a hakan Ayshar tayi sallama ta shigo cikin palor , k'arasawa Aysha tayi kusa da ita tana cewa " dan Allah Gogal karki saka abun nan aranki kinajin abinda likita yace miki , wani kallo Gogal tayi mata sannnan tace " inhar kinaso in yarda dake to lallai inason sanin gaskiyar komai , Aysha cikin zuciyar ta ta furta " bazan iya gaya miki gaskiyar komai yanzu ba , amman nasan wata rana sai kinsani duk b'oye b'oye na , a fili kuma ta furta " iya gaskiya ta nafad'a miki wallahi bansan shi ba ban kuma tab'a ganin sa ba , ranar nan ma dana dawo daga makaranta akwai wasu mata da nahad'u dasu a hanya suma sunkirani da irin sunan da wannan d'in ya kirani dashi , dana tsaya a wajen su nace bani bace suna kallona suka yarda , sai dai sunce min akwai wata 'Yar uwar su wai muna kama da ita sosai in dai aka gan mu to tabbas za'ace 'yan biyu ne , kuma suka tambayeni suna na na sheda musu nan ma sukace sunan mu d'aya da ita , Aysha data kalli Gogal ta gefen ido ta ga yadda maganar ta shigeta tuni tayi k'asa da gwuwowin ta taci gaba da magana muryar ta na rawa tace " bana b'oye miki komai Gogal kinsani , dan Allah kar zuciyar ki tafara rawa akaina ki yarda da Ayshar ki bazata tab'a aikata wani abu wanda zai saka zuciyar ki tayi rawa akanta , tuni jikin Gogal yayi sanyi tasamu waje ta zauna tana kallon Ayshar , sai dai har yanzu zuciyar ta takasa yardar mata abinda Ayshar tace , nisawa tayi sannan tace " shikenan na yarda Allah ya kyauta , cikin zuciyar ta ta k'udurce lallai yanzu dole tasa ido sosai akan Aysha shine kawai zai tabbatar mata da gaskiyar abinda Ayshar tace , Aysha ta d'auko jakar ta ta zuge tare da d'auko magungunan Gogal tana fad'in " bari na d'auko miki ruwa kisha magungunan yanzu saboda yanayin jikin naki , Gogal tace " barshi kawai zan shiga d'aki na kwanta zansha kafin na kwanta d'in , tana fad'in haka ta mik'e tashige d'akinta.......

Aysha tabi bayan ta da kallo har ta shige , mik'ewa tayi tashiga cikin d'akin ta da sauri tana rufo k'ofah sannan ta d'auko wayar ta tashiga laluben number Jabir , dama ita tana da number sa shine dai bashi da ta ta , aikuwa tana kira number tashiga sai da ta kusa katsewa sannan ya d'aga , Aysha cike da jin zafin sa tace " me kake nema dani ne mai nayi maka da kake bibiya ta kakeso kasa Kaka ta cikin tashin hankali ? Jabir tunda tafara magana yagane wace yafara wani shu'umin murmushi , sai data gama sannan yace " Hajiya Aysha kenan ashe kina gari daman , aini na d'auka ko kina wata k'asar saboda yadda kika samu duniya , wata tsawa ta

daka masa sannan tace " ina so kafad'amin meye damuwar ka dani da kake bibiyar rayuwata ? Jabir yace " Aysha ina bibiyar ki ne dan inasonki kuma inaso ki shiryu kidaina abinda kike , sai dai kashh kinkasa bani dama ko sau d'aya inyi magana dake , kuma koda yaushe cikin shigar dani kike saboda kin maidani wani wawa , Abinda yasa nayi miki haka kuma saboda ta hakan ne kawai nasan zaki nemeni muyi magana , kuma gashi hasashena ya gayamin gaskiya , Aysha meyasa kika zab'i ki ringa shiga rigar mutunci kina aikata fasik'an ci ? kuma abin haushin duk abinda kike har yanzu kakar ki takasa ganewa , nikuma abinda nakeso shine ki tagane wace ke ko zaisa ki gyara halinki , Aysha a fusace tace " meye damuwar ka da shiryuwata da rashin ta ? kai uba nane ko wani nawa da zaka shiga rayuwa ta ? inaso kasani wallahi mutuk'ar baka rabh dani ba indai na juyo kanka bazaka ji da dad'i ba , Jabir yace zakimin yadda kikayiwa Farouq ne da Mahaifinsa ko ? take k'irjin Aysha ya buga cikin zuciyar ta tace " wannan kodai ba mutum bane taya yake sanin komai nawa ? katse mata tunani yayi da cewa " kina mamaki da yadda nasan komai naki ko ? to kamar yadda kika iya taku nima haka nake nawa , nabarki Ify ki k'ara shiri My Aysha naki Jabir d'an sa idon ki , tuni yakashe wayar yabar Aysha da waya rik'e a hannu tayi tsaye cak.......

*Comment* plss🥰🌹
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 32

A b'angaren Hameed kuwa duk wata damuwar sa yanzu ta ragu , farga bar sa guda d'ayace Akan Aysha Ko zata amince masa ? ranar duk wani iri yake jin sa Allah Allah yake dare yayi yaje yaji me zata ce masa , Hajiyar sa sai tambayar sa take meke damun sa amman sai yace mata bakomai , ko abinci kasa ci yayi ranar haka ya yini cikin d'akin sa , sai wajen magriba yayi wanka ya shirya sannan ya fito.......

Ana idar da sallar Magriba Hameed yanufi gidan su Aysha , sai dai me yana zuwa yasamu gidan a rufe da kwad'o, wata fad'uwar gaba yaji ta ziyarce sa cikin zuciyar sa yashiga cewa " haba Aysha meyasa zaki yimin haka ? nasan saboda ni kika kuma tashi daga wannan gidan , da kin san baki da amsar da zaki bani da kin cemin inyi hak'uri bakya sona , tuni idanun Hameed sukayi jawur saboda takaicin ganin gidan a rufe , ya dad'e a tsaye a k'ofar gidan yana kai kawo har yagaji ya juya ya nufi gida , sai dai yana zuwa k'ofar gida ya tsaya ya kasa shiga yana nazari , wata zuciyar tace masa " kodai kaje tsohuwar unguwar su ko nan sukaje ? tunda yasan dai ba tashi sukayi ba , haka ya shiga gida ya fito da motar ya nufi unguwar su Aysha ta da......

Aysha tana zaune cikin motar har aka idar da sallar Magriba , tuni tagama yankewa kanta zata shiga cikin gidan tayiwa Gogal bayanai koda zata kashe ta , tasan duk duniya bata da kamar ta kuma bazata iya guduwa tabar ta ba , haka ta fito daga cikin motar tanufi cikin gidan.....

Gogal tun sanda taje Makarantar su Aysha ta buk'aci son ganin Shugaban Makaranta , koda suka shiga office suka gaisa dan yasan Gogal sosai , nan take tambayar sa Ya k'ok'ari da hidima sannan ta fara masa godiyar irin Kyautar da Aysha tasamu , shuru yayi yana nazari kafin yace " ban fahimci abinda kike nufi ba , nan tashiga ce masa kyautar gida da Aysha tasamu da kuma motar har ana shirin bata kujerar saudiya , nan Shugaban Makaran ta yashiga jimami da jinjina maganar ta , andad'e ana kawo masa zancen Aysha tana yawon banza kwata kwata bai mai da hankalin sa akan hakan ba , yasan Aysha ta dad'e bata zuwa makaran ta amman inda yayi kuskure shine bai je yasamu Gogal da maganar ba , nan ya shedawa Gogal komai nagame da halayen Aysha , kuma yace baisan zancen gida da motar ba , dan yafi shekara d'aya da rabi rabon da yaga Aysha tazo makaranta , koda Gogal taji maganar shugaban Makaranta tuni jikin ta ya d'auki rawa , take ta yi masa sallama suka nufo gida ita da Habu........

Bayan ta kwaso kayan ta ta sheda wa Habu shima ya kwaso nasa kayan , nan suka nufo tsohon gida suka bud'e tare da taimakon Habu suka gyara gidan , tunda Gogal ta shiga cikin gida tashiga d'akin ta na da ta kwanta saboda zazzab'in da ke barazanar rufe ta , hawaye ne yashiga zubowa ta idanun Gogal cikin zuciyar ta tashiga cewa " tabbas Aysha kin cuceni kin cuci rayuwar mu , menene wanda kika nema kika rasa da kika zab'i irin wannan Rayuwar ? tamkar wacce Aysha ke gaban ta tadunga fad'in " wanne irin fad'i tashine banyi ba dan ganin

rayuwar ki tasamu nagarta , wata zuciyar tace " kina da laifi kema taya zaki dunga ganin ta tana kashe kud'i amman kiyi shuru , haka dai Gogal ta shiga zancen zuci tare da ambaton istigifari dan neman tuba akan sakaci datayi har Aysha tazama haka , jira take taga Ayshar zata biyota nan gidan ko kuma bazata biyota ba ? kuma in tazo me zata ce mata wacce k'aryar zata kuma yi mata a karo na biyu.....

Aysha tana shiga cikin soron gidan tafara sallama a hankali , muryar ta har rawa take tana k'ara yin sallamar , jin ba'a amsa mata ba yasa tashiga tsakar gidan da duhu yafara mamayewa , haka ta nufi cikin d'akin Gogal d'in wanda ta taga shi kad'aine a bud'e , nan ma sallama tayi tana me raba idanuwa dan ta hango inda Gogal d'in take , da k'yar ta hangota a kan sallaya tayi jigum tamkar wacce ma bata motsi , cikin sanyi murya Aysha ta furta Subhanallah , daga bakin k'ofah ta tsaya tare da zubewa kan gwuiwowin ta tana sharar Hawaye , Sunfi Minty 5 a haka kafin Gogal tafara magana " Aysha meyasa kika zab'i wannan bak'ar rayuwar ? Meyasa kika canza halayyarki da nasanki tun asali da ita ? Aysha kin cuceni da kika maida rayuwar ki a banza , kin zab'i siyar da mutuncin ki akan son kud'i da kuma kyale k'yalen duniya , kin ci Amanata a matsayina na wacce nazamar miki uwa da uba , duk da ina da laifi nayin sakaci har kika zama cikakkiyar *'Yar Hannu* , nakasa saka idanuwa akanki nakasa bibiyar yadda kike mu'amala da kud'i , nabi son zuciya na dunga d'ora miki wasu nauyikan namu , bandamu da irin kud'in da kike samu ba bandamu da irin yadda kike siyo mana kayan Abinci ba , duk da kin yi min k'aryar cewa koyarwa kike a Makaran ta ake biyanki , amman ban bibiya na tabbatar da gaskiya ne ko kuma ba gaskiya ba , hawayen dake zuba a fuskar ta ta goge kuma dai dai lokacin 'yan nefa suka kawo wuta , Aysha idanun ta akan Gogal itama sai zubda hawaye take tanajin wata iriyar nadama na shigar ta , tabbas tayi nadama da irin rayuwar da ta jefa kanta a ciki , kawai shashshekar kukan su ce ke tashi a cikin d'akin , Gogal ta dube ta tace inaso a karo na biyu kifad'amin gaskiyar abinda yasa kika zab'i irin wannan rayuwar , kuma wallahi in har kika kuma yimin k'arya wlh bazan yafe miki ba , nan Aysha tasa kuka tare da duban Gogal tace " zanfad'a miki wallahi amman dan Allah karki tsaneni kuma karki koreni wlh bazan iya rayuwa ba mutuk'ar bana tare dake , runtse ido Gogal tayi cike da tsawa tace " kifad'amin inajinki ,.......

Aysha tuni tashiga bawa Gogal labarin yadda akayi tafara bin maza , tunda ga kan Fyad'en da Khalid yayi mata da kuma cikin da yashiga har ta zubar dashi da yadda Farouq yayi mata shima , duk irin mazan da ta kula da kuma irin yadda take yi inzataje gun su bata b'oyewa Gogal ba sai data gaya mata , .....

Gogal tuni tayi mutuwar zaune dan take tafara nuna Aysha da d'an yatsa tana k'ok'arin yin magana , wani tarine ya turnik'e ta ta dafe k'irjin ta sannan ta daina motsi , da gudu Aysha ta nufeta tana k'wallah k'ara " dan Allah Gogal ki yafemin wallahi natuba nadaina komai , rumgumo Gogal tayi ajikin ta wacce taji kamar bata motsi , da gudu ta ajiyeta ta fito tana neman ruwa ta yayyafa mata , dayake a rud'e take kawai waje ta nufa tana kuka tare da neman taimako , dai dai nan Hameed ya iso a motar sa yana ganin Aysha ta fito ko mayafi yasan ba lafiya ba , ko tsayawa baiyi kashe motar ba ya fito da gudu ya nufota yana cewa " lafiya Aysha meyafaru ? da sauri ta rik'o hannun sa tana fad'in " kataimaka min dan Allah kar Gogal ta Mutu

bazan iya zama a duniya ba indai babu ita ,  haka suka shiga cikin gidan a rud'e dan shima ganin ta haka ba k'aramar rud'ewa yayi ba , ...

Koda yaga Gogal a shimfid'e tuni ya sab'eta a kafad'a yana cewa Aysha zo muje asibiti , tuni suka fito ta janyo hijab d'in ta suka fito  tare , karo sukaci da Habu shima ya rufa musu baya akasa Gogal a motar Hameed suka nufi Asibiti.......
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

*Alhamdulillah !*
*Alhamdulillah !!*
*Alhamdulillah !!!*

_Page._   35

Jikin Gogal itama sanyi yayi tare da jin tausayin Aysha , ba komai ne yayi tasiri a zuciyar Gogal ba yasa har tayi nadama sai Sakacin datake gani tayi akan kula da Ayshar , itakuma Aysha ba komai ne ya janyo mata haka ba face Rashin yadda da kaddara  , da tunfarko ta yi hak'uri da Abinda Khalid yayi mata da bata zama haka ba , duk da bayan Khalid ya yi mata hakan kuma taso wannan yazama farko yazama k'arshe amman sai ga Farouq ya billo mata

shima , a haka zuciyar ta tashiga zugata akan cewar duk Namiji inyazo gunta to tabbas ba soyayyar Allah yake mata ba sai dan surar jikin ta , tunda ganan tashiga bin zuciyar ta meyi mata wannan hud'ubar , Allah yarabamu da sharrin Zuciya Ameen......

Gari nayi haske saiga Habu da kaya a hannun sa ya shigo d'akin d'auke da sallama , samun Gogal da yayi a zaune ba k'aramin dad'i yaji ba , dan yanajin tamkar Mahaifiyar sa saboda gatan da ta nuna masa , nan suka gaisa tare da yi mata fatan samun lafiya me d'orewa , ....

Kunu ya taho mata dashi tare da k'osai sai kuma kayan sawa kala biyu , sosai Gogal taji dad'in ganin kunun tayi masa godiya tare da sanya masa albarka , Aysha tayi murmushi tace " shine ni baka tahomin da waina me k'uli ba kawai ta Kakar ka kake ko ? inda sabo Aysha da Habu sun saba tsokanar juna shiyasa Gogal tayi murmushi kawai batare da tace komai ba......

Dr. Hameed ne ya shigo cikin d'akin d'auke da sallama , amsawa Habu yayi tare da yi masa sannu da shigowa , ganin yadda Aysha ke zaune tana bawa Gogal kunu tana sha cike da kulawa , wani dad'i Hameed yaji ya ratsa shi dan da alama Gogal tadaina fushi da Ayshar , cike da girma mawa yagaida Gogal tare da tambayar jikin ta , amsawa tayi cike da sakin fuska sannan tashiga masa godiyar kulawar da yake bata , Hameed murmushi yayi yana satar kallon Aysha wacce ta kauda kanta gefe tamkar bata gansa ba ......

Gogal ce tace " Sayyada baki gaida Dr ta ba kiyi masa godiya yana da mutunci , Aysha ta jiyo ta gaida Hameed amsawa yayi shima yana me d'aure fuska tamkar bashi ba , Aysha bata damu ba dan tasan dama dole Hameed zai tsaneta dan irin rayuwar datayi , Habu ne ya mik'e tare da cewa bari yaje yadawo .....

Yana fita Hameed yace " Mama inaso dan Allah kidaina saka damuwa aranki , zuciyar ki zata iya samun matsala a zo ana wani zancen ba wannan ba , Gogal tace " insha Allah zan kiyaye daga yau nadaina saka komai arai , Cikin zuciyar Gogal kuwa tace " bazan daina damuwa ba mutuk'ar ba Aysha tayi aure ba , amman indai tana gaba na to zan kasan ce cikin damuwa , a fili kuma tashiga cewa Hameed " yau zaku bani sallama ko ? Hameed yayi murmushi sannan yace " kibari sai nan da kwana biyu jikin naki ya kumayin kyau , Gogal tace " banason zaman asibiti indai ba dole ba kuma jaga ai jikina yayi sauk'i sosai , Hameed yace k'a'idar asibitin sa baya sallama akwana d'aya , dan haka tayi hak'uri zuwa gobe , badan taso ba tace shikenan da yau da goben duk d'ayane , Aysha ita kanta so take a sallamesu dan kawai ji tayi batason zama a inda Hameed d'in yake , wata kunyar sa takeji tare da nauyin sa sannan yadda yake had'e mata rai sai take ganin tamkar tsanar ta yayi , ......

Wata Nurse ce tayi sallama cikin d'akin d'auke da Basket food a hannu , rissinawa tayi tagaida Gogal tare da mik'awa Habeeb kwandon tace " gashi inji direban gidan ku yace abaka , ansa yayi batare da yace mata komai ba ita kuma ta fice....

Hameed ya dubi Aysha yace " ungo wannan ki d'ibar muku kuci sannan ki zubomin nawa ki kawomin office , yana fad'in haka ya mik'e ya fita tare da cewa Gogal anjima zaidawo suyi hira.....

Aysha bata tab'a kayan Abincin ba ta share tamkar bataji abinda yace mata ba kafin ya fita , itama Gogal ba yunwa takeji ba sai dai kawai saboda Dr d'in , duban Aysha tayi tace " kiziba masa abincin ki kai masa mana , Aysha ba musu tashiga bud'e kulolin Abincin , farfesun kaji ne sai kuma farfesun kayan ciki daban , sai Shinkafa da miyar ganye wacce taji kifi wadatacce , sai kuma kunun gyada a cikin wani karamin flast , d'aukar filet tayi sannan ta dubi Gogal tace " nifah bansan wanda zan zuba masa ba , Gogal tace "kawai ki d'auki kwandon Abincin kije office d'in nasa sai kitambaye shi abinda yakeso aciki , Aysha badan taso ba ta mik'e ta d'auki kwandon tafita ta nufi office d'in Hameed......

Tana shiga tayi sallama a hankali ta tsaya , Hameed yaji sallamar amman sai yayi kamar baiji ba , ta dad'e a tsaye kafin yace " waye a tsaye ne in bazai shigoba ya koma , Aysha ta shiga ciki sannan ta ajiye kwandon kayan abincin tashiga bud'ewa , bayan tagama bud'ewa tace " mezan zuba maka daga ciki ? duban Abincin yayi sannan yace ki zubamin kunun gyad'a sai ki zubamin farfesun kayan ciki , hakan tayi masa ta ajiye sannan ta juya zafa fita , Aysha ya kira sunan ta cak ta tsaya zonan , a hankali ta tako tazo gurin dayake ta tsaya batare da tace uffan ba , Hameed yace " meyafaru da Mama ta tashi taganki ? shuru Aysha tayi kamar bazatayi magana ba sai kuma tashiga fad'a masa duk yadda sukayi da Gogal , Hameed ya saki ajiyar zuciya sannan yace " ki godewa Allah da kika samu batayi dogon fushi dake ba , kuma Allah yasa kinyi tuban gaske bazaki k'ara komawa ruwa ba , Aysha sosai taji rashin dad'i akan kalmar sa na cewa wai Allah yasa tayi tuban gaske , Ameen tace masa ta juya tabar office d'in nasa da sauri......

Haka suka yini a asibiti wannan abincin da aka kawo daga gidan su Hameed shi sukaci har Habu ,.....

Hameed gida ya koma sai bayan Magriba yadawo asibitin , da kayan abinci yataho musu sosai Gogal take godiya dan irin kulawar da yake basu har tayi yawa , wannan karon tun da yashigo Aysha ta tsiri lazimi dan batason magana ta had'asu , tanajin sa shida Gogal sai hira suke tamkar sun dad'e da sanin juna , nan take masa godiya akan nauyin ta da ya d'auka a asibitin batare da an anshi ficikar suba , murmushi Hameed yayi sannan yace " Mama ai asibitina ne kuma kinga ke Mama tace taya d'a dan yayi hidima da Mahaifiyar sa ace kuma sai ta biya , Hawaye ne suka shiga zubowa a kuncin Gogal nan tashiga sama sa Albarka .......

*Bayan kwana biyu*

Tuni an sallami su sundawo gida , sosai Aysha take kulawa da Gogal tare da gujewa duk wani b'acin ranta , Anan Aysha ta yanke maidawa da Alhaji Na Lamma mukullin gidan sa da kuma motar sa , Gogal sosai tayi na'am da maganar Ayshar , ranar wata laraba da safe ta shirya ita da Habu suka hau motar tare da tafiya da mukullin gidan dan maidawa Alhaji Na Lamma , sai da suka fara zuwa gidan duk wasu kaya datasan natane a cikin gidan ta kwashe ta fito dasu , Bayan ta gama kwashewa gida ta dawo dasu ta ajiye sannan suka nufi gidan Alhaji

Na Lamma.....

Gidan sa ba b'oyayye bane shiyasa basu sha wuya ba suka gano , suna zuwa Megadi ya lek'o ya tambaye su su waye kuma wajen wa sukazo ? nan Aysha tace masa wajen Alhaji sukazo suna son ganin sa , nan Megadi yace musu " Alhaji bashi da lafiya bazai iya fitowa ba amman bari yayiwa yaron sa magana , nan yashiga cikin gida yayiwa Farouq magana akan suna da bak'i , Farouq yace masa ya shigo dasu kawai , koda Aysha suka shigo Farouq yana ganin ta ya mik'e dan mamakine ya kamasa , cikin zuciyar sa yake tambayar me Aysha tazo yi gidan su kuma yanzu ? Aysha ta gaida Hajiyar Farouq sannan tace mata " dan Allah ko zan iya ganin me gidan ? Hajiya tace " wacece ke baiwar Allah da kikeson ganin sa , Farouq yayi saurin cewa " zaki iya ganin sa Aysha muje in muna miki d'akin sa , Aysha tabi bayan Farouq itama Hajiyar mik'ewa tayi tabi bayan su....

Alhaji yana kwance gefen jikin sa baya motsi , sai dai fess jikin sa da alamar ana bashi kulawa sosai , Suna zuwa Ya kafe Aysha da idanuwa bakin sa kuma yayi nauyi dan baya iya magana sosai , take Aysha tasake jin tsoron duniya da dukkan abinda ke cikinta , tabbas me rai baigama ganin halittar sa ba mutuk'ar ba mutuwa yayi ba , nan tashiga neman yafiyar Alhajin akan barazanar da tayi masa san kawai ta mallaki gidan sa , ta kuma bashi mukullin gidan nasa tare da na motar Farouq , kuma ta sheda musu tuntuni ta goge komai dayake wayar ta na Abinda ta d'auka , Alhaji Na Lamma shima rok'on ta yayi tayafe masa duk da batajin wani abun dayake fad'a , Farouq dama tuni ya tuba ya canza hali yanzu duk yadaina yawace yawacen banza ya koma kula da dukiyar Mahaifin nasa , nan Shima Farouq yakuma rok'on yafiyar Aysha sannan ta fito tabar musu gidan , Alhaji Na Lamma ya yagawa Farouq ya maidawa Aysha komai ya bar mata halak malak , ......

Hameed yazo yayiwa Gogal sallama akan zai koma England sai nan da shekara zai dawo , Gogal tanuna rashin jin dad'i na tafiyar sa , dan zuwa yanzu sosai sun shak'u da Hameed kuma sosai yake bata kulawa , haka tayi masa fatan Alkairi tare da addu'ar kariya daga sharrin duk kan abin k'i , Hameed sai dube dube yake kozaiga Aysha amman bai ganta ba , gashi yakasa tambayar Gogal inda Ayshar taje , haka ya ajiyewa Gogal kud'i me yawa sannan ya mik'e yana mata sallama , har k'ofar soro ta rakosa tana masa fatan ya sauka lafiya , yana k'arasowa jikin motar sa ya fito da kayayyakin abinci da yasiya musu akaita shigar musu dashi , yana shiga cikin motar zai tashe ta ya hango Aysha da Habu sun sauka a Napep , har sukazo suka gitfa ta gaban sa bai tafi ba sai dayaga shigar su cikin gida ,.......

Koda Aysha tashiga gida da wannan kayan suka fara karo , daman tunda taga motar tasan Hameed ne yazo amman ko kallon wajen da motar take batayi ba , duk wannan abun tanayine dan ta nisan ta kanta da Hameed , tasan koda wasa ba aurar ta zaiyi ba tunda ta fad'a masa asalin wace ce ita....

*Bayan kwana biyu*

Ruma sunyi waya da Aysha ta sheda mata sun tashi , nan tazo gidan da suka dawo kuma anan Ruma take bawa Aysha labarin rabuwar ta da Khalid , sai sannan Aysha itama tashiga bawa Ruma labarin waye Khalid da kuma irin abinda yayi mata , sai dai ko kad'an bata gaya mata itace ta turo mata komai da Khalid yakeyi ba , nan suka jimantawa juna sannan suka shiga hirar su , Ruma tacewa Aysha " sister yakamata ki shiga Makaranta dan zaman haka bazai yuwuba ,.. Aysha tayi na'am da shawarar Ruma tasamu Gogal sukayi magana , da k'yar Gogal ta amince mata da taimakon Ruma da Mahaifin ta Aysha tafara karatu a B.U.K ......

*Bayan wata shida*

Rayuwar Aysha sosai ta canza ta koma kamar da , duk wani abu da zai tuno mata da rayuwar datayi ada ta banza sai ta kaudashi , kullum suna tare da Ruma har kwana Ruma na zuwa gidan su Aysha tayi , Mahaifin Ruma ya d'auki Aysha tamkar shi ya haifeta sosai yake taimaka musu , Gogal lafiya tasamu tuni ta koma sana'ar ta ta saida k'osai dan tace bazata zauna haka ba koya sana'a tana da dad'i , ...

Farouq yadawo wa da Aysha mukullin gida da motar kamar yadda Alhaji Na Lamma ya umarceshi , sai dai fir Gogal tace bazasu ansa ba ta gode , haka ya koma jiki a sab'ule duk babu dad'i ,.....

Khalid kuwa tun wani lokaci da yazo wajen Aysha yayi mata rashin mutunci , sannan yace duk kud'in da yakashe mata sai ta biyashi ko kuma yayi mata abinda bazata manta dashi ba , lokacin suka kaishi k'ara akayi musu tsakani , Aysha ta tattara duk kud'in da tasamu a yawon ta takai gidan marayu sadaka.......

*BAYAN SHEKARA DAYA*

Aysha da Ruma suna tafe sai hirar su suke abinsu , dayake su Mummyn Ruma suntafi Hajji shiyasa Ruma tadawo gidan su Aysha da zama , ganin wata mota sukayi tana binsu cikin lungun da zasu shiga gida , Ruma tace " Sister wai bakya ganin wata motar ana bin mu ne ? Aysha tace nagani koma waye shi yajiyo , suna zuwa k'ofar gida suka shige abinsu batare da sun wai waya ba , Motar tayi parking a k'ofar gidan sannan ma mallakin ta ya fito daga ciki , ba kowa bane face Jabir Abokin fad'an Aysha , tsayawa yayi jikin motar yana neman yaron da zai aika ayi masa kiran Aysha , aikuwa wani yaro yazo zai wuce Jabir ya kirasa tare da turasa cikin gidan yace yakira masa Aysha , koda yaron ya shiga ya sheda mata Aysha cewa tayi ace bata nan , har yaron zai fita Gogal tace " kai yaro kace gatanan zuwa kaji , Aysha ta dubi Gogal itafa a yanzu babu shirin soyayya a tare da ita bare kuma aure , amman gudun b'acin ran Gogal yasa batace komai ba ta maida Hijab d'in ta ta fita.....

wa zata gani Jabir tauraruwa me wutsiya ganin sa ba Alkairi ba , d'aure fuska tayi ta samu waje ta tsaya tsam , k'arasowa yayi wajen ta yana murmushi sannan yace " Hajiya Aysha ko kuma nace Malama Aysha , Aysha tayi masa wani kallo sannan tace " duk wanda yayi maka kirani dashi , Jabir yace " me yai zafi haka nifa yanzu bak'one a gareki me niyar zama miji a gunki , wani kallo Aysha tayi masa sannan tace " Kanemi wacce zata zama matarka tun lokaci bai k'ure maka ba , wai menayi maka ne kake shiga rayuwata ? Jabir yace " sonake ki shiryu ki

nutsu ki canza ki zama ba mai 2 face ba , tun sanda nafara ganinki nakamu da sonki saboda kamalar ki , amman dana bibiyeki sai nasamu ashe ba haka zuciyar ki take ba , tunda ga nan na kud'iri niyar gyaraki koda zanyi bak'in jini a gurin ki , to Alhmd kin gyaru yadda nakeso kuma nayi bak'in jini a wajen ki amman bandamu ba tunda kin shiryu , Aysha inasonki ina kuma son aurar ki inhar zaki amince , karki damu da komai kikai a baya ni naji kuma na amince zanyi rayuwa dake , a yanzu ina da sana'ar yi dan haka zan iya rik'e ki batare da kin buk'aci komai daga wajen wani ba , Shuru Aysha tayi tana nazarin magan ganun Jabir , tabbas sai yanzu tagane Jabir yafita gaskiya tunda gashi ta shiryu kuma ta dalilin nasa , amman a gaskiya ita a yanzu bazata iya aure ba dan bata shirya hakan ba , ta d'ago ta sheda masa bazata iya aure yanzu ba kawai taga wata had'add'iyar motar ta tsaya a kusa dasu , andad'e ba'a bud'e motar ba hankalin ta gaba d'aya yatafi wajen motar , Jabir ya kalleta yaga tana kallon wajen da motar tayi parking , wani kishi yaji ya kamasa a d'an tsawa ce yace mata " me kike kallo Aysha magana fa muke , jiyowa tayi sannan tace " naji duk batunka sai dai kayi hak'uri ni a yanzu ban shirya yin aure ba.......

Tana gama ce masa haka ta shige cikin gida dan bata da wani abun da zata kuma gaya masa , Jabir wata iska ya furzar a bakin sa yana me fad'in " bazai yuwuba Aysha wallahi sai kin aureni dan nine nafi dacewa dake , yana gama fad'in haka ya juya yashige motar sa yabar k'ofar gidan ......

Aysha na shiga cikin gida tasamu Ruma tana cin d'an wake ita da Gogal suna hira , band'aki tashiga dan yin wanka dan zafi ya dame ta sosai.....

Hameed yana ganin tafiyar Jabir ya fito daga motar ransa a d'an b'ace , wato Aysha bazata daina kula mazan nan yan iska ba , amman tunda yadawo kuma dama da maganar auren ta yazo komai yazo k'arshe , cikin gidan yashiga d'auke da sallama a bakinsa , Gogal tanajin muryar sa tace " wanake ji kamar Yarona Hameed ? Hameed yana murmushi yace " nine Gogal lale marhabun da yarona saukar yaushe ? Hameed yace " jiya da daddare Mama , tuni ta shimfid'a masa tabarma saboda ana zafi shiyasa batace ya shiga d'aki ba , Ruma ta gaidashi cike da girmamawa sannan ta tashi ta basu waje....
... Aysha kuwa tana toilet tana jinsu samun kanta tayi dajin wani farin ciki , Hameed yadawo kenan lallai Gogal dole tayi murna da dawowar Hameed , .....

Nan suka gaisa ta tambaye sa ya iyayen nasa tare da tambayar sa ya aiki , Hameed duk ya sheda mata komai lafiya itama yashiga tambayar ta ya ya barsu , lafiya lau Muke Yarona ai kullum cikin zuba ido nake tunda shrkara ta cika , Ruwa Ruma ta kawo masa tare da zubo masa d'an wake , Dai dai lokacin Aysha ta fito daga toilet tagama wanka , Hameed sai da k'irjin sa ya buga ganin surar Aysha a yanayi da bai tab'a gani ba , duk da tasa hijab amman iya gwuiwa ne ana hango k'asan k'afarta , da sauri ya saita kansa dan gudun Gogal ta fahimceshi , nan Aysha ta shige d'akin ta da sauri , Hameed ruwa ya d'auka yasha sannan ya faracin d'an waken , dama shi ma'abocin son abincin gargajiya .....

Bayan ya kammala suka ci gaba da hira da Gogal , nan su Aysha suka fito dan zasuje gidan su ruma d'ebo mata wasu kayan , Aysha ta gaisar da shi ya amsa ba yabo ba fallasa.

Suka gayawa Gogal tace musu sai sundawo sai dai kar su zauna , .....

Suna fita Hameed yacewa Gogal " Mama nazo muyi magana dake dafatan zaki amince , Gogal tace inajinka Yarona fad'i duk abinda kakeson fad'a , gyara zama yayi sannan yace " Mama inason Auran Aysha da fatan zan samu , Gogal tayi shuru na wasu lokuta sannan ta nisa tace " a gaskiya Yarona Aysha bata dace dakai ba , Aysha takasance a baya batajin magana duk ta gama yawace yawacen ta , duk da a yanzu Aysha ta tuba tadaina komai amman bazan iya b'oye maka wannan halin nata ba , kaima yarona ne kuma na yaba da hankalin ka dan haka bazan so in rufeka da komai ba , Hameed yayi murmushi yace " nasan komai game da Aysha dan tafad'a min komai lokacin da kika kwanta a asibiti , inhar Aysha ta shiryu wallahi a shirye nake na aure ta kuma banaso bikin ya wuce sati biyu , Gogal tace " sati biyu Yarona ai yayi sauri kabari ku fahimci juna Mana , Hameed yace " ba dad'ewa zanyi ba Mama daman maganar ce tadawo dani kuma nagama magana da iyayena , sun amince min akan auren dan haka zasu zo nema min auren ta cikin satin nan , Gogal shuru tayi na wasu lokutan sannan tace " Babu komai za muyi magana duk yadda muka yanke zangaya maka , Hameed yace " karki damu Mama kece me aurar da Aysha dan haka kece zaki yanke komai , murmushi tayi sannan tace " nasan da hakan Yarona amman komai yanason nutsuwa da kuma shawara , da wannan suka gama magana Hameed ya tashi ya fita , kayan tsarabar da yayi musu ya shigo musu da shi sannan yayi musu sallama ya tafi......

Sai Bayan sallar Magriba su Aysha suka dawo , Bayan sunci abinci sunyi sallah suka zube suna hira har Gogal d'in , nan aka turo kiran Ruma saurayin ta me suna Ahmad wanda shine zata aura , dan tun rabuwar ta da Khalid bata sake kula kowa ba , Ahmad d'in ma dan tayaba da hankalin sa kuma ta gwadashi ta hanyoyi da dama batasame sa da wani mugun halin ba , shiyasa yana zuwa basu d'auki wani lokaci ba aka samu su rana , ....

yarage daga Aysha sai Gogal suke hirar tasu , a cikin hirar da suke Gogal ta sako maganar Hameed akan zuwan da yayi , Gogal tace " Aysha yaron nan da gaske yana sonki kuma yace cikin satin nan zai turo iyayensa , Aysha tayi shuru batace komai ba , meyasa Hameed bazai tambaye ta ba zai ce zai turo iyayen sa ?
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🥴🥴

_NA_
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 31

Aysha ta kalli Leeemah tace " K'awata tashi mutafi kingama aikin ki , dama tuni Leeemah tasa kayan ta dan haka mik'ewa tayi kawai suka nufi hanyar fita , Muryar Khalid a fusace yace " Aysha inaso duk kud'ad'en da nakashe miki kidawomin da abuna , dan ashirye nake in k'waci kud'ina ko taya ya tunda bake na nemawa ba , cak Aysha ta tsaya tare da jiyowa tana duban Khalid , tabbas tasan me hali baya tab'a canzawa amman batayi tunanin Khalid zai sake magana ba dayaji ko wace ce ita , wani murmushi tayi me ciwo sannan tace " inaso kasani duk sanda ka shirya karb'ar kud'in ka ko tayaya d'in nima na shirya , tunda har hakan bazai gyara maka rayuwa ba sai ma wani sabon furuci da kake bina dashi , to tabbas kota yaya ka shirya nima a shirye nake sai najika , tana fad'in hakan tasa kai ta fice daga d'akin batare da ta kuma bi ta kansa ba , Leeemah na biye da ita har suka k'araso wajen motar ta suka shige tare da ficewa daga cikin Hotel d'in , ....

Tunda suka taho ba wanda yayi magana har sai da suka kusa zuwa hanyar da zata kaisu gidan su Aysha, Sai a lokacin Aysha ta dubi Leemah tace " inane unguwar ku inason inkai ki ? Leeemah tace " kawai ki saukeni anan na hau Napep ya k'arasar dani , nan Aysha ta bata dubu Ashirin sukayi sallama ta sauke ta ......

Aysha na k'arasowa cikin gida tafara Hon. Alamar azo a bud'e mata , ganin shiru Habu bai zoba yasa ta sauko da kanta ta nufo k'ofar gidan dan ta bud'e , sai dai tana zuwa taga kwad'o alamar gidan a rufe yake , wani irin fad'uwar gaba Aysha taji ta kamata Ina Gogal ta tafi haka alhalin bata da lafiya ? tsayawa tayi tana nazari can ta hango Jabir ya nufota yana wani murmushi , gaban tane ya fad'i dan yanzu ganin Jabir yazame mata annoba , aikuwa yana k'arasowa yace " Hajjaju Aysha 'Yar Hannu yana ganki a tsaye ? had'e fuska tayi sannan tace " to dan kaganni a tsaye wani abun ne ? wai me nayi maka haka kake shiga rayuwata ? Jabir yayi murmushi yace " babu abinda kikamin kawai inasonki ne kuma inaso inga kin shiryu , Aysha ta galla masa harara sannan tace " dana shiryu da kar na shiryu meye matsalar ka ? inaso kafita daga cikin rayuwa ta tunkafin nayi maka abinda bakayi tunani ba , wannan lokacin dariya sosai Jabir yasa har da tafawa kafin yace " to nikuma wanne abu zakiyi min zakiyimin yadda kikawa Khalid ne shima , sosai Aysha taji bugawar k'irji amman sai ta daure ta saita kanta tace " zanyi maka mutuk'ar kaima kashiga hurumina , Jabir yace " sud'in wanne Hurumin naki suka shiga ? kawai dan kin kasa hajarki sun siya shine zaki dunga binsu kina musu

barazana ?  runtse idon ta tayi dajin Abinda yace , katseta yayi da cewa " kece kikayi tallah kuma aka siya to dan me zaki dunga binsu kina anshe musu kayan da kika siyar ?  Aysha a zafafe tace masa " Ya isheni haka malam , inaso kafita daga cikin sha'anina tunda bansaka ka a ciki ba ,   Jabir ya tab'e baki sannan yace " ai dama bance kisakani ba ,  kuma inaso kitanadi wata k'aryar da zaki kuma yiwa Kakarki dan wannan lokacin kamar baki da mafita  , yana kaiwa nan ya juya yayi tafiyar sa .......

Da ido Aysha ta bi bayan Jabir tana mai maita kalmomin sa na k'arshe ,  me Jabir yake nufi ?  kodai yakuma zuwa ya had'ata da Gogal ne ?  indai hakane tabbas Jabir zai girbi hukuncin ta nan bada jimawa ba ,  komawa tayi  cikin motar ta zauna tana sak'e sak'en tare da tunanin inda su Gogal sukaje , a haka har aka kira sallar Magriba bataga wasu masu kama sa Gogal ko Habu ba , tuni gabanta ya shiga fad'uwa take ta tuna ai bata kira Habu taji ina suke ba  ,  nan tayi saurin d'aukar waya tare da kiran Habu  aikuwa bugu d'aya ya d'aga  , da sauri Aysha tace " wai ina kukaje ne Habu nadawo naga gidan a rufe da kwad'o ?  jin Muryar sa tayi a sanyaye yana cewa "  Muna tsohon gida , a zabure Aysha ta mai maita Tsohon gida kuma ?  Habu yace " Ea tun bayar fitarki ba dad'ewa Gogal ta fito tace mun inzo in raka ta Unguwa  , Makarantar da kike zuwa mukaje da ita nan tagana da Babban Malamin makaran tar taku , to nan san me yace mata ba tunda muka taho hanya take zubda hawaye har muka iso gida , muna zuwa tasani na nemo me napep ta d'ibi kayan sawar ta tare da cemin nima in d'ebo nawa zamu koma tsohon gida , na tambaye ta meyasa amman haryanzu bata gayamin ba har muka dawo gida ,   tuni Aysha tayi mutuwar tsaye ko motsi takasayi , tanajin Habu nata faman cewa Hello hello amman takasa janyo maganar ma tayi ,  kashe wayar tayi baki d'aya tanajin wata zufa na karyo mata , taya zata tunkari Gogal ? mezata ce mata intaje gurin ta ? kodai guduwa zatayi tabar garin baki d'aya ?  kuma inta gudu ina zataje  batasan ina zata nufa ba , sannan kuma indai tayi haka to tabbas Hak'k'in Kakar ta bazai tab'a barin ta tasamu kwanciyar Hankali ba , dole ta shirya tunkarar duk irin hukuncin da Gogal zata yanke mata ,  haka ta zauna cikin motar tana ta tunane tunane ,  kafin daga baya taja motar ta nufi hanyar tsohon gidan su........

Khalid tunda su Aysha suka fita ya zauna bakin gadon yana furzar da wata irin iska , tabbas Aysha tagama cutar sa meyasa zatabi ta wannan hanyar danyin ramuwa akan abinda ya mata ?  dan kawai yayi kwanta da ita shine zatace yayi mata fyad'e  ?  ai koma Fyad'en yayi mata itace ta janyo tunda ta bayyana surarta yaganta ,  yanzu gashi tayi masa buk'ulu kasuwar dayake zuwa an koresa , duk kud'ad'en daya samu tayi masa gaba dasu , Mahaifin sa babu irin gargad'in da bai masa ba akan ya rik'e amana a kasuwan cinsa , sannan ya kyauta ta mu'amalar sa da uban gidan sa ,  haka yasa k'afa ya ture dan son zuciyar sa  , gashi yanzu yayi biyu babu ai ba Ruma kuma ankorwsa daga kasuwa , yana zaune yaji ana buga k'ofar d'akin  , a hankali yabada umarnin ashigo d'aya daga cikin Ma'aikatan Hotel d'in ne yashigo , duban Khalid yayi yace " Oga lokaci ya cika zaka fita zamu gyara d'akin wasu zasu shigo , duban sa Khalid yayi sannan yace " kamarya in fita alhalin kud'in kwana d'aya na kama ,  Ma'aikacin ya dubi Khalid yace " gaskiya ba kwana bane a list d'in da muke dashi , yarinyar da takama kud'in Awa Uku ta bada  kuma lokaci yayi ,  Khalid runtse idanun sa yayi yana jin wata iriyar tsanar Aysha na shigar sa , tabbas dole ya d'au mataki akanta , haka ya mik'e ya fice daga cikin d'akin yana jin wani irin d'aci aransa .......

Tunda su Ruma suja fito daga cikin Hotel ita da iyayen ta take sharar hawaye , Mummyn tace ta janyota jikinta ta shiga rarrashin ta tare da bata baki , Ruma tace " Mummy ba ina kukan rabuwa da Khalid bane kawai inajin muguwar tsanar sane akan abinda yayi mana , ashe bashida hali me kyau yana ta zalintar Daddy duk bamu gane ba sai yanzu , Mummy tace " kansa ya zalinta ai tunda gashinan Allah ya toni asirin sa tun ba'aje ko inah ba , Daddy yace " ai wannan yaron ba k'aramin azzalumi bane , tunda yazo shagona nake ganin yanayin kamar ana min d'auke d'auke , amman ganin yadda yake nunamin shi na Allah ne kuma yana nunamin zai iya tsaremin komai na dukiya ta , sannan ya nunamin yana da k'wazo sosai wajen nema hakan yasa nasaki jiki nadaina kawo zargin sa araina , ashe lullub'eni yake da mugun k'ullin sa arai , lallai Allah ya dubemu da bamu aurar dake gashi ba da yanzu sai kin shiga zaifara nuna halin sa , haka suka ci gaba da zancen Khalid har suka k'araso gida......

Aysha tunda ta tunkari tsohon gidan su gaban ta yake fad'uwa , haka ta daure har ta k'araso k'ofar gidan ta nemi guri tayi parking , zama tayi cikin motar ta had'a kanta da sitiyarin d'in motar tana tunanin ta inda zata fara...........

_Inayiwa 'Daukacin Masoyana Albishir na Sabon Book d'ina Me Suna_ *NI KO ITA* _wannan littafi ya k'unshi abubuwa da dama,kudai kuyi saurin Mallakar naku akan farashi K'alilan_ ✍🏻

*Sai najiku Masoyana*🥰😍

_Ina mutuk'ar K'aunar ku Masoyana kamar yadda kuke sona❤️_ _saboda Son danake muku kamar nazo na janyoku muyi rayuwa tare😹😹💃💃💃❤️🥰_🤝🏻
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Assalamu Alaikum Masoyana   ina yi muku fatan Alkairi a duk inda kuke , ina Barar addu'arku daga bakunan ku masu Albarka , Allah yabiya mana Buk'atun mu na Alkairi_🙏🏻🙏🏻🤝🏻
*Taku Har Kullum*
_Zee MD_ 🥰❤️💞

_Page._     33

Banda Hawaye babu abinda idanun Aysha ke zubar wa , addu'ar ta d'aya shine Allah yasa kar Gogal ta mutu dan tasan itama rayuwar ta tazo k'arshe ,  suna k'arasowa Asibitin da yake mallakine ga Hameed tuni likitoci sukayo caa kansu ,  tuni aka nufi Emergency da ita akan gadon marasa lafiya ,...

Suna zuwa k'ofar shiga aka dakatar da Aysha ita da Habu aka shige da ita ,   Aysha hawaye sai zuba yake akan kuncin ta tana zagaye k'ofar d'akin , Habu ya dube ta yace " kiyi hak'uri Aysha kisamu waje ki zauna  insha Allah zata samu sauk'i , Aysha ta kalli Habu tace " bazan tab'a yafewa kaina ba mutuk'ar Gogal ta rasa ranta , a yau nayi dana sanin zuwa na duniya Allah na tuba Allah kayafemin ,  nan kuka yaci k'arfin ta tashiga rerasa tamkar k'aramar yarinya ,   Bayan kusan Minty 10 sai ga Hameed ya fito daga d'akin , da gudu Aysha ta nufoshi tana fad'in " Dr dan Allah kar kacemin tarasu , wallahi itace kad'ai farin cikina itace duk wani gatana a duniya ,  Hameed ya kalleta cike da tausayin ta tare da tsan tsar K'auna yace " Am sorry My Dear mun shawo kan Matsalar  yanzu haka tasamu bacci , kuma insha Allah inta farka to komai zaiyi dai dai , tasamu Bugawar Zuciya ne na wani lokacin amman munyi nasarar saita komai ,  Aysha ta lumshe ido hawayen da suka cika idanuwan ta suka gangaro a hankali ta furta " Alhamdulillah Allah kabata lafiya ,  Hameed da Habu suka amsa da Ameen....

Hameed ya dubi Habu yabashi wata takadda yace " kaje Reception kace a nuna maka Dr Kamal , kabashi takaddar nan kace ya duba sai yabaka abubuwan  da suke a rubuce , Habu yasa hannu biyu ya karb'a sannan ya nufi Reception ,....

Sauran likitocin da suka shiga da Gogal d'akine duk suka fito , nan suka cewa Hameed tasamu bacci nan da awa biyu zata iya farkawa ,  suna gama masa bayani suka bar gurin cike da bashi girma , Aysha tayi sauri zata shiga cikin d'akin  Hameed ya tsayar da ita ,  duk Abinda kikasan zai kuma d'aga mata hankali in ta farka to lallai a nisan tar mata dashi ,  cak Aysha ta tsaya sannan ta jiyo tana duban Hameed   shima ita yake kallo idanuwan su suka sark'e waje

d'aya , take kowannen su yaji wani Abu ya soki zuciyar sa , Aysha tayi saurin kau da kai sannan tace " yanzu kana nufin sai dai abar ta ita kad'ai kenan ? Hameed yace " indai kinsan ganin ki zaisa takuma samun matsala to tabbas ki nisanci gurin ta har zuwa wani d'an lokacin da komai zaiyi saiti , Aysha jiki a sanyaye ta dawo ta zauna kan wata kujera , Hameed ya tsaya yana kallon ta tare da nazarin yanayin ta cikin ransa yace " wato wannan matsalar da Kakar ta tashiga tasamu asali ne daga gare ta , lallai yana son jin meyasa Kakar ta tasamu wannan bugun zuciya haka , a hankali yacewa Aysha " in babu damuwa inaso ki biyoni office zamuyi magana me muhimman ci , batare da musu ba Aysha tacw masa to tare da mik'ewa tabi bayansa ......

Suna shiga office d'in wani k'amshine ke tashi tare da sanyin ac , wani hoton Hameed ne k'ato tamkar zaiyi magana kana shiga shine yake kallon ka , samun waje tayi ta zauna shima Hameed d'in ya zauna yana duban ta , sai da ya nisa sannan yace mata " idan babu takura inaso kibani labarin da kikace zaki bani yau , sannan inaso insan dalilin cutar kaka , dan bai kamata ace ta had'u da wannan cutar me saurin salwan ta ran mutum ba , tabbas inaso inji damuwar da ta haifar mata da hakan , Aysha ta yanke gayawa Hameed gaskiya , haka kawai takejin bazata iya b'oye masa komai ba , watak'ila ko ta sanadin sa tasamu ta shirya da Gogal dan yaga yana da halayen k'warai , ....

Gyaran Murya Aysha tayi tare da fara bawa Hameed labarin su tunda farko har izuwa lokacin da suka kawo Gogal Asibiti.... Duk irin rayuwar da Aysha tayi babu abinda bata gayawa Hameed ba , har cikin datayi ta zubar tare da gaya masa lokacin da suka had'u da ita shima wato lolacin da Farouq da Abokan sa suka mata fyade.......

Hameed tuni ya jik'e da gumi saboda rud'anin da yashiga , Ayshar sa wacce yake tsananin so yake mafarkin mallakar ta wacce yake wa kallon Ustaziya kamammiya me rik'o da addini ashe *'YAR HANNU* CE ? shuru yayi tare da yin k'asa da kai , tabbas Gogal tayi sakaci da yawa da har Ayshar tazama haka batare da ta lura ba , amman dole zaiyi mata uziri saboda yadda Ayshar takasan ce me nuna Fuska Biyu , Muryar Aysha ce tadawo dashi daga tunanin daya tafi tace " kaji Labarina kaji irin yadda nayi rayuwata wannan yana d'aya daga cikin Abinda yakesa nake nisan ta kaina da kai , kai Mutum ne kamili wanda yake da tsoron Allah dan sai dana bibiyeka nasan yadda halin ka yake , kana da taimako tare da tausayi da kuma kyautatawa Al'umma , nikuma rayuwata babu wani Abu wanda yake na Alkairi a cikin ta , ba kowa bace ni face *'Yar Hannu* mai bin Maza wacce tagama saida jikin ta , Hawayen dake idanun ta ta share sannan ta mik'e tana fad'in " ina fatan daga yau zaka nisan ceni nagode da taimakon da kayi mana , bata jira cewar saba tasa kai ta fice daga cikin office d'in .... Shima Hameed baiyi yunk'urin dakatar da itaba dan bashi da abin da zai ce mata a yanzu......

Ruma tunda suka dawo gida take kiran wayar Aysha , sai dai tana ta ring. Amman ba'adagawa , tunani ta shigayi ina Ayshar taje tabar wayar haka ? haka ta hak'ura da kira ta tura mata test akan yadda sukayi da Khalid da kuma irin amanar ta dayaci , ......

Aysha tana fitowa daga Office d'in Hameed ta samu guri ta zauna dai dai d'akin da Gogal

take , duk bayan minty 5 tana lek'awa ta windo dan ganin ta , a haka Habu yazo yasa meta a wajen yashiga tambayar ta ina Dr ? nan ta nuna masa hanyar office d'in Hameed batare da tayi magana , Habu ya nufi office d'in rik'e da Magungunan da aka bashi , Bayan kusan minty 3 saiga Hameed da Habu sun nufo wajen Ayshar , Suna zuwa Hameed ya shiga cikin d'akin tare da cewa Habu kaima ka jira anan , bayan wasu minty na shima ya fito tare da cewa " zan turo wata nurse d'in sai ta kwana da ita , zaku iya tafiya gida saboda gudun damuwar ta kuma kunga dare yayi , Habu bai fahimci inda zancen Hameed ya nufa ba shiya sa yace " ai anan zamu kwana nida Aysha basai ka turo nurse ba , Hameed yace " kai zaka iya kwana amman ita zaya iya tafiya yana fad'in haka yayi gaba abinsa , Aysha wani abu taji ya soketa arai taya zaice ita ta tafi abinta ? meyake nufi da hakan da zai fad'i ? ai koda bazata je wajen Gogal ba to tqbbas bazata bar asibitin nan ba dole ta zauna dan kulawa da Gogal d'in ta , ....

Nan ta dubi Habu tace " Habu kazo ka komq gida , kaga ko rufe gidan ba muyi ba kar azo asamu matsala , kuma kaga jinyar mace ai sai mace kai inyaso ko gobe ne sai kadawo , Habu yace " to shikenan babu abinda kuke buk'ata ? Aysha tace " babu komai sai da safe kawai , Habu yayi mata sallama ya shige yatafi abinsa ,.......

Hameed yana komawa Office ya d'auki wayar sa ya kira Hajiyar sa akan bazai dawo gida ba , yana da mara sa lafiya anan asibitin sa kuma suna buk'atar kulawar sa , Hajiya tasan halin Hameed da son bawa marasa lafiya kulawa , shiyasa tayi masa addu'a tare da yi masa sai da safe ,......

Yana zaune cikin Office haryanzu zuciyar sa takasa fad'a masa matsayin da Aysha take , sosai yashiga tunani ga shi ko kad'an Son Aysha da K'aunar ta basu ragu a zuciyar saba , wani sabon son tane ma yake kuma ratsa duk wata gab'a ta jikin sa , a hankali ya runtse idanu yana tuno labarin nata , tabbas so masifa ne dan badan so ba a gaskiya da bazai iya k'ara saurarar Aysha ba , amman ina a yanzu ma ji yake tamkar ya tashi yaje yagan ta ko zai samu sauk'in zuciyar sa , a hankali yabi shawarar zuciyar sa me cewa yaje ya duba ta Allah yasa bata tafi gida ba , yana fitowa daga office yanufo hanyar d'akin da aka kwantar da Gogal , tunda ga nesa ya hango ta ta takure a jikin Bango , daga gani kasan sanyi takeji duba da yanayin garin ana zabga sanyi sosai , wani tausayin tane ya kama Hameed har ya k'araso wajen da take batare da ta sani ba , rigar dake saman tashi ya cire ya d'ora mata ajikinta ganin yadda take rawar sanyi...........

[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *K'arashen 'YAR HANNU*🤒🤒

Gogal tace " nidai na ruga na yaba da hankalin sa amman kisamu 'Yar uwarki kuyi magana , tana fad'in haka ta mik'e tabar wajen .......

*Bayan kwana biyu*

Kwata kwata Aysha ta daina sukuni , Ruma tayi tambayar duniya akan meke damun ta amman tayi shuru , sai Gogal ce take fad'awa Ruma abinda yasa Aysha tarage wal wala ,

Ruma murna tayi sosai tashiga tsokanar Aysha Amaryar Hameed , Aysha dai bata tankaba dan batason ayi mata zancen Hameed , suna cikin hirar sai ga Hameed d'in yayi sallama , nan Ruma ta amsa masa tare da yi masa sannu da zuwa , ya amsa cike da sakin fuska dan jin sa yake cikin farin ciki tun baiji amsar da zai samu ba......

Bayan sun gaisa da Gogal yasamu waje ya zauna suka shiga magana , nan Gogal ta sheda masa ya jira dawowar Mahaifin Ruma dan shine zai amshi kud'in auren Aysha , murna sosai Hameed yashiga tare da yiwa Gogal godiya , itama godiya ta masa dan shine masoyin gaskiya wanda ko wacce mace zata yi Alfahari da samun sa , duk da irin abubuwan da yaji na Aysha amman ya amince da auren ta tabbas shine ya can can ci ayi masa godiya .....

Hameed bai tab'a zuwa gurin Aysha zance ba sai dai kullum cikin yi musu hidima yake , ko waya basayi amman kusan kullum sai yazo gidan dan yaganta ,..

A b'angaren Hajiyar Hameed baisamu matsala da ita ba , dan tana son abinda d'an ta yakeso take tashiga hidimar had'awa 'Dan ta kayan lefe , duk da bata tab'a ganin yarinyar ba amman Hameed ya gaya mata yadda take , Unguwar su Aysha babu magul mata shiyasa bawanda yakai sukar auren ta......

Alhaji Ashir suna da wowa bayan ya huta Gogal tasame sa da maganar zai anshi sadakin Aysha , yayi farin ciki da jin hakan kuma ya amince dan dama Gogal ta sheda musu basu da kowa , Dan haka shine yazama Uba ga Aysha ,....

Iyayen Hameed sunje nemawa Hameed auren Aysha gidan Alhaji Ashir , sosai aka karramasu bayan nan suka bada kud'in aure aka tsaida wata d'aya za'a had'a dana Ruma .....

Hameed baiso aka saka wata d'aya ba duk da yayi farin ciki da yadda aka karb'esu hannu biyu suka gaya masa , nan aka fara shirye shirye ta kowanne b'angare.....
Mummyn Ruma tuni ta tura Amare gida Mrs MD dan ayi musu gyara tare da tsumasu da magun guna , Aysha kwata kwata bata murna da auran nan dan ita a ganin ta Hameed b son ta yake ba , kawai dai zai aure tane dan wata manufar tashi daban , ko sau d'aya bai tab'a zuwa gunta zance ba sannan ace a hakan zasu zauna zaman aure , ba yadda zatayi haka take zuwa gyaran jiki ita da Ruma , yadda Ahmad ke nan nan da Ruma abin na birgeta amman ita ko sau d'aya Hameed yaki bata kulawa , bata b'oye wa me gyaran jiki ba aka itafa fa ba cikakkiyar budurwa bace , nan aka shiga had'a ta da magun gunan matsi masu kyan gaske batare da Ruma ta gane ba ,.....

Yau saura sati d'aya bikin Aysha da Hameed Ruma da Ahmad , suna hanyar su ta dawowa daga gidan gyaran jiki sukayi karo da Farouq nan yake gaya mata rasuwar Alhajin sa da kuma auren da yayi , sosai Aysha taji mutuwar Alhaji Na Lamma tayi masa Addu'ar samun Rahamar ubangiji , tayiwa Farouq gaisuwa tare da yi masa fatan Al kairi akan auren sa ......

Suna zuwa gidan sukaga ankawo lefen su baki d'aya , Alhaji Ashir gidan Gogal yasa aka kawo kayan lefe dan shima jin ta yake tamkar Mahaifiya a gurin sa , Ruma ankawo mata akwatuna takwas ita kuma Aysha Akwatina 12 kaya iya kaya abin ba'a magana , Ruma tafara yiwa Aysha maganar yadda zasu tsara dinner da party amman Aysha tace bazatayi ko d'aya ba kawai walima zatayi ,....

A daren ranar Hameed yazo wajen Aysha da maganar tayo masa list d'in duk abinda take buk'ata , Aysha ta sheda masa bata buk'atar komai duk da haka ya d'auki dubu dari yabata sannan yatafi ,...

Ana gobe kamu sukaje akayi musu kunshi da gyaran kai , nan ne Aysha taga Jabir yake sheda mata bayan yazo wajen ta ya tafi yan zuwa gida ya tadda Mahaifin sa ya nema masa auren wata yarinyar Abokin sa , yanzu haka saura sati bikin sa kuma Baban sa yace mudun ya bijirewa maganar sa sai ya tsine masa , Aysha tace Allah yasanya Al kairi Ruma tace " itamq jibi d'aurin auren ta Allah yabata miji na kere sa'a , duk da Jabir yaji rashin dad'i amman yataya Aysha murna yasan ko ba komai aure shine rufin asirinta ......

Walima kawai sukayi basuyi wata bidi'a ba , Washe gari aka d'aura auren Aysha da Hameed Ruma da Ahmad , sai muce Allah yabasu zaman lafiya.....

Komai iri d'aya Alhaji Ashir yayi musu babu wani bambanci , Gogal ta had'a musu gyara sosai itama wacce komai itama kai d'aya tayi musu , dare nayi kowacce aka mik'ata gidan mijin ta tare da tarin nasihohi daga wajen iyayen su ......

Fad'in had'uwar gidan Aysha b'ata bakine dan gidane na alfarma , kuma Alhaji Ashir ya zuba musu dukiya sosai kowacce sai san barka , tunda aka kawo Aysha take kuka dan batasan wace irin rayuwa zatayi da Hameed ba , shigowar sa ce tasa tayi k'asa da murya dan karyaji sautin kukan nata , ledojin hannun sa ya ajiye tare da shiga toilet yayi wanka , bayan ya fito ya umarce ta itama akan ta je tayi wanka ta d'auro arwala dan suyi sallah nuna godiy ga mahaliccin su , Bayan tayi tafito sukayi sallah nan ya yi mata addu'oi tare da addu'ar Allah yabasu zaman lafiya , .....

Wannan Daren haka Hameed ya rayashi tare da nunawa Aysha zallar k'auna , kwata kwata sai ya susuce mata tamkar qani k'aramin yaro , ita kanta sai da ta ji ajikin ta dan tabbas ta yadda da gyara da kayi mata tamkar wata sabuwar budurwa , shi ya taimaka mata ta gyara jikin ta yana ayyana anya wannan Aysha *'Yar Hannu* ce kuwa ? dan ji yayi tamkar shine yafara bud'e ya aleda, haka yai tasa mata Albarka ya zage ya rungumi matar sa yana nuna mata zallar k'auna.......

Satin su biyu sukayi sallama da iyayen su da Abokan Arziki suka d'aga England.......

Acan Aysha taci gaba da karatun ta tana karanta irin aikin mijin ta wato Likita , tare suke fita kullum suna tare da juna tamkar su cinye junan su sabo da kulawa ....

*Bayan shekara biyu*

Tuni Aysha ta haifi d'iyar ta mace wacce suka saka mata sunan Gogal , wato Aysha kuma sunan uwara ta suke kiran ta Eesha , lokacin Aysha ta gama karatun ta suka shirya zuwa Nageria , kafin suzo tuni angyara musu gidan su suna zuwa suka sauka a nan , sai da suka huta sannan suka je gidan su Hameed , sosai Hajiyar Hameed tayi farin cikin da ganin su tare da jikar ta , anan suka wuni sai dare suka nufi gidan Gogal , sai dai Aysha tasha mamakin ganin yadda aka maida gidan Gogal har da saka masa gate , tana shiga taga irin had'uwar da yayi sosai tasamu Gogal zaune da wata yar matashiyar budurwa suna hira , suna ganin su Gogal tace " ai bayi fushi wato sai yanzu zaazomin ko , nan Aysha tasa dariya tana fad'in " ko kinyi fushi dani ai bakyayi da Esha ba , nan Gogal ta anshe ta tanajin k'aunar yarinyar har cikin ranta , ashe da rabon zataga 'yar gidan Aysha lallai duniya komai mai wucewa ne , Anan suka kwana sunsha hira sosai anan take gaya mata wannan gyaran gidan Hameed ne yaturo da kud'i akai musu , sannan ya kaita aikin hajji ita da su Mummyn Ruma da Alhaji , sosai Aysha tashiga mamaki dan ko sau d'aya Hameed bai nuna mata ba , lallai Hameed gwarzon namiji ne wanda takewa Allah godiya da samun sa ....

Wannan budurwa da tagani Gogal ta sheda mata ai Matar Habu ce daya auro daga garin su , shine tace su zauna tare da ita dan batason zaman kad'ai ci , sosai Aysha taji dad'i gashi ta yaba da hankalin Rabi'a matar Habun , washe gari Hameed yazo ya d'auke ta suka nufi gidan su Ruma , saida suka jima da Mummy suna hira sannan suka nufi gidan Ruma , murna sosai Ruma tayi da ganin 'yar uwar tata tare da Esha ita lokacin har tana shirin yaye Abul kairi , dayake ta ruga Aysha haihuwa , anan Ruma take bata labarin Khalid ya haikewa 'yar gidan yayan sa anka masa yanzu haka yana can virson sai ya shekara goma sannan zai fito , Aysha tace " Allah ya kyauta wato me hali baya canzawa Allah yasa mudace , dare nayi Hameed yazo ya kwashe su suka nufo gida .....

Aysha tana jikin Hameed a kwance tace " bani da bakin da zanyi maka godiya mijina akan Alkairan ka gareni , sai dai a koda yaushe ina maka addu'a akan Allah yabiyaka da mafificin Alkairi , rungumeta yayi sannan yace " Ameen My Baby Esha one inaso kibani had'in kai a yau musamowa Esha baby k'ani ko k'anwa , dariya tasa tana tura fuskar ta cikin jikinsa , anan nafito na barsu dan kar nasa musu ido ......

*Bayan shekara uku*

Tuni Aysha tazama cikakkiyar Dr. Itama tafara aiki a asibitin da Hameed keyin aiki acan k'asar England , lokacin yaran ta biyu ga Esha ga Daddy wanda yaci sunan Mahaifin Hameed , In sun samu hutu suna zuwa Nageria dan Gogal ma Aysha tuni ta d'auko ta ta dawo da ita wajen su , Arzik'i sai Abinda yai gaba , dan yanzu Aysha tazama Babbar Hajiya tare da Mijin ta Alhaji Dr Hameed , Rayuwa ta sauya musu sai dai suce Alhamdulillah ........ Hameed yazama na Aysha Aysha tazama ta Hameed , kullum inta tuna irin abubuwan da tayi sai taji tana tarin nadama tare da kuma yin istigifari dan neman tuban Allah , Allah muntuba Allah kayafemana 👏🏻👏🏻👏🏻👏🏻

*Tammat*

*Alhamdulillah Allah yakawomu K'arshen littafin 'Yar Hannu , Abinda nayi ba dai dai ba Allah ka yafemun , wanda nayi dai dai kuma Allah yasa mu amfana dashi ,*👏🏻👏🏻

_Nagode sosai Masoyana ta yadda kukai ta bibiyar littafina batare da gajiyawa ba , Allah yabar k'auna Ina muku fatan Alkairi_🙏🏻
*tabbas komai yayi farko akwai k'arshen sa*

*Taku a ko yaushe*
*'Yar Mutan Kanawa*🌹🤝🏻🥰🥰🥰
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *Cigaban 'Yar Hannu*🥴
22

Kiran Aysha zatayi dan taje gidan su ta bata shawara akan Khalid dan gaskiya tunanin sa yadame ta , gashi ta rasa  kan sa kwata kwata dan ko kiran sa tayi kwata kwata baya d'agawa , ganin datar ta tayi a bud'e sak'onni na shigowa  rufe datar tayi sannan ta shiga neman number Ayshar  kiran ta tayi har takusa katsewa sannan Aysha ta d'aga ,  lokacin  suna tare da Khalid a manne suna zabga love , ka rantse wasu shahararrun masoyana na gaskiya , amman ina ko wanne da burin dayake ransa ,  d'aga wayar tayi tana fad'in " K'awata ya akayi kwana biyu , Ruma tace " lafiya lau dan Allah kina gida ? Aysha tace " bana gida amman indai zuwa zakiyi kibari zuwa anjima sai mu had'u ,  Ruma tace to shikenan sai kindawo , Aysha ta katse wayar tana jin tausayin Ruma har cikin ranta , dan tasan tabbas tafi son Khalid akan son dayake mata , dan yadda ta karance sa kwata kwata ba dan Allah yakeson Ruma ba kawai saboda dukiyar Mahaifinta yake sonta , kuma da sannu zata rusa masa duk wani shirin sa , zata yi k'ok'arin raba Zuciyar Ruma da soyayyar sa , sai tasa Ruma ta tsanesa tsana mafi muni ,  ta kallesa suka had'a idanu ya wani kashe mata ido , itama murmushi tayi masa a zuciyar ta tana fad'in " ka kusa yin kuka da idanunka , dan tuni tasamu labarin yadda yasamu aka d'aukesa kasuwa da k'yar , kuma babu laifi mahaifin Ruma yana masa sallama me tsoka shiyasa yafara shigowa gari ,  yanzu lokacin da zata fara rabashi da kud'in jikin sa yayi  , dan sotake sai ta rabashi da kud'in jikin sa sannan ta Rabashi da Ruma da kuma kasuwan cin sa , sai yaji irin ciwon da taji a zuciyar ta na rabata da Mutuncin ta dayayi.........
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🥴🥴

_NA_
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 23

Aysha ta dubi Khalid tace " kasan da wa mukayi waya ? Khalid ya girgiza kai yana fad'in " taya zan san da wa kikayi nasan dai mace ce , Murmushi Aysha tayi sannan tace " Mutuniyar ka wai zatazo yau in ina gida , Khalid ya tab'e baki sannan yace " nasan indai tazo to sai tayi zan cena , kinsan Allah Baby ni nafison inyi rayuwa da wa yayyiyar mace irin ki , inason inga budurwa ta tana bani kulawa kamar yadda kike bani , Ruma babu abinda ta iya sai k'auyan ci itafa ko romance bata bari muyi , kullum sai ta runga cewa in k'ara hak'uri in mukayi aure tazama tawa komai sai yadda nayi dashi , ...

Aysha tuni taji wani ciwo a zuciyar ta yataso , tabbas ko wacce mace me mutunci babban burin ta shine ta tsare mutuncin kanta , amman ita ta k'arfi da yaji aka b'ata mata mutuncin ta , ta sanadin haka yanzu gashi ta lalace ,hawaye ne suka cika mata idanun ta tayi saurin maidasu , dan bata so ko da wasa Khalid yasan damuwar ta , Khalid yaci gaba da magana " kin san wani Abu Baby ? Aysha ta girgiza kai alamun a'a , yace ko sau d'aya bantab'a son Ruma ba , saboda bata d'aya daga cikin Matan da nake da burin aura , kawai ina kulata ne dan kud'in Baban ta , kuma sannan ina son dukiyar kaf tazama tawa nan gaba bayan babu shi , Aysha ji tayi wata tsanar Khalid ta nunku a cikin ranta , tabbas Khalid azzalumine kuma sai takawo k'arshen zaluncin sa nan ba da jimawa ba , Murmushi tayi nasu na asalin 'Yan duniya ta dubesa tace " to meyasa ka yadda zaka aure ta bayan kuma bata d'aya daga cikin matan da kakeso ka aura ? Murmushi Khalid yayi sannan yace " Baby ai kinsan a k'ark'ashin Mahaifinta nake kinga da kunya 'yar sa ta nuna tana sona nak'i amincewa , da zarar komai yadawo hannu na zan iya rabuwa da Ruma ko kuma na auri wacce rai na keso , Aysha tace " gaskiya kai d'in ka iya buga game amman karkaje fa ayi maka Babban bugun da ya wuce naka , Dariya yasa yana fad'in " waye zai bugani alhalin ba wanda yasan meye a zuciya ta indai bake ba dana fad'a miki , kuma ni nasan ina da tabbacin bazaki fad'awa Ruma komai ba , Aysha tayi murmushi tace " haba Dear taya zan tona maka asiri , ai in nayi haka tamkar na tonawa kaina asiri ne nima , kadaina ma fad'in haka dan kasan ni taka ce kai nawa ba ta yadda za'ayi inga wani abu da zai zo ya kawo maka matsala batare da na kaudashi ba , haka Aysha ta karkace tashiga yiwa Khalid

dad'in baki sosai , nan yayi mata alk'wari komai takeso tafad'a zai siya mata , ...

Aysha tanajin haka ta kashe masa ido tace " account d'inka da zurgi kenan My Dear ? Khalid cike da shauk'in so yace "2 milloine acikin account d'ina yanzu , sai kinsan dayake ban dad'e dafara zuwa kasuwar ba , kuma ahakan ma ina had'awa da cuwa cuwa batare da me wajen ya lura ba , nan Aysha taji sirrin Kud'in da Khalid yake dashi , Murmushi tayi cikin ranta tace " yanzu zaka fara rabuwa da 1 Million kafin nan da kwana biyu ka rabu da sauran ma , cike da kissa Aysha tace " ni yanzu abinda nakeso kawai shine muje kasiyamin zobunan gold da sark'a dan ina son du sosai , Khalid ganin irin yadda Aysha ta kwanto jikin ta ajikin sa ga Na shanun ta rabin su duk sun fito yasa shi rud'ewa tare da cewa " muje Baby angama ,......

Jabir tunda suka rabu da Aysha yake ta dakon kiran ta amman shuru , gashi ya gwada layin ta amman baya tafiya kwata kwata , damuwa ya shiga sosai tare da fad'in " wato wayo Aysha tayimin batare da nagane ba , meyasa na yadda nabar ta ta tafi batate da nabi bayan ta ba ? tabbas indai yakuma ido biyu da Aysha bazai barta takuma raina masa hankali ba , kuma ai yagane number motar ta dakuma kalar motar tabbas zai ci gaba da neman ta tamkar yadda yayi kwanaki , .......

Yau saura kwana biyu Hameed yabar k'asar Nageria , hankalinsa sosai yatashi ganin har yakusa tafiya bai samu Aysha ba , yaje sau biyu unguwar su Aysha yana ganin ko Allah zai sa yayi sa'a sundawo , sai dai ko kad'an basu dawo ba kullum gidan arufe yake , yauma yana zaune a k'ofar gate d'in gidan su yana chat da wani abokin sa a can k'asar London , kwana biyu zaman cikin gidan baya masa dad'i saboda Hajiyar sa ta damesa da Maganar Abida , shikuma har ga Allah bason maganar yake ba , shifa indai ba Aysha ba haryanzu baiga macen data yi masa ba , dan acan ma London akwai mata wad'an da suke son sa sosai amman duk yak'i basu fuska........

Koda su Aysha sukaje wajen saida sark'ok'i , sai da Khalid ya siya mata na Million d'aya da dubu Hamsin , dan zab'a tayi sai dataji masu kud'i dayawa tace su takeso , Khalid sosai yaji fitar kud'in amman gudun kar ta gane ya dake tamkar wani Alhajin Birni , da suka taho hanya tasa shi ya biya da ita wani Shopping Mall tayi siyayyar dubu d'ari nan ma ya biya , Khalid suna fitowa ya nuna shima yanaso tabashi jikin ta dan haka su biya Hotel yakama musu waje , ko kad'an Aysha bata damuba dan dama jiran wannan ranar take , dan tasan daga wannan ranar bazai k'ara ganin Nonon ta bama bare jikin ta , haka sukaje Hotel Khalid ya kwashi gara sosai ,kusan sumewa yayi saboda sambatu dan iya jin dad'i yajishi a tare da Aysha , sai yake ganin ko nawa ya kashe mata bai fad'i ba ganin yadda ta rud'ashi shima , sosai yayi mamakin yadda Aysha ta k'ware wajen iya wasanni ,ko dayake bazai mamaki ba ganin ta wayayyiyar Yariya wacce tagaji da had'uwa, haka suka gama d'ebewar su sannan sukayi wanka suka nufo gida......

Aysha tun a farkon layin su tasa Khalid ya sauke ta , koda zata fita daga motar sai da Khalid yace " Babyna yaushe zamu kuma had'uwa ne ? dan gaskiya kinjiyar dani wani dad'in

da ban tab'a ji ba sai sau d'aya , Murmushi tayi sannan tace " sau d'aya Dear ashe katab'a yin sex ? Khalid yace " natab'a kwanciya da wata yarinya duk ba'ason ranta ba mukayi kuma shine farkon yina nima bana cikin nutsuwa amman haryanzu abin na raina , Aysha wani abune yataho mata ya tokare k'ahon zuciyar ta , kallon sa tayi cike da tsana tace " Saboda me ya tsaya maka arai kuma alhalin kace ba'ason ranta kayi ba ? jin yadda tayi maganar yasa ya dube ta , sai sannan Aysha tayi saurin ankarewa ta sassauta muryar ta tace " sorry Dear tausayin yarinyar naji ,amman meyasa kayi mata haka Alhalin bataso ? Murmushi yayi sannan yace " gaskiya sha'awarta tadameni kullum in muna tare to sai kinga abata a mik'e saboda yadda nake shaawar ta , ban daina jin hakan ba har sai randa na kusan ce ta , tana kuka tana magiya amman haka idona ya rufe na keta mata mutuncin ta , Aysha jitayi kamar a lokacin Khalid yake keta mata mutunci , hawaye ne ya cika idon ta wanda ta kasa iya maidasu , tabbas Khalid ya zalince ta dan shine sanadin komawar ta wannan rayuwar , yanzu waye zai aure ta a irin wannan rayuwar tata ? Meza tacewa Yaranta dazata haifa nan gaba ? taso ace Mijinta wanda zai aure ta shine zaifara sanin ta a duniya , amman Khalid ya rusa mata duk wani shirin ta ya lalata mata rayuwar ta , yasa taci gaba da sab'on mahaliccin ta , duk da tashiryu bayan zubar da cikin da tayi wanda yayi mata , Farouq shine ya maida ta ruwa shima yasa ta koma *'Yar Hannu* , tabbas Khalid azzalumine ya cuceta a rayuwar ta , jin tayi shuru yasa Khalid yin magana yace " meye naji kinyi shuru My Baby ? wani guntun Murmushi tayi sannan tace " wallahi danaji abunda kayiwa Yarinyar nan sai na tuno da wani Malamina a makaranta nima da yayimin fyad'e , Khalid yace " ayya sorry Baby kice mugun malami shine yafara yi mana hanya , nima kinsan Allah nine nafara yiwa yarinyar nan hanya , daga baya tasamu ciki nikuwa nayi mata korar kare , dan a ganina taya za'ace daga kwanciya sau d'aya wai ciki yashiga ai tazo da iskanci , sotake na aure ta ganin bata da wani asali gasu talakawa ba k'aruwa yasa na yi mata fata fata muka rabu , Aysha jitayi in bata yi saurin fita daga motar Khalid ba to tana gab da had'a masa jini da majina , shiyasa tayi saurin d'aukar kayan ta tace "muyi waya My dear , bata jira cewar saba ta fice da sauri abinta , Khalid ko ajikin sa bai kawo komai ba sai ma bin Mazaunan ta dayayi da kallo yana kuma wassafo dad'in daya sha ajikinta.......

Hameed yana zaune kamar ance masa ya kalli hanya ya hango Aysha ta nufo ta wajen dayake , da sauri ya mik'e yana murza idanun sa itace dai ba gizo take masa ba , kwata kwata Aysha bata kula da Hameed ba har tazo ta gifta ta gaban sa , haka yashiga binta batare da yayi magana ba , sai datazo k'ofar gidan su lokacin Habu na zaune yanajin radio ta wuce shi yana mata sannu da zuwa , da yauwa ta amsa ta shige ciki abinta shikuma Hameed yaja ya tsaya gana yiwa Habu sallama.........

*Ina mutukar Son Comment d'inku Masoyana*
_Yin Comment shine ke k'ara mana k'aimin yin Typing_✍🏻✍🏻

*Saina jiku*

*'Yar Mutan Kanawa*
_Ce_ 🌹😘🥰
[11/08, 3:43 pm] Maman Islam: *'YAR HANNU*
🤒🤒

_NA_
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Page._ 34

Aysha firgigit tayi ta mik'e dan batasan sanda tafara baccin ba , duban Hameed tayi sannan tayi k'asa da kanta dan wani kwarjini yake mata , shuru sukayi kowanne yana sak'e sak'e aransa , can Hameed ya nisa yace " kishiga Office d'ina sai ki kwanta a ciki in bacci kike ji , Aysha a hankali tace " ba bacci nakeji ba yanzu ma bansan sanda nafara gyangyad'i ba , Hameed ya dube ta sannan yace " amman kinsan dai nan akwai sauro kuma cizon sa zai iya haifar miki da zazzab'i , Aysha tace " ai zan iya shiga d'akin da Gogal take inyaso danaga ta farka sai na fito ko , Hameed yace " ai dama ba'a hanaki shiga ba kwata kwata kawai dai a yanzu tunda tana farkon ciwon dole in ta farko taganki abin zai dawo mata sabo , amman nan da zuwa safiya ma insha Allah zaki iya shiga ko yaushe kikeso , Aysha ta share hawayen da ya gangaro mata sannan tace " nagode Dr bari nashiga kafin ta farka sai na fito , bata jira cewar sa ba ta tura k'ofar d'akin tashige abinta........

Hameed komawa yayi office d'in sa ya had'a ruwan tea yana sha , tunowa yayi ba lallai in

Aysha taci komai ba , da sauri yatashi ya d'auki flast d'in shayi da biscuit ya nufi wajen nata , ..

Yana zuwa ya tura k'ofar d'auke da sallama sai dai ji yayi shuru ba a amsa masa ba , gadon da Gogal take ya kallah yaga idanun ta a bud'e alamun ta farka , tuni ya duba ko inah baiga Aysha ba , hakan ya sheda masa ta fita kenan dataga Gogal d'in ta farka , to ina ta shiga tunda bai ganta a waje ba kafin ya shigo ? gadon ya nufa d'auke da murmushi yana fad'in " sannu da jiki Mama dafatan yanzu babu abinda ke miki ciwo ko ? Gogal ta d'aga kai batare da tayi magana ba , Hameed yace " bari na had'a miki ruwan tea kisha sai inbaki magungunan ki kisha ko , da sauri ya had'awa Gogal ruwan shayi sannan ya tashe ta ya jingina jikin filo, hawowa yayi kan gadon da kofin tea yashiga bata a hankali yana lallab'a ta , aikuwa babu laifi sosai Gogal tasha ruwan shayin wanda yaji kayan k'amshi , ..

Duk abinda akeyi Aysha na hangen su ta cikin toilet d'in d'akin , tunda taga Gogal tafara motsi tayi saurin shigewa toilet d'in tare da addu'ar Allah yakawo Dr.Hameed d'in , Allah kuwa ya amshi addu'ar ta saigashi yazo har da Shayin sa a hannu , dama tunani take me za'abawa Gogal d'in taci gashi dare yayi , yadda Hameed ke bawa Gogal tea cike da nuna kulawa ba k'aramin birgeta yayi ba , take taji wata k'aunar sa na ratsa duk ilahirin jikinta tabbas Hameed shine irin mazan da mata ke muradin samu , da ace lokacin da take Sayyadar tace da babu abinda zai hana ta amincewa da auren Hameed , dayake toilet d'in a tsaftace yake shiyasa Aysha bata damu da zaman ta a ciki ba,....

Hameed ya kammala bawa Gogal magungunan ta , duban sa tayi kamar zatayi magana sai kuma ta fasa , Hameed yayi murmushi yace " ki kwantar da hankalin ki karkisa damuwa aranki yanzu ki kwanta ki huta zuwa safiya , Gogal itama murmushin ta maida masa batare da tace komai ba ta kwanta a hankali da taimakon Hameed.....

Hameed zama yayi a gefen Gogal yana ta danna wayar sa , ba'afi minty 10 ba Gogal ta koma bacci abinta , rufe mata jiki Hameed yayi tare da rage mata gudun fanka sannan ya mik'e zai fita daga d'akin , gani yayi ana k'ok'arin bud'e toilet dan haka ya tsaya dan ganin waye , Aysha ce ta fito tana sunkuyar da kanta k'asa , Hameed cikin ransa yace " dama tana cikin toilet duk wannan dadewar ? A fili kuma ya kalleta yace " Dama kina cikin toilet ? Aysha ta d'aga masa kai batare da tayi magana ba , d'an tab'e baki yayi sannan yace mata "ga tea can a flast ki tsiyaya kisha sannan ya mik'a mata biskit yace "ki had'a da wannan dan nasan ba lallai inkinci wani abun ba , yana gama bata tasa sannu biyu ta ansa tare da yi masa godiya ya shige ya fice daga cikin d'akin.......

Washe gari tun asuba Aysha ta farka dama ba wani bacci tayi me tsayi ba , shiga toilet tayi ta d'auro arwala sannan ta fito ta shimfid'a d'an kwalin ta ta tada sallah , bayan ta idar ta zauna tana lazimi da yatsun hannun ta , abinda Aysha bata lura ba shine tun fitowar ta daga toilet Gogal ta farka ta zuba mata idanuwa , wani kallo Gogal takewa Aysha wanda yake nuni da tanajin harda sakacin ta a lalacewar da yarinyar tayi , kuma a yanzu tadaina ganin laifin Ayshar dan duk acikin abinda yafaru da ita ta had'u da yaudarar 'Yaya maza ne , Abinda yafi d'aga mata hankali shine jin wai har ciki Aysha tayi kuma taje ta zubar batare da ita ta fahimci

hakan ba , tabbas tayi sakaci sosai kuma nadama tashige ta na yadda tayi sakaci da rayuwar Marainiyar Allah , hawayene suka shiga zubowa ta idanuwan Gogal tanajin tausayin kansu , yanzu wane namijin arziki ne zaiso Ayshar har ya aure ta ? tabbas wannan abu zaiyi wuya tunda ta riga tazama uwar mata , Aysha d'aga hannu tayi tana addu'a akan Allah ya bawa Gogal lafiya tare da neman gafarar ubangiji akan laifikan ta data aikata , hawaye na zuba tana fad'in " Astagafurullah Allah natuba kayafemin bazan sake aikata zina ba , duk addu'ar da takeyi Gogal najin ta tana kuma amsawa da Ameen , sai da ta shafa addu'ar sai taji Muryar Gogal nacewa Sayyada zo ki kaini band'aki in kama ruwa nima nayi sallah , Aysha da sauri ta waiwayo dan batasan sanda Gogal d'in ta tashi ba , wani sanyi taji a ranta hakan na nufin Gogal ta rage fushi da ita kenan , da sauri ta nufi wajen gadon tana kamo ta tashigar da ita band'aki , bayan ta gama kama ruwa tayi arwala sannan Aysha tazo ta fito da ita daga cikin toilet d'in ,.....

Bayan ta idar da Sallah Aysha ta dube cike da jin wata iriyar kunyar ta tace " ina kwana ya sauk'in jiki ? Gogal ta amsa da lafiya lau jiki Alhmd babu inda kemin ciwo , shuru ce ta biyo baya kafin Gogal tayi gyaran murya tace " Aysha inaso kibani aron hankalin ki , tabbas kinyi wauta da tun farkon da Khalid ya kusan ceki baki gayamin ba , da tun a lokacin zan d'auki mataki akan hakan , amman saboda kina tsoron kar nashiga damuwa yasa kika cuci kanki har abin ya girmama , duk da nima nataka rawa a komawar ki haka ta b'angaren sakaci da rashin saka idanu akan ki , duk irin yadda kike kashe mana kud'i bantab'a kawo wa ba a makaran ta kike samu ba , tabbas nima nayi kuskure babba kuma ina neman yafiyarki a akan hakan , Aysha da take kuka tunda Gogal tafara magana da sauri tace " baki da laifin komai Gogal , nice na zalinceki da halayena masu kyau taya zaki yadda zan aikata wani halin makamancin wannan , ban daina shigar mutunci ba ban kuma daina janyo aya ba duk lokacin damu ke tare dake , nice na yaudareki da fuska biyu wacce na zama saboda dalilin d'aukar fansa , tunda ga lokacin da Khalid ya yaudareni kuma yazo ya gujeni tare da gayamin maganganu mara sa dad'i nafara shirin d'aukar fansa araina , kwata kwata banyi basirar cewa cutar da kaina zanyi garin d'aukar fansar ba , idanuwa na sun rufe wutar d'aukar fansa na ruruwa a cikin zuciyata , na d'auki fansa Kamar yadda na k'udurta amman ina meyin tarin nadama da abinda na aikata wa rayuwata , wallahi natuba Gogal bazan k'ara aikata zina ba har nakoma ga mahaliccina , jikin Gogal ta kwanto tana kuka me tsuma zuciya tare da tarin yin nadama game da son zuciyar ta data bi..........

_Ina farin cikin sanar da Mata 'Yan k'walisa da Amare masu shirin shiga daga ciki , ga dama ta samu maza ku garzayo dan gyara jiki tare da mallakar tsumi gangariya ,_

*Akwai maganin gyaran nono ga macen da take shirin yaye yaron ta , ga turarukan gyaran jiki dana turara d'aki da na wanka tare da Humrah me ratsa zuciyar megida , akwai kulacca da man shafawa me kamshi ,*

_Uwargida Amarya maza ku garzayo dan mallakar naku ,   gyara shine mace Mata kutashi ku gyara dan kwato mazajenmu daga wajen matan banza 🤝🏻🥰_

*Dan samun kayanmu ku tuntubi wannan number 07046107812*
Sai najiku🤝🏻🥰